"Dubu dari da hamsin?! Dan na gasa ne, sai service da akayi dubu sha biyar, da kudin kawowa dubu biyar, kudin me aiki dube biyar.

"Waye ya baki kudin?!" Take cikina ya hautsina bakina na rawa na kasa bashi amsa yayi murmushi yace.
"Allah! Ko?"
Na gyad'a kai na, "idan ya karb'a me zaki ce"
"Alhamdulillah nagode mishi da ni'imar da yayi min"

"Toh ki leka waje! Bayan haka kar naji kinyi wani magana Allah yana tare damu"

Ban iya fita ba, Maryam da Innarmu suka leka, da kuka Maryam ta dawo, cikin gida.

An cika a kofar gidan sai surutu akeyi, ni kam bance kome ba, na girgiza. Dan sai da nayi zazzaɓi.

Taya zan kuma zuwa na ciro kudin bayan nasan duk inda yake yana ganin alert. Kuma comfirm ina amfani da kuɗin.

Amma babu karya na kwana ina kuka, domin sai da Meemah ta zauna muka yi kukan tare sannan muka kwanta.

Kirana Baba yayi sannan yace.
"Kudin sun kare ko?!"
Girgiza kai nayi alamun akwai, amma bazasu wuce na rufwa kai asiri ba.
"Toh indai akwai ki kuma buɗe shagon koda kuwa kayan masarufi ne!"

Jinjina kai nayi, sannan nace.
"Shikenan!"
Kwana goma tsakani, muka gyara shagon, sannan muka tafi har bauchi muka kuma yin sayayyar kayan masarufi, duk abinda za a nima hatta katin waya, da abin canjin waya muka sayo babban generator, da wata karamar deep freeze.

Wannan karon na cire kudi me mugun yawa, zuciyata har bugawa take, tare da Addu'ar Allah yasa daga wannan bazan kuma tab'a mishi dukiyar shi ba.
Dama masu azancin magana sunce practice make Perfect.
Doing something reapeadily is the Only way to be become good at it.

Dan haka nasaka a raina, Allah zai bamu nasara. Dan kuwa shi ba Azzalumin sarki bane.

Babban J5 aka kawo mu, inda muka samu masallacin kofar gidan mu, cike da maza baba yana tsaye.
Kallon mu yayi lokacin da ake sauke kayan, sannan ya kuma lalle su.
"Wallahi! Na rantse da Allah, idan aka kuma fasa min shago sai na bawa kowa Mamaki, anyi na farko. Kar a kuma."

Yadda yayi maganar ya basu tsoro dan sun san shi mutum ne mai mugun hakuri, kuma idan aka kure shi toh.

Barin su yayi yazo yana son taya mu sauke kayan Amma bai da lafiyan ko nace karfin hakan.

Kallon mu Baba Yawale yayi cikin jin haushi yana kumfar baki yace.
"Wallahi sai naga bayan shi tun."

"Kafin kaga bayan shi ka fara duba Alamarin yaron nan Kamalu ashe mu, a nan muna tacewa yana yar sana'a a birnin ashe yaron nan karatun nasara yake yi, gashi mun dauki Kuluwa mun bashi."

A zabure yayi kan Baba Iro, yana zare idanu.
"Toh wallahi yau zai sako min Y'ata."
Fuya- fuya, ya nufi gidan surukinsa, dan zubda kima yaje ya dauko yar shi, da tsohon ciki, muna gyara shagon bayan mun kai freezen ciki, muna saka kome a cikin mazaunin sa.
Suka zo zasu wuce, abinka da mai ciki ta hango biscuit aikuwa ta tsaya ta ciro kudinta tace.
"Addarmu, bani biskon nan?! Shi Kamalu yake sayo min idan zai zo daga birni "

Na diba a bakin leda na saka mata, nace.
"Tsohuwa da alamun nice zan amshi haihuwar."

"Kan jakar, buhun kaniyarki me tsaba"
Baba Yawale ya danna mata ashar, yazo ya fisge ledar ya wurga min, sannan ya shiga balbale ni da masifa.

"Wallahi ni sai naci! Dan ji nake kaman zan mutu, kuma kasan Kamalu ba mutuncine da shi ba, domin ya ce min yana irin karatun masu kaki ne, wallahi idan ka bari muka mutu, toh kaf danginmu sai ya alburushe mu."

Yazo ta amshi ledar tace .
"Nagode sosai."

Hmmmm.
Su suka sani, mu kam damuwar mu ta ishe mu, bazamu ari damuwar kowa ba.

A tsorace muka shirya kayan mu, amma da dare yayi muka kwashe aka mai da cikin gida.
Wannan karon babu matsalar kome, amma sai dai babu ko kare da yake zuwa sanyan kome sakamakon ce musu da akayi ai Zina nake zuwa yi a birnin, da kudin muke wannan facakan, ranar da naji haka.

Yankan jiki nayi na suma, bawai dan naji haushin kalmar bane, a'a sai dan tension yayi min yawa at my age, bani raba dayan biyu jini na ya haura sama da 360,

A karon farko da nayi wani katob'ara nace.
"Me yasa ma ban mutu ba?!"
Buge min baƙi Innarmu tayi, tare da zuba min rankwashi tace.
"Mu da aka abin sabida mu, muce me?! Ki godewa Allah da ya jarabce ki ta wannan hanyar, sai ki gode mishi."

Nasiha tayi min sosai, sannan nace mata.
"Innarmu kiyita mana addu'o'in, ina bukatar addu'o'in ki, ba iya Ni ba hatta yan uwana."

Na fada cikin kuka da gajiyawar halin rayuwa.

---

Bature (POV)

Tsaye yake a cikin ofishin sa, ya zubawa window idanu, har yanzun dai yana nazarin makomar kwanakin da aka bashi, a gida akan Devanah! Allah ya gani bayi son Devanah. Amma karfi da yaji ta makalewa Rayuwar shi.

Kara wayar shi tayi ya kalla sannan ya kauda kai, sake jin kara yayi, sai ya share.

Jin kara na uku yasa shi dubawa.
Dubu dari biyu da hamsin sau biyu, aka cire.
"Miss Manga!"
Ya ambata cikin cool Voice ɗin shi, lumshe idanun shi yayi, yaga Balance din cikin account ɗin ko girgiza basu yi ba, dan yasan each Sunday ana turo mishi 1.6m , kudin service din da yayi a ranar, wai ma dan bai da mata ne, da yana dashi tabbas da yafi haka samun kuɗi.

"Ina take a Bauchi?!"
Wannan itace tambayar da bai da amsar ta.

Tattaro kayan shi yayi sannan ya saka kai zai fita, a bakin kofa suka hadu da Dr Aahil, mika mishi hannu yayi suka gaisa.

"Dr BYC! Kana biyu ina ka shiga ne?! Ko nazo bana samun ka?!" Murmushi yayi sannan yace.
"Ina dab da barin kasar ne! Shi yasa bani zama sosai kuma ina son na gama da daliban master din nan!"

Wucewar wata daliba yar sabon shekara ya sanya shi juyawa yana binta da kallo musamman yadda ta Cancare cikin riga da wando, ga earpie da key mota a hannunta.

"Dr A'A! Har yau baka cire ranka akan yan mata ba, bayan kana da mata a gida."

Cikin iya shege ya kwashe da dariya yace.
"Ka san Allah ina son na kuma haɗewa da wancan Yarinyar, amma bana son mu same matsala irinta Miss Manga."

Tab'e baki Dr Bature yayi sannan yace.
"Ai yayi kyau!" Daga haka ya mika mishi hannu, suka kara gaisawa ya wuce, abin shi.

---

Yana tsayawa da motar shi sai da zuciyar shi ta buga, nakine ya sanya shi haka ba, sai hango motar Devanah! Fitowa yayi a matuƙar jin haushi, ya shiga gidan ganin key din kofar shi a kasa an fasa, turus yayi sakamakon ganin kowa da kowa har da yan church din shi.

Mik'ewa suka yi, aka fara rabtab'o addu'o'in, yana tsakiyar su, sai addu'a suke mishi yana cewa.

"Amin?!

Suna gamawa Mommah ta mika mishi dan karamin a kwati me dauke da zobe, kallon su yayi sannan ya girgiza kai yace.

"As i told do you! Nifa bani sonki! Kiyi hakuri kije ki auri Joel! Na rantse bana jin kome akanki bana jin kaunarki!"

A gaban kowa ya gaya mata baya kaunar ta, bakinta na rawa take nuna akan ta, tare da kallon kowa na gurin hawaye na zuba mata da mugun gudu tace.

"Gaya min! Meye na rasa da baka sona? Meye na rasa kyau, ilimi, waye, ko nasaba, dukiya ko me?!"

Girgiza mata kai yayi cikin damuwa yace.

"Kinga irinta ko?! Baki rasa kome ba, amma ni zuciyata babu sonki ne?!"

"Amma ita Bahaushiyar fa?!"

"Kinga karki kawo mana shirme mana. Ni babu wata yar Hausawar da nake kulawa zargin kine kawai."

Kwace wayar shi tayi ta gama dube dube bata ga kome ba, sai shaidar ciran kuɗi, kuka ta fasa me tsuma rai da ruhi.

Riko hannun shi tayi cikin tashin hankali tace.

"Da sonka na girma! Dashi na tashi a raina, na rantse maka da Yesu bani da mafarki sama da na same ka, Idan baka da lafiya ne, am agree zan zauna da kai haka! But don't reject my love, na rantse zan zauna na jiraka har ranar da zaka fara sona!"

Ya zai fahimtar da Devanah! Ta gane so ba a mishi tilis, amma halin da take ciki ya karya masa zuciya.

Fadawa jikinshi tayi, yana jin kukanta, na cika mishi kunne. Yaki yake da zuciyar shi.

Mikawa Mommah hannu yayi, ta sanya mishi zobe ya riko hannun shi yace.

"Zan zauna dake! But ku zama sheda duk ranar da na sami wacce nake so zan aureta ne ya zama dolenki you be patience, da abinda zan yi idan na sami wacce nake so."

"All is fair in love nd War"

Ta faɗa a hankali.

Shi kuma ya bata amsa da cewa.

"Things that are done in love or war can often be excused."

D'ago kai tayi tana kallon shi, bayan ta amshi zobenta zata da mishi tace.
"Karka ga laifina! Loveless life is a living death. Dan haka dan na haukace akan son ka ko na mutu bani da kaico"

Murmushi yayi bayan ya rungume ta, yana me jin zafi da ciwo a ranshi yace.

"Without affection, life is difficult, karki zurfafa dayawa!"

"Indai bazaka wulakanta ni ba, zan zauna da kai har karshen rayuwa ta."

Abinda zuciyarshi yace mishi.
**Devana kina cikin love blind**, **shi yasa baki ganin bakina dan nace bani sonki**!

Nan aka rufa musu kai da addu'a bayan baikon su.

---
Husnah (POV)

Sam bana son fita ko ina koda shagon ne, duk da yanzun akan zo a sayi irin su klin may soap, sugar, da dai sauran su, amma ban tab'a ganin mugayen mutane irin dangin Babanmu ba, kome da gafara suke zuwa su dauka, kuma hakan bamu tsira ba.

.......
Second Challenging....
Loading 🌺

[7/2, 8:54 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BAHAUSHIYA□

*Hattara Yan Mata*

Second Challenging.

Babi-sha-daya

Ban san me ya faru ba, kawai sai ga Mubarak ya shigo da Baba rike dashi, fitowa muka yi dukkan mu. Innarmu tace.
"Lafiya Mubarak"
Ganin Abdullahi muka yi ya zari wani itace ya fita da gudu, babu dan kwali na bi bayan shi, wallahi yaron nan baya ji. Yana zuwa ya sami kafadar Baba Haruna ya zabga mishi b'arin Itacen nan.

Cak na tsaya ina kallon ikon Allah, haukacewa yayi baki daya yayi ta muka musu itace.
Kusan shekarun shi nawa, sha takwas! Amma dake yana da tsayi ya mike zaka rantse yafi mu shekaru.

Zuwa nayi na zabga mishi mari, cikin ciwon rai dan ban san me zan iya yi mishi after all,
Yana huci yace.
"kai Tsohon banza maza sake min kanwa! Saketa kafin na ci..."

Jijjiga shi nayi cikin gigita nace.
"What?!"
"Wannan tsohon banzan wai dan ya renawa mutane hankali, wai auren meemah yazo yi, wallahi idan bai saketa ba, Allah sai na kashe banz...."

Rufe mishi baki nayi. Ina kallon su, cikin nuna dagaske haka ne, dattijon yace.
"Bashi na Haruna yaci. Na kusan dubu talatin, shine ya bani auren diyar wan shi."

Akan 30k an wargaza future din kanwarmu.

Juyawa nayi na koma cikin gida, birkita kayana nayi na ciro dubu talatin cif na kawo ishi, nace.

"Bani? Sakinta!" Na mika mishi hannu, cikin duniyanci yace.
"Ko kina da inda zaki kaini tsohuwar kilaki?!"

"Abdul! Ji min da tsohon nan ba shi ba hatta wanda ya tsaya mishi ka karya min kafafuwan shi."

Allah kenan, ganin yadda Abdul ya kinkimi itace zai kai mishi, aikuwa yace.
"Toh mara kunya ko girman tsofa na baki gani ba, toh na saketa daya."

"Ina ukun zaka yi tsohon banza!"
A take dai sai da muka raba auren abinda babu kyau, Allah mun tuba. Baba Haruna kan ai shiga dashi cikin gida aka yi, tare da nima mishi maganin tsamin jiki.

Koda muka shiga cikin gidan, rufe Abdul Innarmu tayi da duka, tana yi tana kuka.

Ba shi daya ba, nima bata kyale ni ba.

Mun zata case din ya kare washi gari sai ga, yan sanda.

Ban san yadda zan fada muku halin da muke ciki ba, amma maganar gaskiya, muna cikin

bakin ciki mara iyaka, muna ganin tasku da jarabta, bamu rasa kome ba, sai kwanciyar hankali da nutsuwa.

An tafi da Abdul, wani abin bakin ciki, shine ba ajiye shi a Toro ko Magama gumau, ba sai aka kawo shi bauchi.

Sannan aka ki gaya mana inda yake, tsabar zalinci.
Koda muka zo bauchi mun fara bin kananun ofishin yan sanda. A ranar a cikin garin bauchi muka wuni.

Har dare babu labarin inda yake, sai da muka gama yawo. Dakyar muka sami labarin inda yake, an kai shi can Dass.

A daren muka dauki shatar mota har Dass, acan suka ce baya nan. An kai shi wani karamin kauyen dass, wato Zan.

Abinda bamu sani ba, tsohon da ya auri Maryam ne ya biya kudi aka kawo Abdul gurin, mun same shi an mishi mugun duka, ko daga kai ba ya iya yi.

Kuka rahama ce, dan haka basu bamu shi ba sai da muka yi Yaren hannu da aljuhu.

Aikuwa suka sake mana shi, a daren muka wuce dashi asibitin bauchi, aka bashi magani.

Muka kuma biyan kudin mota aka dawo damu gida, Muna isowa karfe biyar na asuba. Gida muka shiga dashi, Mubarak da Driven da ya kawo mu, suka wuce masallaci.

Anan ma sai da Su Baba Yawale suka musu wani diban albarkan.
Haka Driven ya tafi yana mamakin wasu dangin al'ajabi.

Wato abinda na fahimta a rayuwar Bahaushe, shine idan yana bariki. Shi na kowa ne, kuma idan da zasu haɗu da dan garin su, toh tabbas sun zama yan uwa, wannan bawai dan labarina nake fada ba, sai dai nasan cewa akwai yan arewa da suke kudancin Najeriya, sun san da haka.

Amma a cikin garin shi toh fa, idan bai kai zuciya nisa ba. Bakin ciki ya ishe shi. Domin zaman mu a garin Kaduna, bamu san tashin hankali ba, haka ma a toro bamu san me ake kira hayaniya ba.

Amma dawowar mu, mahaifar mu, yau ta kare mana. Domin ido da ido ake mana hassada, ga gaskiya jahilci da kauyanci ya rufewa mutane ido.

Duk wata hanyar da aka san zamu karu toshe shi ake.

Idan nace da Ciwo a rayuwata ban yi karya ba, dan na zata a Novel ko a film ake labarin destiny, sai yanzun na fahimci asalin destiny. Ina da magana a bakina, amma bani da wanda zan juyewa, sai na zabi nayi ta kallon kowa da ita.

A yau ina raye ne, dan wata kaddarar, amma nasan gobe bakin ciki ya ishe ni riga da wando.

Domin dan saurayin da yan mata ke yi, bani da shi. Asalima Manga ne ya hanani sukuni, tare da cewa idan ina son a cigaba da sayan kayan mu, toh na amince mishi mu raya wani dare, daya har gonar Baba zai dawo mana dashi.

Kallon shi nayi tare da murmushi nace.
"Toh Malam Manga, sai dai har ka mutu Hussy bazata tab'a baka abinda kake hari ba."

Dariya yayi sannan ya taso zai yo kaina, na daga mishi hannu cikin b'acin rai nace.
"Wallahi ka Kuskura ka tabani zan maka.."
Takawa nayi har gaban shi, ina kallon cikin idanun shi nace..
"Wallahi zan maka kaciya!"
Ganin yadda fararen idanuna suka dira a cikin nashi ne ya sanya shi firgita ya juya da sauri ya fita.

.......
Ina ganin mun tsallake wannan matakin. Sai ga wani tashin hankali wai ana zargin Abdul da satar akuyar Baba Yawale.

Dariya muka yi, Abdul yayi bakin ciki sosai, dan har zolayar shi muke. Tsaki yake kawai yana cira.

Toh ya zamu yi, tunda muna cikin line of destiny, dole mu cigaba da tsallakawa, har Allah ya bamu ikon cinyewan.

---
Aahil (POV)
Kallon matar sa yayi wacce take ta sharan barci, ya zuba mata ido. Bawai ya rasa kome bane, domin kuwa yazo mishi yadda yake so, sai dai duk matan da yake mu'amala bai ji mace kamar Hussy ba.

Ajiyar zuciya yayi, da ya tuna lokacin da yake, murjeta bata ko tari. Sannan duk yadda yayi da ita bata ce mishi ta gaji, sai dai idan sun gama ya nemi kari tace tana da Class.

Duk yawon bin matan shi bai tab'a haduwa da irinta ba, kuma baya jin zai samu irinta, idan ya duba matar shi tafi hussy kyau amma. Tsarin halittar ba daya bane.

A ina zai samu hussy dako lallabata zai yi ya cigaba da moreta idan yaso sai ya san yadda zai saka a dawo da ita schl.

Tashi yayi ya shiga ban daki, kwara ruwa yayi sannan ya fito.

Kwanciya yayi yana nazarin ta yadda zai sameta.

"Teemah"

Itace yake da yakinin zai samu number ta a gurinta.

.... Washi gari ko karyawa bai yi ba, ya shirya dan matar shi ba aiki take ba, a bakin kofar fita ya hadu da Yarinyar da take musu aiki, kallonta yayi sannan ya bata hanya ta wuce, ba kome bane matsalar shi yaga tudun mazaunin ta.

Aikuwa tana shiga yabita da ido, bai ga wani abin burgewa ba. Shifa burin shi ya hadu da me irin halittar hussy!

(Amma kana ruwa)

---

"Allah Dr idan akayi baiko zamu iya gwada kanmu, a gani ko muna da lafiya, dan haka nazo maka hutu tunda anyi rabin aure, sauran zamu karasa a gidanmu."

Inji Devanah,

Kamar ya fashe da kuka, haka ya kalleta, sannan yace..

"Yanzun ke ko kunyar fadar haka baki ji ba. Ai ni bana fatan na sumbaci matar da zan aura, sabida kar Shaidan makiyin Baban mu, Adam yayi sanadin da zanyi laifi wa Ubangiji me ceto."

"Amma dai naga wannan zamanin na jin dadin rayuwa ne! Don Allah ka daina mai da kanka, mara wayewa."

"Lal.."

Jin sakon a wayar shi ya sashi dubawa, dan a yanzun baya jin kome a ranshi na damuwa matuƙar zai duba wayar shi yaga an cire kudi, sai yaji ya kara jin tausayin yarinyar, domin yasan banda dole bazata tab'a karban kudin ba, kuma shima ko a yanzun yayi aikin lada saboda Ubangiji zai bashi wani shatin babban fili a cikin aljanna.

Murmushi yayi sannan ya zubawa wayar ido.

Fauce wayar tayi tana kallon shi, tace.

"Yaushe tafiyar ka?!"

Tsaki yayi sannan yace.

"Wata sati, amma ina son zuwa bauchi, akwai taron da zanje nayi na addini."

"Ok zan raka ka!"

Ware idanu yayi akanta yace .

"Baki da hankali, me zaki yi a can, kawai ki koma gida idan na gama zan zo kafin na wuce."

.     Gyad'a kai tayi tare da tura mishi baki.

Ya kalli wayar yafi sau goma, badan kome ba sai dan tausayin Husnah, ko wani hali suke ciki?! Ya dangin Baban su suka karb'e su?! Banda ya hango ilmi ibada a cikin ƙwayar idanunta ba, ba makawa da sai ya shiga garin ya mai dasu kiristoci, tare da buɗe musu makarantar primary da Secondry, tare da primary health care.

Toh ba zai iya ba, domin fahimtar Husnah HABIB Manga, itama ba taya baya bace, a cikin dalibai Musulmai na cikin makarantar.
Dan ko kwanati a cikin award da aka bada na World hijab day, sai da aka bata kyautar yarinyar da tafi kowacce daliba saka hijab, tare da mata fatan Alkhairi ta dawo cikin makarantar lafiya.

A lokacin da yaga takardan gayyatar bai damu da yage ba, sai da yaji Dr Aahil yana zage zage, wai akan me za a karrama yar iska shine ya duba, aikuwa ranar da za ayi taron yaje cikin shigar jamfa na wata material na maza. Sai wando kaftani brown, yayi matuƙar kyau da Yasaka hula minister.

Shi yasa da yaje, sai ya saje da masu sallar, kamar ba Christian ba. Kuma har wasu daga cikin malamai musulmai sai da suka nuna mamakin su a fili, a karon farko da Dr Imran Shaikh Abdul Hakim, yayi mishi tayin shiga musulunci, murmushi yayi sannan yace.
"Dr Imran Shaikh Abdul Hakim! Abubuwan da kuke a musulunci mu Kiristoci bamu yi! Sannan ni da nake daya daga cikin manyan a cikin kungiyar CAN, me kake tunanin zan fuskanta. Ni bana jin zan iya wata addini bayan na Yesu Almasihu. Ruhin Ubangiji."

...... Kome Dr Imran Shaikh Abdul Hakim zai ce?!

Kuyi hakuri, pagen dan tsugul ne
[7/2, 8:55 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BAHAUSHIYA□

*Hattara Yan Mata*

*Wato ko dayawan mutane basu san inda darajar take ba!Nice zanyi nomar gyad'a na cigaba da kula da ita ƙar ta watsa ya banya!ina kula da ita ƙar sabida karwasu ciyawa da wasu dabobin su b'ata min ita, ƙar lokacin da zata zuba y'aya na roreta! Sai nayi tunanin na bawa mutanen da suke tare dani! Ba tare da naji kyashin kome ba!Amma kusan abin dariya! Sai kaji mutane na cewa A'a bazamu karb'e shanshara ba sai anyi matsarshi, sai an b'are! Idan na bare ace a'a bazamu karbi tsaban ba!Sai kinyi matsar shi! Hmmm! Maybe kai tsaye Hausawa su fahimta!*

Dr Alman.
Babi-sha-biyu.

"Ƙamar Yadda yazo cikin kowacce al'umma, ana samun b'ata gari da mutane na gari, babu addinin da basu dashi idan muka duba cikin addininku, which mean Kun fimu fahimtar waye Annabi Muhammad S.AW, kaje ka duba chapter din ku na original Bible. Domin an tabbatar da zuwan Ahmad After tafiyar Annabi Isah D'an Maryam  bayan karnin da basu kai dubu."

Mik'ewa yayi tare da tattara duk wani abinda yake mallakin shi, kama daga waya har keyn motar shi, yace.
"Imran! Addinin Kirista itace Addinin gaskiya! Domin itace Addinin da, sannan idan har akwai gaskiya a cikin addininku me yasa kuke wulakanta addinin ku? Taya ma kake ganin zan fahimci addinin da mabiyan shi suke zubda jini?! Duk wani terrorist na duniya zaka samu from islam ya fito!  Sannan kayi tsammanin zan fahimci haka! Karamin misali abinda aka yiwa Yarinyar nan Husnah HABIB Manga! VC namu musulimi ne! Amma saboda kuɗi ya dakatar da ita! Wanda nayi imani idan da Addininmu ne bazamu koreta ba, ba me yasa kuke son ganin kananun masu kokarinku sun fadi! Kasan me yasa Dr Aahil ya wulakanta Yarinyar? Toh kaje ka nime ma'anar haka! Ku musulimai ne a baki amma a zahirance Kun fimu karkata daga hanyar addininku. Ni yanzun idan nacewa Mabiyana karsu yi abu! Aka ce Governo yace akayi abun. Baza su yi ba, sabida  Ni Pastor Bature na hana su yi bazasu bi dokar kowa ba, sai nace su bi! Sab'anin ku da kome aka ce sai kunyi abinda ranku yake so! Am sorry."

Yana gama gaya mishi haka ya fice daga cikin hall din.

Bawai Imran ya rasa yadda zai fahimtar dashi bane, kawai zurfin da yayi a cikin addinin shi yayi yawa ne, musamman da ya kasance member na CAN! Toh sunfi kowa taurin kai a cikin Christian.

...... Fitar shi daga dakin taron, zama yayi a motar shi ya kunna Ac din motar, ya kurawa daya side din ido.

Tadda motar yayi, a zahiri tafiya yake amma a cikin zuciyar shi bai san inda yake tafiya ba, sai da tsinci kanshi a saminaka.

Parking yayi a gefen hanya yana me dafe goshinsa, tare da mamakin toh ina zai je?! Ina kuma yake shirin tafiya.

Har ya juya zai koma sai yayi lissafin lokacin da zai karfe nawa zai kai shi bauchi?! A cikin yan mintoti ya juyar da motar ya cilla akan titin, ya cigaba da shata gudu.

Awa guda ya kawo shi garin Rahama rishi, daga nan ya cigaba da tafiya, har ya wuce Garin Narabi?!

Karfe shida ya shiga garin bauchi, tsabar ya gaji bai tsaya a ko ina ba sai zaranda hotel, dan ita a farkon shiga bauchi.

Anan ya kama daki a hawa na na sha uku, daki na dari da talatin, yayi odar abinci.

Bai zo da kayan shi ba, iya na jikin shi kawai yazo da ita, dan haka yana hutawa wajen seven ya sauko ya shiga yar shagon Bouquet ya sayi kananun kaya ya haura dakin shi, dan yana da yakinin zai sameta a garin cikin kwanaki biyu da zai yi, a da bai da wannan tunanin sai da ya shigo garin bauchi.

Washegari..

---

Husnah POV

Yau da wuri muka shigo garin bauchi kawo ba.

Dan tare da Abdullahi ne muka bar Mubarak da Innarmu, a gidan.

Sai da muka iso, na tsaya a layi har aka zo kan Babanmu, layin na zuwa kan mu, na shiga da Baba.

Ja mishi kujera nayi ya zauna, na koma bayan shi na tsaya, nan ya shiga duba shi da mishi tambayoyi yana yi, tare da jefa ni cikin hirar, kin amsawa nayi dan bani son a dinga shiga hidimata haka.

Har ya gama ya kuma rubuta mana magani sannan yace.

"Babana karka kuma, yarda ka zauna inda ake tadda kura ko hayaki, dan ciwonka baya son su. Ranki shi dad'e African Queen a kula da Babanmu!"

Shiru nayi ban ce cikanka ba, muka fito da Baba, har mun fito sai ga Dan jaraba ya biyo ni, yazo yayita iyayi tare da tambayar daga inda muke, Baba da Abdul suka bashi amsa. Dan ko kallo bai ishe ni ba.

Yayi yayi nayi magana naki, daga nan suka yi sallama dasu Baba.

"Baki da kirki, mutumin nan yazo gurinki ne, amma kika ki amsa mishie."

"Kayi hakuri!" Na ce mishi.

Da Baba zai san yadda nake gudun maza da ba zaiyi tunanin kome kaina ba.

.... Yau ban je bank road ba, a tan doka road na cire kudi sannan na wuce central market naje nasayi magani da wasu abin bukata?!

Sannan muka bar bauchi.

Lokacin da na cire kuɗin, yana cikin bankin ecowa, ai kuwa ya nunawa Manajan, nan Yasaka aka bi inda naje na cire kuɗin bani nan.

Kamar zai had'iye zuciyarshi tsabar bakin ciki.

Haka ya gama shawagin shi bai ga kome kama dani ba, koda ya dawo zaranda ruwa ya sakewa akan shi, saura kwana uku tafiyar shi. Wanda zai dauke shi wata goma cif.

Waye ya sani ko sun mata aure da Manga?!
Wannan itace abinda zuciyarshi take kawowa a koda yaushe.
Ina bazata yarda ba! Tunda ta tsaya akan ra'ayin ta Allah zai bata wanda zai kula da ita.!

.... A hankali ya fito yana daure da towel, shirt da 3qst ya saka. Ya fito falo yana kallon ko ina, ta sama.

Kara wayar shi tayi ya koma dakin nan ya saka a kunnen shi.

"Mommah!"
"My Son! My God Bless."
Murmushi yayi sannan yace..
"Mommah! Wani abu kike so?!"
"My Son! Devanah! Tace zata bika idan kuka dawo za ayi bikinki"

"Mommah! Bazata bini ba! Kuma idan ta matsa min zan fasa aurenta."

"Toh my Son ba kome ta fasa!"
"Hmm!"
Yace mata sannan ya katse kiran.
Juyawa yayi tare da tattara kayan su, sannan je ya biya kudin wunin da yayi, a ranar ya bar bauchi.

....... Yau kwana biyu kenan, da dawowar mu daga Bauchi, ina kusada Maryam da take sakar hular jarirai.

Ta nutsu sosai, sai aikinta take Innarmu kuwa, zaune itama tana kunsawa Lu'lu'a lalle, da rana tsaka.
Dariyar su muke, dake gobe Ummi zata Toro ana bikin yar Alhaji dan Azumi.

Shigowar Abdul ya katse mana tsokanar lulu da nake. Inda yake cewa..
"Addarmu! Wannan mutumin na asibitin yazo yana waje da Baba!".

Dauke wuta nayi sabida bana son wani mu'amala ya haɗa ni da wani da namiji. Dr Bature ne na yarda dashi.

Ban ce musu Uffan ba har Baba ya shigo, yace min.
"Kije ku gaisa!"
Haka na tashi tare da barin abinda nake idanuna, cike da kwalla.
Na zumbula hijab har kasa sannan na fito, tare da Manga na hango su, daga yanayin fuskar shi na fahimci Manga gaya mishi magana ne.

A hankali na karasa gurin, tare da sallama, kallona yayi cikin murmushi ya amsa sannan ya kalli Manga yace..
"Ko da kuwa A gidan karuwai take da zama naji na gani, ina sonta haka, ni ita nake so ba halayyar ta b"

"Barka da zuwa African Queen!"
Kallon Manga Nayi sannan na kalli Dr.
Jiki a mace ya bar gurin, sunkuyar da kai nayi, cikin damuwa nace.
"Nagode sosai! Da tattaki sabida ni! Amma inda hali kayi hakuri, bamu dace da juna ba."

Daga haka na juya zuwa cikin gida, d'akina wuce. Sannan na kifa kaina a jikin pillow Ina shashekar kuka. Sosai nayi kukan, kafin na fito waje nayi alola tare da wanke fuskana.....

----
Jahar Adamawa..

Tana cikin yankin arewa maso gabas din Najeriya, jaha ce da ta haɗa kabilai mabanbantar addinai da halayya da zamantakewa.

Jaha ce me dauke da mafiya yawan fulani, da kuma manoma, sannan a cigaban rayuwa Allah ya azurtasu da Manyan mutane, kama daga mataimakin shugaban kasa, a lokacin baya. Sai wasu manyan mutane.

Imam Moddibo Usman Abubakar!
Babban Malamin addinin musulunci ne, Uwa Uba kwararren dan boko ne, wanda yake da ilimin sarafa kowacce irin samar da abinci na zamani da kuma na gargajiya.

Manomi ne, kuma makiyayi ne, sannan bazan ce kai tsaye waye shi ba, amma attajiri ne.

Ilimin addini ya lullube mishi bokon shi, sai ake ganin kamar bai san kome ba, sai dai idan ka zauna dashi toh idan ba kayi da gaske ba, zaka sha kunya domin yana cikin mutanen da aka dauka zuwa London lokacin da ake diban dalibai zuwa kasar waje karatu, lokacin mulkin turawan biritania.

Idan Imam Moddibo Usman yana turanci sai ka rantse da Allah bai jin fulatanci ko hausa,.

Imam Moddibo dan shekara  Saba'in da biyu, idan ka ganshi zaka zata bai kai shekarun ba, dan har yanzun Mahaifiyarshi tana raye.

Allah ya bashi arziki da samu, wanda ya zarce yan uwa shi, amma bai da kyashi e Hassada abin shi na kowa ne.

.....

Imam Moddibo yana da mata biyu yara Bakwai cif.

Uwar gidan Nenneh itake da Yara hudu, Amaryan Me yara uku, amma kafin wannan amaryan shi ya tab'a auren wata yar uwan shi wacce suka rabu da ita, ta haihu. Daya sannan suka rabu ya amshi d'an. Me shekara daya. Daga Baya ya auro Nenneh, sai Hajja Kubrah.

Itace me yara biyu, mutuniyar kirki, ga hakuri da jin tausayin duk wanda yake tare da ita.

Sab'anin Hajja Nenneh da take nunawa kowa kirkinta zuwa anjima zata sauya. Saboda bata da kirki.

Yau ma suna zaune an gama karatu, za a tashi Mahaifiyar Moddibo tace.
"Ya Allah! Duk munafikin da yake da hannu a tarwatsa gidan nan Ya Allah ka kawo mana sanadin da zai ji kunya! Duk algungumar da take da hannu a cutar da Fa'iz ya Allah ka lalata goben shi,"
cikin jimami, Hajja Kubrah tace.
"Amin Dadah,"

"Ina dalili? Haka kawai dan finfiritin bakin ciki, ace daga fita masalaci ace ayi kifinatin yaro, wallahi zan yi magana me yasa dan jakar kaniya ba a dauki wancan me bin yan mata kamar bunsurun ba, sai salihin yaro me halin d'an uwan shi, aka akayi kifinatin, Kai Allah ka tozarta wanda yayi mana yankar kauna da farin cikin mu. "

Kallon Imam Moddibo tayi cikin masifa tace.
"Kai kuma! Wallahi na rantse da Allah yau ba gobe ba, kaje ka dawo da Zuhrah, dan rashin Imani. Shekaru sama da kusan talatin da wani abu tunda kuka rabu taki kowa sai kai, bayan nayi Imanin sharrin mayar da kake son aura ne Yasaka ka rabu da Yar kirki"
Dafe goshinsa yayi, har yau baya manta abinda idanun shi suka gani, taya zai so ganin bakin dare. Taya zai manta bakin dare! Bayan irin so da kaunar Zuhrah da yayi sai ta saka mishi da kyautar bakin ciki.

Daga sandarta tayi ta mukawa yarinyar kusada Ita, wacce take ta daman tura baki,

Cikin masifa da jarfa tace.
"Yar banza me kama da halittar farko, Ni bansan dalilin da yasa Moddibo ya jajjibo mana rumada ba, taya gida bazai zama da Sharri ba"

"Deejangala! Kiyi hakuri, Insha Allah yaron nan zai fito, Fakizu Insha Allah, dole yan kifinatin su kyale min kai, Ai badan Jauro baya raye yaushe wani zai wulakantaka min zuria, dan Ni nayi imani da Jauro ya girma sai ya zamewa kowa Inuwar gajimare, Allah ya isa min, kuma Wallahi Moddibo sai ka dawo da Zuhrah. Sharrin da aka mata sai ya koma kan wanda yayi."

Ta mike Da kyar tana dogara sandar ta, gefe guda hararar Matar da take kusada Moddibo take

sabida tsabar tsanar da tayiwa matar, har zata fita tace.

"Moddibo! Wallahi kasaka idanu akan Kiyama da sungura, dan ina da yakinin yaran nan zuwa suke ana gwagure su, yara yan banza nasu shegen fitina cikin dare sai dai naji ruwa na zuba a ban d'akina, ana shaaa, sannan kayiwa, Rakifu magana ya daina cinye min dambu Nana na, Ke kam Deeji ai sai san Barka, ki cigaba dawa Takwarata Aminatu Addu'a itada Uwata Fatu, Shi kuma Fakizu Allah zai fidda shi."..

Sannan tabar falon cike da jimamin jikar ta da aka sace.

Fa'iz, shine Babban dan Hajja Kubrah, sai Aminatu takwaran Dadah, sai Fatimah. Ita kuma Maman Dadah.

Abubakar shine babban dan Hajja Nenneh, sai Siyamah wacce Dadah take kira da Kiyama, Sai Sughra wacce aka kirata da sungura, sai Rafi'q, wanda aka kira da Rafiku.....

[7/2, 8:55 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BAHAUSHIYAH□

*Hattara Yan Mata*

Hie

*Babi-sha uku*

Ban san me ya faru ba, sai ga baban mu ya shigo ran shi a b'ace, a raina nace wandanan mutanen!

Ruwa na dauko mishi tare da zama ina kallon shi dan Innarmu ta fita zuwa gidan su.

Sauke ajiyar zuciya yayi sannnan ya kalle ni, yace..
"Meye yasa kika sallame Dr Alman"
?!"

"Baki son shi?! Haka zaki cigaba da zama? Haka zaki zauna muyi ta kallonki."
Ya tambaye ni a raunane, sunkuyar da kai nayi, ina tuna abinda na rasa, wanda nasan duk na mijin da ya aureni sai ya tambaya ina na kai mishi tukuwaicin aurenshi.

"Baba! Nifa bana son shi! Kawai ya gane mana!"
Shiru yayi bai kuma ce min kome ba.

---

Dr Bature POV.
Yana gama hada kayan shi, kallon wayar shi yayi cikin damuwa, saka wayar yayi a haka bayan ya kashe baki daya sannan ya fito daga dakin, Devanah sai kuka take, dan tana tsaye a bakin kofar shi.
Karb'an jakar shi Daniel yayi, suka ci-gaba da sauka, har kasa suka sauko. Mommah ta kalle shi cikin kuka tace.
"Son zaka tafi! Ka cigaba da tsare addinin mu!"

Gyad'a yayi sannan yaje gaban Bishop Yohana Chibok, ya durkusa.
"Lord ga yaronmu Albarkanka ya sauka akanshi, Yesu zai tafi cikin salama da aminci ɗan ruhin ka ka tsare mana shi, Yesu bamu yi abinda zai zamana sacrifice, Yesu tun farko muka baka hadaya ga soyayyar mu, Oh lord gave him a good moments in the world, Jesus mentioned our son toh be a Great man in the world, God don't let any Destiny toh came to him. We shall sacrifice our Happiness for him, In the name of Jesus Christ! Fathar May all your blessing guide our son. Lord protect my Son from any bad destiny, My Lord am Hippocrates oath I with sacrificed everything to protect him from any bad moment."

"Amen!!" Suka ce baki daya, har zai mike Devanah tace.
"Jesus Christ closed Abraham eyes, don't let him look any lady."

Tausayi ta bashi, yana mik'ewa ya rungume ta, yana murmushi.
"Idan auren wata mace bayan ke is my Destiny baki da abinda zaki yi sai Addu'a."

Janye ta yayi sannan ya nufi inda Mommah yaje ya rungume ta, fita suka yi har da Joel.

Rungume shi Devanah tayi tana sauke wasu tears masu zafi, tace.
"I love you! Da duk zuciyata!"
"Nagode!"
Sannan ya shiga mota, kallon Joel yayi suka sake murmushi wa junan su, kafin suka bar gidan cike da kewar juna.

Deeply in side Dr yana jin so sad akan rashin haduwarsu da Husnah! But babu yadda ya iya tunda har ya bar bauchi sai da ya koma kofar bank din ko zai ganta.
Safe trip BYC...

Husnah POV
Wato idan kana son ganin bakin ciki, toh shiga inda babu ilimi.

Yau Kuluwa ta tashi da ciwon haihuwa, dan Yarinyar kafirin taurin kai ne da ita, tana wannan halin tazo gidan mu, tsaya daga bakin kofar shiga tace.
"Ma'ulle?!"

Ina daki na daga labule, Maryam tana cikin Kitchen.

"Shigo mana?!"

Dakyar take d'aga kafarta, ga ruwan titsiya da yake binta nace.

"Ke lafiya baki san baki da lafiya ba?!"

"Ai nasani, shi yasa nazo ki duba ni!"

Shiru nayi, ina tuna ko ina da handglob. Dake munyi it a cikin asibiti. Duba wata jakata nayi naga babu, tashi nayi na dauki biro da takarda na rubuta kome da zan bukata, na fito waje zan bawa Mubarak ya Sayo sai ga Mijin Kuluwa da Baba Yawale ana surfa Bala'i, mijin kulawa nacewa.

" Idan kaga wata tsohuwa ta tab'a min mata sai na harbe keyarta, har da kai kuwa, dan haka Husnah ce zata duba min ita."

Shima cikin arzuka yace.

"Wallahi karuwa bata tab'a min Ya, idan kuwa ta. Amshi Haihuwar Tsinanane nake!"

Rab'a su nayi na mik'awa Abdul nace.

"Maza ka fita zuwa gumau ka sayo min kayan nan"

Dake ba dake bamu rabuwa da Mashin, aikuwa suka fita da mugun gudu.

Rezar na dauka a shago na kalli mijinta, nace..

"Kaje ka kawo min kayan da kuka ajiye na zuwa asibiti."

Watsar da hannu yayi cikin zafin rai yace.

"Wannan mutumin banza ya kashewa kowa sa ranshi na niman ilimin boko,  na Addinin ma ya aka kare. Azzalumin mutum kawai wallahi ban da darajar Kulawa sai nasanya sojoji sun mata rashin mutunci baka sanni bane."

....... Rashin mutuncin kan sunyiwa juna, wallahi ba a haifi namijin da zai wulakanta min iyaye ba ahhe.

Matan garin kuwa kowa ta zuba ido, aga yadda zan amshi Haihuwa ina yarinya karama, ban da budewar idanu, aikin manya nayi karabanin shiga.

Bani da damuwa dasu, dan haka lokacin da Abdul yazo tana dab da Haihuwa na saka handglob na duba naga Haihuwar ce a kusa, ina d'ago kaina tana sauke ƙatuwar nishi, sai ga yaron ya diro.

Daukar rezan nayi na yanke cibiyar, sannan na maza na dauki zaren dinki na daure cibin, sannan na koma kan uwar na taimaka mata uwa ta fado, nasaka hannu na kwaso jinin.

Kafin wani lokaci na gyara uwar tsaf da jaririn sannan na duba kwalbar allura na mata, sannnan na fito.

Fitowa nayi da jaririn na mikawa Innarmu, sannan na koma dakin. Na taimaka mata. Ta

mike na bata zanina ta daura, sannan muka fita waje.

"Ehhyo ta amshi Haihuwar, Ikon Allah! Ashe dai abin ilimi ne."
"Kai tayi dace ne! Kawai wanda suka fita ma ai Haihuwar tana zuwa musu da matsala balle ita, ku jira an jima kufa sai ku yarda"

Ban damu ba, sabida aikina ne abinda na karanta ne, amsar Haihuwa.

Wannan karb'an Haihuwar ya janyo mana, wasu irin cigaba na musamman, domin kuwa mutanen da suke gudun mu sune suke zuwa gurina domin duba lafiyar matan su. Shagon mu kuwa kafin wani lokaci kome ya kara bunkasa.

Domin kuwa sayan kayan mu ake,

Sosai duk karshen sati sai munyi sabon sari, kankance me har kayanmu.

Zaman Maryam ya dame mu, sai muka yanke shawarar ta shiga makarantar tunda akwai a nabardo, Tunda bata gama Secondry ba, kullum Abdul yake kaita, idan za tashi ya daukota.

Lu'lu'a itama an sanyata, muma mun sami yar karamar Freedom.

---

Yola....
Moddibo Family....

Zaune yake cikin yan uwan shi ana tattaunawa, akan halin da Fa'iz yake ciki.

"Hamma Moddibo! Ina ganin kayi abinda dan kasa yace! Kawai na bar mishi kamfanin jirgin ka da suke Poland, wanda kasaka marigayi Jauro...."

"Amma Hassan ka bani mamaki, taya zai bar mishi wannan kamfanin bayan kai ma sanin kanka ne, kuɗin da ke shiga ta wannan kamfanin yafi wanda yake shigowa ta kamfanin jirgin ruwan shi na Canada, kai ko gonar audigan shi da take Accara yafi abinda Dan kasa ya nima."

Shiru Moddibo yayi jikin shi a sanyayye yace.
" Bai nemi kome ba, sai dai abu biyu. Na farko yace mu bar mishi wannan Jauro Estate! Na biyu nasanya hannu a kwangilar da yaron shi yake so!?"

"Toh Alhaji ka sanya hannun mana!" inji Hajja Nenneh,

Mik'ewa Hajja Kubrah tayi murmushin karfin hali tace.
"Kawai ka bar shi ya kashe shi, Da ka rasa Jauro kayi hakuri, sai da zaka rasa Fa'iz ne bazaka hakura ba"

Girgiza mata kai yayi cikin damuwa yace.
" Tura mishi zaɓi, idan ya amsa to shikenan!"

Bai rufe baki ba wayar shi tayi kara, yana dauka ake ce ga yaronka a asibitinka.

Hamdala yayi sannan suka fita baki dayan su.

---

Narabi...

Yau ake sunan Kuluwa, dan haka tun safe Innarmu taso shiga gidan, nima naso shiga amma na fasa nace zuwa dare zan shiga.

Can muna zaune da Maryam muna karatu, sai ga Lulu da gudu. Tana kuka wai wasu mata sun daki Innarmu.

Saka hijab Nayi muka shiga gidan, muka sameta durkushe kanta a kasa, wasu mata suna cewa.
"Barauniya sai kin fidda abinda kika dauka!"

Uwar Baba Matar Baba Yawale Tana gefe, da wani kodadden zaninta wanda yaji duniya, ita da Mamar kuluwa, suna cewa.
"An saba hali shine daga zuwa har ta xari kudin Adashen mutane. Toh wallahi sai kin fidda musu."
Goggo Kande tace.
"Hmm Ashe abin da ake fada gaskiya ne, daga zuwa har ta zari kudin mutane."

Bakin ciki ya hanamu magana, zuwa nayi na riko hannunta ta mike.

"Insha Allah! Sai Kun gurbi abinda kuka aikata, gamu ga duniya. Allah ya bamu yawan rai, Wallahi sai kun kasa daga ido ku kalle mu."

Na karshe maganar ina kuka.
"Addarmu! Muje kinji!" Inji Maryam,

Bamu fita ba sai ga Goggo Hajara tace.
"Wani kudi ake magana akai ina sallah?!"
Nan suka gaya mata, aikuwa ta kalli daya matar da take gefen inda Innarmu ta zauna tace.
"Tabbaye miko min Kudin nan"

Tabayyen matar Baba Haruna ce.
Babu kunya ba tsoron Allah ta mikawa Goggo Hajara kudin, dake ba a garin take da zama ba, kuma bata da wani masaniyar akan abinda ake mana ba.

"Yanzun dan rashin adalci har kun manta da halin tabayyen kuna daurawa Zainab sata, sabida k'iyayyar da kike nuna mata, wallahi kun yi asara. Duk abinda zaku yi kuyi amma tabbas Zakarar HABIBU tayi carr, wato har da Habu da Yawale ake wulakanta, Allah sai ya bi musu hakkin su, Ciki daya ba wasa ba! Amma kinyi wa kanku, kema tabbayye dan rashin imani kina jin ana niman kudi bayan kece kika dauka kika ja bakin ki shiru dan rashin Imani."

Sun santa masifaffiya ce, babu wanda yayi magana Gata da tsayi sai ta iya bawa mutum kashi.

Haka taron ya watse ana gutsiri tsome.,. Wata shirgeginyan mata wacce itace matar Baba iro ta fito tana cewa.
"Dadin abun bamu ajiye tsohuwar budurwa ba, idan sun matsu su aurar da ita, waye ya sani ko har da Uban a a masu haketa"

Wannan Maganar ya zama babbar Magana, domin dai baba ya Kai Makura sai da aka same unguwa, shima yace zai kaiwa dagacin Narabi, Inda Shima yace zai kai gurin me Littafi, shima kuma ya mika ga me gunduma, daga Nan shima ya mikawa hakimi!, Abinda ya mugun d'aga hankalin yan uwan baba kenan domin duk cikin mutanen da za a kai su me Littafi ya fisu rashin mutuncin, zai iya sanyawa a zane mishi mutum kome girman ka, sannan ya sanya akafta maka rashin mutunci.

Nan suka shiga bawa Baba hakuri, abinka da me sanyin halin sai yace ya hakura.

Aka dawo gida , sabon rashin mutunci suka kuma buɗewa. Bana kome ba, sai an dainawa Baban mu magana koda sallama yayi.
Sannan ko zama yayi a gurin sai an bad'a toka, Idan masallaci ne, ba a tsayawa a Sannun shi.
A hankali magana ya fito wai baban mu yana da tarin tb kuma daman tun can suke faɗa ba a dauka ba, sai bayan da ciwon shi ya tashi yana tari jini na fitowa, kuma shima hakan ya faru ne, ranar da suka je Gidan me unguwa.

Shine ciwon ya tashi sabida b'acin rai.

Wuyar da muke sha a hannun mutanen nan sai Allah kuma ba kome bane sai jahilci..

Kuma damuwar su kar Baba ya zama wani abu ko yaran shi, sai dai sun makaro.

---

A cikin shekara daya mun ci wata hud'u, babu labarin Dr banda Atm ɗin shi wallahi har

mantawa nake dashi, sai idan na ciro kayana zan yi abu zanga ATM din shi.

Murmushi nake kawai na kance Mr Arrogant!

Ina kake, ka barni da dukiyar ka Inata barna dashi.

Koda yake rabona da tab'a kudin tun wata uku Baya yanzun bana tab'a kudin domin sana'ar da muke Allah ya sanya mishi Albarka, ga Chajin lanter mutane da muke yi.

Uwa Uba an fara zuwa gurina Antinatel abin gwanin tausayi, ana kin mu kuma ana zuwa gurin mu, dan tun ranar da akawa Innarmu sharrin sata baba yayi fushi me zafi, wanda yace ko mutuwa yayi bai yarda Yan uwan shi su zo kan gawar shi ba.

A yanzu takai ko barci muke da zaran mace ta fara nakuda za azo kirana Mubarak yake rakani duk inda aka kirani,
Wannan ba kome bai ne sai Only hie! Daukaka waton...

---

University of Tokyo.....

Sanye yake da sweater, sabida dusar ƙanƙaran da ake musu, a lokacin sanyi.

Zaune yake a wani coffee shop, yana shan coffee, amma idan da zaka tona zuciyarshi, tausayin Husnah ce, ta cika mishi ciki da wajen shi, abu na gaba yadda zai cusawa zuciyar shi kaunar Devanah, iya kokarin shi kenan.

Yana gama sha ya ajiye kudi a kasar cup din ya fita a shagon, kofar church din da yake kallon shagon yaje.

Har cikin church din take gaban gumkin Jesus Christ, ya durkusa tare da rufe idanun shi ya haɗa hannun shi ya dunkule.

Ya fara da cewa.
"I don't know what is in side my mind, but Jesus mentioned me in hie people in Earth, Lord I can't believe how many times am thinking about that girl, Lord don't let any devil's to curse any bad destiny for me, am just Compassionately for her! Lord forgive me and my family, protect."

Tashi yayi ya sanya hannun shi a goshinsa da gefe da gefen shi sannan ya sumbata, ya juya zai fito.

Tsohon da yake kula da wasu al'amuran church din ƴace.

"Idan kaddara ta shata layinta! Toh babu wanda ya isa kauce mata, kai me Sa'a ne. Ban tab'a yiwa wani Magana ba, amma yau nayi maka. Kayi ƙoƙarin ka amshi duk abinda yazo maka me

kyau ko mara kyau a cikin su kuwa har da sabunta kanka da Wasu shatin kaddarar ka, dube tafin hannunka, ka gansu toh sune zanen kaddararka, tayu tun Haihuwar ka ce take zane tayu daga baya kaddarar tajuya maka. Koma ma menene, tabbas kai dan baiwa ne. Ba a cika samun irinka ba, miracles daga kwaryar idanunka kawai ya Wadatar. Lallai akwai al'ajabi a duniyar ka, akwai B'oyayyen al'amari da babu wanda yake son ya tallata maka.

Sai dai taki kadan zaka yi, zai iya sauya maka kaddarar ka, har abada kai din ma'abucin tausayi ne, da kyakyatawa Yakini, zaka yi nasara amma dole sai ka same jajjirtacciya Wacce tasan me ake kira da Kaddara, wacce kome zafin Bala'i zata zame maka garkuwa! Wacce bata da wani dogon addiction akan ka, wato buri. Yarona kayi ƙoƙarin inganta gaskiyar ka kayi ƙoƙarin ka rike amanar duk wanda yake tare da kai, Lallai Ubangijin da muke bautawa ya boye wata al'amari a rayuwarka"

Haka tsohon ya juya jikin shi na rawa yace.
"Yau mun gana ba lallai bane wata rana muga juna, kayi hakuri da yadda kaddarar ka yazo a haka"..

Shiru yayi yana kallon hannun shi, kafin ya d'ago kai mutum ya bata a cikin church din,

A hankali ya juya ya bar gurin, yana mamakin yadda mutumin ya gaya mishi, tunawa da yayi ai kawai irin wannan a cikin addinin su, kuma da yawa adam suka fadi abu tankar wata alfarma ce, dan haka zai iya kiran da mutumin da Miracles, me al'ajabi, kuma zai so ya abinda ya faɗa mishi ya tabbata bada gaske.

Tabbas zai iya yarda da hakan tattara zance yayi ya watsa a gefe sakamakon tunawa da cewa canfe ne babu kyau zai iya kai ga Yesu yayi fushi da mutum........

Tohfa kunji Yan Paid group sun ce ya isa batin da ake baku ya isa haka....

Inuwar Gajimare da Bahaushiyah sune ake sayarwa ne....

08130269641..... Domin niman shiga paid group taboni ta nan.....
[7/2, 8:56 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BAHAUSHIYAH□

*Hattara Yan Mata*

mock
***Babi-sha hudu***...

***Annabawa guda biyar da suka fi sauran daraja***! ***Allah ya basu Mujiza***/ ***Annabi Ibrahim***, ***Allah ya***

***ganar dashi tauhid tun kafin yasan waye shi*, *sannan mafi girman Mujizan*.**

***Annabi Nuhu Allah ya bashi ma mu'ujizan*, *sai Annabi Musa inda Allah wanda Allah ya bashi mu'ujiza ta inda yake sarafa sandar shi zuwa ga maciji*, *da kuma dukar ruwar da yayi koramar gidan fir'auna ta koma jini/ da sauran su*.**

***Sai Annabi Isah/ wanda Kiritoci suke kira Father of Miracles/ Annabi musa ya warkar da makafi/ kurame/ ya tadda matacciya/ Sai Annabi Muh'ammad S.A.W*) *shugaban duk wani manzo*! *Limamin Annabawa/ Allah yayi mishi tashi mujizan sosai*, *sannan dukkun su babu wanda yake amfani dashi sai da Ikon Allah*! *Ma'ani Ixinin Ubangiji*.**

.... ***Akwai mutanen da suke da baiwa su Haka Allah yayi su*, *suna da matukar hatsari*. *Domin ba dukkan sun*, *suke iya sarrafa kan su*! *Sannan akwai a cikin mu hausawa amma wani lokacin gani muke kamar Aljanu ne dasu*, *sannan a yanki Asia irin su India da bangaladash*, *suna da irin wannan mutanen*, *asalin su ana kiran su Masu Ilimin taurari*! *Amma a musulince haduwa da irin su akwai hatsari dan cikin ruwan sanyi suke turmushe maka imaninka*..... *Allah yasa mu*** Dace

...........

A yanzun Izgilanci da ake mana ya ɗan ragu amma bawai an daina bane, ana yi lokaci zuwa lokaci.

Tunda yanzun sun fara cin gajiyar baiwar da Allah yayi mana. Sannu a hankali al'amuran rayuwa suka fara sauyawa daga tsana zuwa girmamawa.

Zan iya cewa a yanzun fatan iyayena shine nayi aure, kuma har lokacin yanzun miji bai zo ba.

Haka muke rayuwar mu da dadi ba dad'i.

Mutanen unguwar mu sun dan fara damuwa sosai da rashin karatun yaran su musamman na islamiyya, a masallaci suke jajjantawa har suke cewa Baba ai jiya da bai zo sallah ba Ghaddafi ne yaja su Sallah shi ya kira sallah ma.

Daga yadda suke nanata abin yayi musu dad'i, kawai sai Baba yace.
"Idan kuna da bukatar karatun su za a bude musu islamiyya"

"Ai wallahi HABIBU zamu so haka! Kaga yaro karami yadda yake karatun Alkur'ani, yo ni ko lokacin da na tafi hajji ai sai labarawan da suke jan mu sallar nan nake jin irin karatun nan."

"Haba me gari! Ai mu a kaduna zaka ga yaro karami Allah ya bashi baiwar haddace Alkur'ani"

Inji Baban mu,

Shiru Mai gari yayi can yace.
"Akwai abinda yake damuna! Duk shekara idan nake aikin hajji."

"Subhanallahi! Toh meke nan?!" Baba ya tambaye shi.

Ajiyar zuciya ya sauke, dukda akwai mutane a gurin sai da Yasaka fuska dan kar a rena shi yace.
"Wato mutumin nan da ya b'ata mana! Lokacin aikin Hajji"

Zuba mishi ido suka yi Baba ne ya samu damar magana tunda dashi yake.
"HABIBU! Baka tab'a zuwa Makka ba, amma da kaje zaka ji ana cewa! Malam Hamza ya b'ata! Laaa baku ganshi bane, Malam Hamza ya b'ata"

Sake baki Baba yayi da ido, yana jin jina karfin jahilci mutanen garin shi, girgiza kai yayi cike da tausayi tare da bakin cikin abinda yaji mutumin da duk shekara sai yaje hajji...

"Allah ya taimake ka! Hajjinka bata yi!" Inji Baba,

"Inji waye?!" Ya tambayi Baba a fusace,
Gyaran zaman Baba yayi sannan ya shiga cewa.
"Hajjinka bata yi ba inji ni! Labbaika Lallahummah Labbaika, Labbaikai laashaarika Labbaikai, Innalhamda wanna'amata lasharika Labbaikai, wannan shine abinda kake cewa Ana niman wani ya b'ata"
(Sorry akan talbiyan idan nayi Kuskure! Ina karb'an gyara zaku iya gyara min Nagode)

Sai dukkan mutanen gurin suka zubawa Mai gari da Baba Idanu, sabida shine ya fara jure Mai gari cikin lalluma.

A dame me gari ya kalle shi sannan yace.
"Habibu! Ashe duk shekarun nan shirme na nake zuwa yi, shi yasa idan na dawo kaga na muntika kina Kai kace tsutsa, gaskiya sai ka koya min. Dan ina son nake nayi hajji karb'abbiya"

Nan Baba ya shiga musu bayani akan musulunci da shika-shikanta, da kuma abinda da ya shafi sallah.

Sannan ya roke su da su bar yaransu suna zuwa karatu, gidan mu.

Nan Baba Habu ya kwashe da dariya, sannan yace.
"Toh bari ga yadda za ayi."
Kai Baba Yawale yace.
"In ruwa ta hura wuta ba"

Tsakanin su da Allah suke Izgilanci ta sigar dariya, Baba bai kula su ba, dan ya musu uzuri a rayuwar shi, kuma zai cigaba da musu uzirin har karshen rayuwar shi, dan yayi alqawari bazai kuma fushi da abinda suke mishi ba.

Sai da Me gari yayi musu barazanar kai su gurin me Littafi sannan suka daina mishi dariya.

.... Muna zaune ana cin abincin dare, nan Baba ya ture nashi da hannu. Alamar ya koshi.

Shiru yayi na wasu lokuta, sannan ya sauke ajiyer zuciya, zuba mishi ido muka yi kowa ya tsame hannun shi a cikin abincin muna kallon shi.

"Kuci abincin ku! Yau naga abinda ya bani mamaki"
Jin haka sai gashi mun cire hannun mu a cikin abincin mun zuba mishi ido.

Nan ya zauna ya bamu labarin abinda ya faru, kai Abdul Mugu ne, na bugawa a jarida, dariya yake har yana tintsirawa.

Kai Ghaddafi yace.
"Toh shi malam Hamzan an same shi kuwa? Tunda ya b'ata ne lokacin aikin Hajji"

"Ina kuwa Bawan Allah! Ai bazasu same shi ba, sabida ba b'atan yayi ba, kawai rashin mai da hankali ne irin na mutanen mu, kinsan Allah Innarsu! Sun rigani zuwa makarantar allo, amma Kinga wata shirme wai malam hamza wani ya b'ata." Ya karshe maganar cikin murmushi.

Gyara zama nayi sannan nace.
"Baba wannan garin akwai matsala sosai, musamman na rashin ilimin addini, matukar bazamu tashi tsaye ba toh wallahi idan fushin Allah ya tashi kama mu, sai mun wahala, dan haka yana da kyau abu de musu yar islamiyya tunda akwai karamar rumfa a waje, sai mu fara koyar dasu, su ahlari da kitabul Tauhid, tare da Littafin kawa'idi."

"Wannan haka yake Addarmu,! Babu wasa Insha Allah! Da yardan Ubangiji sai mun wayar da musu kan su sosai."

"Allah yasa idan su Yaya sun bar ku ba"
Inji Innarmu,
"Sallama dai! Wai Husnah tazo inji wani a waje"

Kallona duk suka yi, na b'ata rai, na cigaba da gogewa Lu'lu'a hannunta, tana kallon na.
"Addah zan rakaki?!"

D'ago kaina nayi na kalli idanunta,

Sunkuyar da kai tayi tare da gyad'a min Kai.
"Husnah baki ji ana Nimanki bane?!"

Mik'ewa nayi, sannan na nufi cikin dakin mu nasako hijab me hannu, na rike hannun Luluh muka fito. Daga yanayin mara mutunci na fahimci Manga ne!

Karamin tsaki naja aikuwa suka fasa min dariya da wani katon muryan su.

"Kunga itace nake son na mallaka daren mu na farko, awara da dundunkwalo zan kawo mana,"

Aikuwa suka kuma saka dariya,, dayan yace..
"Zamu na zuwa ganin irin soyayyar sharukan da karina"

"Amma kasan ta tsufa a dandali wannan baza ka bita a nitse ba da zafi zaka bita,"
Suka kuma fasa dariya,

"Kuma naji ance akwai kayan hutu, don Allah idan mun zo bazaka kore mu ba"

Suka kuma fashewa da wani dariyar.

Ba a tab'a min Izgilanci irin na yau ba, sai naji a raina, da zan iya musu wani abu ban ce kome ba, na juya abuna.
"Laaa! Amaryan mu zata koma Cikin gida tsaya mana ko sumbatar nan a miki zaki yarda da Jarumin mu"

Idanuna ko kallon gaba na bayi, na shiga cikin gidan, zama Luluh tayi jikin Baba tana gaya mishi abinda ya faru a wajen, bai ce kome ba sai ma bani hakurin da yayi.

.........
A sannu muka fara koyar da karatun safe, wanda yaran basu wuce goma sha uku ba daga gidan me gari, idan aka tashi baba yana saya musu alewa, abinka da yara sai suka fara gayawa yan uwan su ai idan kazo makarantar malama Husnah ana raba alewa.

Kafin wani lokaci har mun tara yara sama da 50, kuma suna fahimtar kome.

Tafiya ta fara mikewa, bakin ciki kamar ya kashe su Baba, amma basu da yadda suka iya damu.

Sai dai Izgilanci kan babu lefi domin suna haduwa da iyayen yaran zasu fara musu dariya wai sun dauki yaran su . Sun kawowa karuwa.

Basu masu kula su, domin iyayen yara since sun huta da fitinar da yaran su , kuma

da suna jin dadin yadda yaran suke fahimta dan haka babu ruwan su a cikin al'amarin yaran su.

Sannu a hankali kofar gidan mu ya kasa mana, dole muka raba abin wasu suka shiga zauren mu, Maryam da Ghaddafi suna koya musu.

.......

Yau Alhamis babu makarantar, dan haka zan mai da Baba Asibiti, ina gama shiryawa, muka fito.

Wannan karon ni da Ghaddafi ne sai Baba, haka muka zo bauchi muka gama abinda zamu yi sannan muka komo, gida Ban tab'a kudin Dr ba. Sai .a kokarin tattaro mishi duk ribar da na samu a cikin shagon mu.

---

Bishop Yohana Chibok..

Kiran layin Dr Devanah take yi, amma fir yaki d'agawa. Joe ya kallon ta sai murmusawa mata yake.

A dame ta kalli Mommah cikin zubda kwalla tace.
"Mommah! Yaki dauka zan bishi.
tokyo kawai"

"Karki fara dan zaki samu saba'ni ne dashi." Inji Joe,

Hararar shi tayi cikin jin haushi tace.
"Munafiki! "

Dariya yayi sannan yace.
"Ban damu ba! Bature ne dai bazaki sane shi ba, dan koda kin kira ba zai dauka ba"

Daukar matashin kuran tayi ta jefe shi da shi, tana kuka.

Dariya Daniel ya yake musu, dan wani lokaci tsakanin Joe da Devanah kamar tom&jerry, haka tayi kukan ta, har ta koshi.

Ita dole sai taje tokyo. Joe ya ce.
"Zaki gwajin farko ne? Tunda kin san dai baiko kawai aka muku, kuma shi bai da ra'ayin gwajin kwayoyin halittar jikinsa."

Kiran shi tayi cikin damuwa tace..
"Wallahi sai nayi maka rashin mutunci, kuma sai naje bazan dawo ba sai da ciki dan dashi za ayi bikinmu."

Tana gama fad'ar haka ta bar falon zuwa sama....

---

Japan... In Tokyo

Farin wanda har kasa ne a jikin shi, sai shimi, yayi rubda ciki, tare da kifa fuskarshi a pillow, yana juyar da kai yake cikin damuwa dan daga yadda yake juyar da kan shi zaka fahimci akwai matsala.

Yasan dazun Samantha ta bashi ruwa dazun da tashigo, dan yana cin abinci ne ta shiga shi kuma bai dauko ruwa ba shine yace ta bashi ruwa don Allah.

Tunda yaci abincin ya shiga wannan halin ko nace ruwa.

Jin yayi an kwanta a bayan shi, tare.

Juyawa yayi tabbas ita ce, cikin b'acin rai yace.

"Me kika samin a cikin ruwan da kika bani"

Zare towel tayi tare da kwanciya a jikin shi, dukda halin da yake ciki baya jin zai iya biye mata, tureta yayi. Ranshi a ɓaci yace.

"Ki fita kafin na wulantaki,"

Ganin yadda ya birkice mata yasata mik'ewa da sauri ta saka kayanta.

Ta ficce mishi daga gidan, drowe gadon shi yana da sauri ya ciro wata yar roba, ya bude kwayoyin magani ya hadiya har guda hudu, goran ruwan kusada shi ya daga sai da ya shanye tass, sannan ya kwanta.

Bayan kamar minti goma kacal, barci me nauyi yayi gaba dashi.

.......

A yanayin da suke ya tabbatar mishi cewa, ta tafi da duk wata damar da yake tanadin shi, sabida jin daɗin kasancewa shi da ita. Ya kara mishi kwarin gwiwar abinda take mishi. Wani irin abu yake ji, tare da rungume ta.

Ji yayi an finciketa daga jin daɗin shi, ana tafiya da ita, shima kuma ana janshi.

Kokarin kwace kan shi yake, domin inda ake jan shi, was so darkness, ita ce take inda haske ya, kwace rikon da aka yi mishi yayi ya falfala da gudu, sai dai an sami akasi domin akwai wawakeken ramin da ya shata tsakanin su.

Durkusawa yayi ya kwalla mata kira da Hus.........

Dr Aahil kana ruwa💔

Good Morning....

[7/2, 8:58 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BAHAUSHIYAH□

Highlights
Babi-sha-biyar

Tashi yayi yaji gabaki daya ya zubda abinda yake dankare a matan shi, wanda har sai da yaga damshin sa a jikin farin wandon shi.

"Husnah! Why she?! But Jesus why you sent in to my dream?"
Wannan itace abinda Dr yake tambayar kan shi. Bai taba jin kome a ranshi ba, sai tausayi toh me ya kawota cikin mafarkin shi.

Ganin hasken da wayar shi yayi yasa shi daga kiran sabida Sunan Blessing Mom,

A kasalance ya d'aga Kiran ƴace.
"Mommah!"

"My Son! Ya kake?! Da fatan baka da wata matsala?!"

Lumshe juyayye idanun shi yayi cikin nutsuwa, sannan ya sauke ajiyer zuciya yace.
"Babu Mommah?!"

"Toh Allah ya maka albarka! Amma me yasa kak'i daukar kiran Devanah?!"

"Mommah! Karfe nawa?!"
"Karfe huɗu na yamma," ta bashi amsa a takaice.

"Toh mu nan hudu na safiya ne,! Kinga ta kirani tsakiyar dare ina barci kuma"
Nan yayi ta mata bayani har ta fahimta.

Har suka yi sallama bata daina jaddada mishi muhimmancin shi a rayuwar su ba.

......
Doris Yohana Chibok, yan asalin karamar hukumar Chibok ne na jahar Borno, Doris Babanta baban Reviren ne a church Catholic charities dake garin Chibok, Suna da kakkafewa akan addininsu na Kirista, nd basu da son shiga hidimar kowa,

Mahaifin doris Amos Eshaya da Mahaifiyar Doris yara uku suka haifa, Jacob sai Doris da

Ezrah, Mahaifin Devanah.

Mr Yohana yaron Amos ne, yazo daga wani kauye kwandiga na cikin jahar Borno, karatun addinin Kirista gurin Mahaifin Doris, Kawai suka fada soyayya.

Ganin Yohana mutum ne mai matukar biyayya da addini, tasa suka bashi auren Doris tare da bashi matsayi babba a church Catholic dake garin Chibok.

Anyi Shagali sosai, sannan aka kai bawa ango matar shi, inda suka tafi can aka dagargaji amarci.

Bayan shekara biyu, wasu irin falala da samu suka shigo rayuwar ma'auratan guda biyu, daga cikin har da samun karuwar yaron su wanda suka sanya mishi Bature kasancewa shi din yafi su farin fata. Shine suke kiran shi da Bature, sun kai shi. Church Baban Doris ya ganshi.

Dafa kan shi yayi cikin damuwa sannan yace..

"This child! Yana da karfin miracle! Yana tare da mu'ujiza me ƙarfi zai ta muku abin al'ajabi bi, dan haka ku dauke shi ku tafi Rome dashi sabida haɗuwa da manyan manyan papa roma, domin killace shi har ya iya sanin kanshi.

Karku gina shi da wata akida sai ta namu, domin idan kuka barshi zai iya zame mana kalubale.

Karku bari mace ta shigo rayuwar shi, in ba haka ba zaku iya rasa shi, ku gina mishi zuciyarshi da kin mata, koda basu a kida daya, amma karku barshi ya kawo wacce yake so? Domin itace mafarkin rugujewarshi.

Kunga yaron ku, ga line of destiny din shi, ga kuma line ko Ya'ya yayi Crossing dis line everything zai sauya, my Daughter and my Son In-law, ki k'iyayye, karku sake mace ta shigo rayuwar shi, Yarone da yake da kashin arziki!

Yarone da yake da baiwar arziki duk wanda zai zo kusadashi, sai ya zama wani abu.

Hanyar Arzikin ku ne yazo gare shi. Karku tab'a barin yayi fushi domin zai iya zame muku samuwa da rashi.

Karku sanya shi yayi abu dole, sabida jinin shi cike take da Izzar attajirai!

My daughter, yaron ki shine yaro mafi al'ajabi a wannan ƙarnin. Behind good and bad line! Akwai Love and Compassionate! Uwa uba! Line of destiny! So karku yarda da sadaukarwa! Daga ranar da kuka barshi ya sadaukar da wata abu daga cikin akidar mu! Ban san me zai faru ba."

Daga haka yayi musu addu'a sosai, sannan ya kuma basu addu'o'in, musamman na Evil

lady! Karta shigo rayuwar shi.

Sannan suka tattara shi suka koma Rome dashi can aka haifi Joe da Daniel, Devanah kuwa mahaifiyarta baturiya ce. Kanin Mommah Ezrah ya aureta dake tare suke a can.

A can Italy, a can suka zauna tsawon shekaru talatin da biyar, lokacin Bishop Yohana ya bautawa Addinin shi tun kafin ya dawo CAN suka bashi matsayi na Musamman.

Tun Bature nada five years suka haɗu da Aahil Aliyu Maitama,

Tun Doris da Bishop suna bakin cikin abotar Bature da Aanil, gashi basu kaunar fushin Bature shi yasa suka hakura, kuma abin mamaki yadda Allah ya bunkasa su.

Dr Bature ya karanci anatomy me, yayinda Dr Aahil ya karanci Biology.

Akwai banbancin halayyar tsakanin, domin shi mutum ne mai mugun kyamar zina, sabida tarbiyyar da yasa mu, baya son shiga harkan mata, sab'anin Aahil da ya zama na mamajo.

Bature baya da yawan magana, sannan idan zai yi toh akan addinin su, a bangaren addini kuwa toh har tsoron shi wasu mutanen suke.

Kowa na mamakin yadda abotar Bature da Aahil..

Har suka nemi aiki a A.B.U zaria

----

Ajiyar zuciya ya sauke, taryo tarihin shi, murmushi yayi sannan ya tashi zaune yana me jin dadin irin nasabar da yake da shi.

□□

Tambayar bazata ne ya zo min daga Baba, zufa da tsoro e suka kamani.

"Asma'uh ! Baki bani amsa ba yaushe zaki koma makaranta, ina ta zuba miki ido, tsawon wata hudu mun shiga na biyar. Meye nufinki da zaman gida."

Kafin na tattaro duk wata bayanin da zanyi mishi Mubarak ya amsa maganar da cewa.

"Ai baba! Lokacin da ciwonka ya tashi kace ta dawo gida zamo koma Narabi. Dalilin da ya janyo tayi asarar wannan shekarar dole ta sake mai-maita shekara."

Shiru yayi yana kallona nayi tsamotsamo, tare da zaro ido bakina yana rawa nace.

"Dama ina son zan maka bayani lokacin da muja Bauchi na tura sako ta cafe, shine suka ce an dakatar da ni na tsawon shekara d'aya. Yanzun saura wata."

Shiru Baba yayi amma da alamu bai yarda ba, kawai baya son zargi ya tabbata a tsakanin mu shi yasa ya share, ya kuma min fatan Alkhairi.

....
Wannan yanayin da nagani a fuskan Babana, ya sanya ni kuka. Sosai sabida duk wata hope din da yake a kaina na kasa, sannan na fadi warwas.

Allah ya isa min da abinda Dr Aahil yayi min domin ya gama cutana, ya rabani da duk wata burin da Iyayena suka daura a kaina.

Dare mahutan bawa, amma Ni ina kan abin sallah ina kai karar Aahil ga Allah ina kuma niman karfin da zan rama abinda yayi min, a cikin wata biyar zuwa shida, nasan iya adadin bakin cikin da naci.....

□□
Karatun da muke na safe iyayen yara sun kara rokon Alfarmar ayi musu na yamma,, na dare ne dai nace a'a sai suka ce toh a bari ina koyar da iyayen yara daddare, haka ya kara bakanta ran yan uwan Baba.

Har suka fara jifarmu da cewa.
Ai koyawa mata yadda zasu yi lalata muke.

Kai magana marasa mutunci da dadin ji, abinda ya basu haushi da suka gama surutunsu, sai ga mazajen da suka turo matan su suka musu caaa..

Rayuwa me tattare da kalubale, tankar baiwar Rahman Ubangiji ne, domin Kuwa mun zama nakiyan kan kabari maganin me kwalama, gamu nan dai amma mun gaggari yan tsurku.

---
Adamawa State..

Tsakanin Alhaji Muhmood Dan Kasa da Imam Moddibo Usman, abun ya zazzafa Wanda takai, sai da Governo da Mai Lamidon Adamawa suka shiga maganar kasancewar Daga Moddibo har Dan ƙasa, dukkan su manyan mutane ne masu daraja da kima uwa uba, su din wasu j-j ne a jahar wato,

Dan haka suka sanya su a gaba da cewa.

"Imam Moddibo! A matsayin ka na babban malamin a cikin Jahar nan, mun hada ku Anan ne. Don ku sassanta kanku, wannan abinda kuke bai dace ba, kune jigon siyasar jahar nan, sannan ai ko ba kome Dan kasa kamar kanine maka, don Allah ki ajiye duk abinda yake tsakaninku."

Shafa farin gemi shi Imam Moddibo yayi cikin dattako, sannan yace.
"Allah ya taimaki Mai martaba, ya wuce a gurina. Abinda nake bukatan sani shine Yarona Fa'iz da yake hannun shi, ya sake min yarona"

"Karka min sharri kazo ka zauna kamar mutumin Allah nan kuwa munaf....."

"Hattara dai! Dan kasa a gaban Mai Martaba kake, ba ayi ya shashiyar magana. Dan haka akul kar harshen ka taja maka mummunan aiki!"

Girgiza kai Imam Moddibo yayi, fatan shi Fa'iz ya fito daga hannun Dan kasa.

"Toh wai ni kam meye janyo wannan al'amari?!".

Taimakin Gwanman Adamawa yayi musu wannan tambayar.

Gyara zama Ɗan kasa yayi cikin jin haushi ya fara magana.
"Meye kuwa bayan mutumin nan me kama da jan gwanda ya k'amk'ame kome ya hana kowa cigaba. Baka isa ka sami kwangila a gwamnatin ban ba sai wannan mutumin banza yayi ma sanadin an hanaka, taya bazan ji haushin sa ba, da aka tashi bada appointment na siyasa, tunda aka janyo wannan mutumin aka bashi Kwamishinan noma ya k'amk'ame kome, yanzun kamfanin da za ayi na sarrafa takin zamani, ina saka ran zan samu ni da Yarona sai naji wai shine akan aikin da Injiniya Fa'iz, wai an basu aikin noma takin zamani."

Nan ya dinga tonawa kanshi asiri da yadda ya tsanin Imam Moddibo, har yake gaya mishi ya kula dan bashi daya yake fakonshi ba, Akwai na jikinshi a musu kin shi kuma matuƙa bai dai na. Mamaye kome ba tabbas yayi kuka da abinda zai sami Fatima da Amina ba, dan ya lura kamar yadda yake nuna son kai a waje haka yake nunawa a cikin gidan shi.

Imam Moddibo, mutum ne da Allah yayi mishi hakuri sosai, amma bai iya jure cin amanar ruhi, ajiyar zuciya ya sauke sannan ya kalli D'an kasa yace.
"Toh naji zan janye daga duk wata abu da aka nime ni a kai, Sai dai nayi Imani da Allah ka kiyayye fushin Allah akan abinda kayi min, ka kiyayye fushin fusatace, ba ita Aminatu"

Da sauri ya d'ago kai yana kallon shi. Yana nuna shi da yatsa.
"Haka yace tabbas haka yace."

Yana fadan haka ya tashi daga falon sulhun ya fita da sauri gudu gudu.

Yana kuma mai-maita abinda yaji Moddibo ya faɗa.

......

Mamaki ne ya kama su Imam da Mai martaba da maitamakin gwamna, suka bawa Moddibo hakuri da kuma nuna mishi baso don ya ajiye mukaminsa, domin sun san sami karuwa da shi kan shi kanshi da dukiyarsa, domin yana iya saka dukiyar shi a cikin abubuwan gwamnati idan an samu riba a bashi hakkin shi.

Daga fadar sarki Asibiti ya wuce.

Inda Fa'iz yake kwance.....

□□

Alhamdulillah, makarantar ya bunkasa fa domin baba ya fara koyar da maza, musamman irin su Mai gari! Gudun kar a kuma Malam Hamza Wani ya b'ata (🤣😂👈🏻)  kuma abin burgewa suna dauka, domin basu damu da zigar da ake musu ba.

Kuma idan kaga yadda mata suke dauke karatu da sai kasha mamaki domin, ko wani abu ya shiga musu duhu zaku ji suna tambayar mu, haka ma mazan ma haka.

..... Muna wanki sai gasu Fadilah ta shigo, ta zauna tare da tura min baki, dalibana ce.

Cire hannuna nayi a cikin wankin ina kallon ta.

"Malama!  Nifa bani da lafiya?!"

Cike da mamaki nake kallonta sannan nace.

"Kamar ya?! Baki da lafiya"

Ganin yadda su Innarmu suka zuba mata ido, sai ta tashi ta rogo zaure, biyo ta nayi ina na tsaya daga bakin kofar, ina kallon ta.

Kuma da matar aure ce, ba a jima da auren bane, shine take min shiririta, dake tun last week nace mata kamar tana da juna biyu, tayi ta min shirme har da kuka ita babu ciki yaushe ma ta yarda da mijin, ba koda aka yi sai biyu ne! Sai da na toshe mata baki dan zata fara yanko min wasu manyan bayanan tsaron sirrin ta.

"Kin kira ni kuma kina ta min shirme! Baki ina wanki bane?!"

Juya min baya tayi sannan tace.

"Malama! Maganarki ya tabbata, juna min biyun ne dani"

Takowa nayi inda take na dafa kafad'arta, nace.

"Na tayaki murna! A yanzu za a zama Uwa ko? Toh idan kin sami lokaci gobe kizo na duba ki.".

Juyata nayi naga tana kuka, riko hannunta nayi, na kanta d'akinmu, nace.

"Menene na kuka?!"

"Malama bana son Shine, ni da nake son na fita naje nayi karatu irin naku, taya zan iya karatu da yaro, malama ance karatun likitanci kika yi meye zan sha cikin ya zube?"

Murmushi nayi sannan nace mata.
"Ke abin murna ne ya same ki? Ai ciki baya hana kome, haka ma D'a baya. Hana kome?! Sannan ke abin murna ne a gare ki. Baki gan ni har yanzun babu mijin aure ba, kin san ciwon da nake ji a haƙa toh ki godewa Allah da ni'imar da yayi miki."

Nan nayita mata nasiha, sannan na rakata har kofar gida......

Domin kasancewa a group bin Bahaushiyah kayi min magana ta nan 08130269641......
[7/2, 8:59 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BAHAUSHIYAH□

*Hattara Yan Mata*

1 Year challenge..

Babi-sha-shida

A cikin shekara guda da muka yi mun mun amshi jarabawarmu hannu bibbiyu, na farko dai kafewa da baba yayi akan sai nayi karatun boko, na biyu. Fushin mahaifa yana tare da fushin Allah,

Na uku rashin addu'o'in akan kome da muke bukata, sai rashin niman zabin Allah.

Wadannan sune suka jagoranci wannan matsalar da muka fuskanta, amma Alhamdulillah ban cika shekaran ba Baba ya faɗa da bakin shi. Duk abinda ya faru damu shine silah....

A cikin wannan yanayin Baba Yawale ya fara wani irin ciwo.

Sosai fa, gashi babu halin kai shi asibiti.
Dole suka sami Baba da maganar jikin shi, Baba na ganin shi yace.
"Wallahi ciwon bata zaman gida bane asibiti zamu kai shi."

Ai kuwa Baba Iro da Baba Habu da Baba Haruna suka ce basu kai shi ba.

"Amma da kun bari an jaraba, tunda." Cikin fada suka rufe Baba har da cewa.
"Bazamu kai shi ko ina ba, sabida mun san me ke samun shi, sharrin da kuka kulla mishi sai ta koma kanku."

"Ni kuma?! Wallahi bani da wata manufa"
Ya gaya musu araunan. Amma suka rufe idanun su, suka mishi sharrin ai shi yawa Baba Yawale Yasin me tafiyar rana.

Haka yaje shi da Allah, duk da halin hakuri na Baba sai da ya rike Abin a ranshi wanda haka ya masifar d'aga mana hankali domin saka abin da yayi a ranshi yaso d'aga masa ciwon shi.

Sai gashi ba akai Baba Yawale asibiti ba mu mun kai Baba Asibiti.
Dake a toro kwanan shi biyu muka dawo.

Saura wata  wata biyu kacal na koma makarantar, wanda na tsananta addu'o'in sosai, har Azumi muke da Innarmu, dan haka shiri nake sosai.

Domin kuwa na mikawa Allah alamarina, kuma na maida hankali na akan duk motsin yan uwana da dangina, amma zuciyata tana cike da fansa abinda  Aahil yayi min amma dole sai da wanda zai min jagora zuwa makarantar.

---
Wata goma da yayi baya kasar bai hana shi jin kamar karya dawo ba, duk da kewar da yake yi na wasu abubuwan, idan ya tuna da Devanah, sai yaji dama ya zauna, idan ya ɗebe tsamanin da gani na sai yaji ran shi ya b'aci, kamar yayi ta zaman shi a tokyo, tunda ba zai samu abinda yake da tsananin don gani.

Shigowa Samantha tayi suka gaisa, komawa gefe tayi tana matsar kwallar, ya tako har gabanta, sannan ya rike hannunta yace.
"Kinga ni dake muna da banbanci, kuma ina da matar da zan aura har anyi mana baiko, don Allah kiyi hakuri karki raba min hankali gida biyu., Zan yi alfahari idan kika zauna a duniyar ki."

Dan rungume ta yayi sannan ta sake mishi kuka.
Daga nan ya dauki jakar shi ya fito duk wanda suke gaisawa sai da suka ji babu dadi har ya gama abinda ya kawo shi zai koma.

....... Daren juma'a ya sauka a garin abuja, Mommah da Father sai  dai Devanah wacce take ji kamar zata shige jikin shi dan murna.

Haka suka zo gida ananta hidima dashi...

---
Tabbas ya auri matar da yake so! Sai dai matsalar bai da kwanciyar hankali, domin kuwa mugun zarginta yake dan tun sau daya da ya tab'a ganinta a kofar wani hotel a garin kaduna, yaji zuciyarshi kamar zata fado.

Matar shi na aure, me tazo yi a hotel?!
Ko kafin ya same ta har ta shige cikin hotel din haka ya gama dubata, karshe ya gwada kiranta sai gashi ta dauki kiran, yace.
"Kina ina gani a hanya ina dawowa!"
"Ok Allah ya dawo da kai lafiya.".
Sam Sai yaji bai yarda da ita, domin kuwa, taya gashi ya ganta zata ce, ita tana zaria.

Kamar mahaukaci ya kama hanyar Zaria, abin takaici yana hanyar da zai kai shi zaria road sai gashi an hada wani husuma wanda taja dole ya hakuri sai da aka bawa damar wucewa.

Lokacin da ya iso ya sameta tana barci. Tun daga nan sai ya soma taka tsantsan da ita, wanda haka yasa shi mata kule sosai.

Tana zuwa islamiyya, ya hanata zuwa. Duk inda take zuwa indai akwai Maza Aahil ya hanata.

Kamar tayi hauka ta gayawa Iyayen su, akayi ta zama amma fir yaki ya rage takurawar da yake mata.

Kuma dan tsiya bawai ya daina mugun abinda yake yi bane, shi dai matar shi ce kar ayi da ita.

Haka yayi janyo musu rikici dan yace bazata bikin kawarta ba, aikuwa tsabar kishi kai Aahil ki kasuwa baya barinta fita sabida kar wani ya ganta yayi mata magana.

Ana haka ta sami ciki, Amma dan wulakanci, sai da ya zubda mata da cikin. Karshe ya dauketa ya kaita asibiti aka k'ak'aba mata implanin.

Kuma dake masifar bin mata tayi masa yawa, har yau burin shi Husnah, dan duk macen da ya kwanta da ita yana tashi sai yayi magana yace.
"Dalla dubeta, da kofar shiga kamar rijiya"

Karku yi mamaki hatta matar shi haka yake zama yace mata.
"Zaki nunawa Husnah kyau ne amma dan dad'i kayi sex kamar ka haura gajimare ai Sai Husnah. Ba irinki da ana tab'aki zaki fara hawaye duk lalaci ya cinye ku. Ita ko yaushe na bukace ta zata zo, kuma kayi kome da ita bata damu ba sai ke, tur."..

Wannan Iskancin da yake yi mata ne, ya sanya ranar ta haukace mishi, shi kuwa ya rufe ta da duka.

Wanda ya sanya aka kwantar da ita a asibiti.

---

Satin shi biyu da dawowa daga Tokyo, bai fita ko ina ba, iya kar shi abuja.

Dan haka yau ya hada kayan shi. Devanah tasaka shi a gaba sai kuka take mishi.
Bai kulata ba yana ta kokarin hada kayan shi, dan haka yadda ta mike kawai ta rungume shi, juyawa yayi dan ya dakatar da ita, sai dai kafin yayi wani abu tasan mishi bakinta a cikin nashi.

Dake shaidan ya sami mafakar siyasa, aikuwa ya amshi tayin ta. Suna daga tsaye har sai da suka zube, a gado.

Zuciyarshi da kwakwalwar shi bata buƙatar abinda ke faruwa, amma gangan jikinshi yana maraba da wannan yanayn, ganin yau Allah ya bata shi bata yi wasa da damar ta, dan haka duk inda tasan zata iya tab'awa dan ya motsa nan take yi idanunta a rufe, jikin shi ya amshi sakonta.

Duk yadda yaso tabuka kwatar kanshi, ya gagara, dan haka ya barta ta cigaba da juya shi don ran ta.

Buɗe idanu yayi ya kalleta yadda take, niman tab'a mishi, Kamfanin sadarwan shi(🤔🤣😂 Yanzu sai wata tace ikon Allah! Ita mai Dambu ko wani bu sai an sami sunan 🤐 muke tunda baka da burodi amma ai Kanada kamfanin sadarwa)

Caraf ya riko hannunta, yana girgiza mata kai.
"Baka da lafiya ne a Manhood dinka?!"

A shake yace.
"No Ni bana son haka!"

"Na rantse baka isa ba!"
Ta faɗa masa a fusace, tana ƙoƙarin saka hannun ta a cikin wandon shi.
Tureta yayi, ta fadi. Kallon mamaki tayi mishi idonta na kawo ruwa.

Tashi tai ta rufo kofar tare da ɗaukar keyn tasaka a cikin bra dinta.

Zaro Ido yayi cikin b'acin rai ya tashi yace.
"Bani key na, sannan ki fitan min a d'akina!"
.
"Ai na rantse bazan fita, sai ka gaya min baka da lafiya ne?!"
. "Kifita kafin raina ya ɓaci!" Ya buga mata tsawa.
"Na rantse bazan fita ba sai ka gaya min, meye matsalar ka akan mace."

Shiru yayi yana kallonta ran shi na kara fusata, kamar ya mata rashin mutunci, amma ba zai iya ba. Kuma dan tsiya sai kwaɓe mishi kaya take a gaban shin.
Sunkuyar da kai yayi yana me jin bakin ciki da b'acin rai, ji yaƙe kamar ya kurma ihu, ko zai samu sauƙin Iskancin da take mishi.

Kuma kan shi na sunkuye tazo, gaban shi. Tare da durkusawa.
Dafa shi tayi, bai san lokacin da idanun shi suka rufe ya tsinka mata mari.
"Dauki kayan ki! Kafin nayi miki abinda bazaki manta dani ba."

Mik'ewa tayi dan jin muryan shi take kamar zata fasa gidan, ta dauki kayan ta ta saka tare da barin mishi daki, dake ran shi ya b'aci ko shirin bai karasa ba, ya kwanta jikin shi na rawa.

Shi yasa bai cika son ran shi na b'aci ba, domin idan ya fusata jikin shi har wani rawa yaƙe ina dalili yarinya sai kace ba mace me kunya ba, tazo tana mishi Iskanci da rashin ta ido.

........ Har yamma bai fito ba, sai da Mommah tazo dakin ta zauna tana cewa.
"Don meye ya hadaka da Devanah, kuma ta fito tana kuka."
Shiru yayi mata haka ya tabbatar mata da tabbas bata kyauta mishi ba, dan haka tashiga bashi hakuri har ya fara ajiyar zuciya, kafin wani lokaci zazzaɓi ya rufe shi.

Kwantar da shi tayi ta fito, zuwa d'akinta ta dauki magani taje ta bashi, sannan ta zauna a gurin tana shafa kan shi.

Har barci ya dauke shi. Fita tayi daga dakin taro har dakin Devanah, tace.
"Me kika mishi?! Shin an taba so dole ne? Ko ance miki yana sonki ne?! Haka kawai kin hana min Yaro sakat ayi magana kice ba a sonku. Ku ɗin kuma abin da ya dace ne, rabona da na gan shi cikin wannan halin kusan shekaru talatin da takwas, yaro ne kunya da da'a, shine zaki zo ki sanya shi cikin damuwa.

Toh ga zoben ki, dama sabida ni ya amshi tayin ki, idan yayi miki kike can ki kashe kanki, Shi yasa kullum nake addu'o'in sabida karya ga yarona shaidanun mata irin ki, tabbas na yarda kece shaidaniyar da zaki raba ni dashi. In ba haka ba me yasa zaki Wani zo kisan shi a cikin mugun hali Muguwa me mugun nufin, ina ma turoki akayi toh zai koma kanku.

Aure ne ance ba ayi sai me? Kije akwai mazaje da yawa a duniya ki bar min yarona don Allah, karki kuma samun shi kije ki nemi abokin rayuwarki.

Yarona yana da rayuwa me kyau. Dan haka kar na kuma ganinki anan gidan.."..

Tana gama fad'ar haka ta juya tabar dakin . Tana fita kuwa Devanah ta saka kuka me matuƙar cin rai, domin bata tsammaci maganarta zai zafaffa haka ba. Meye laifinta.

Dan taso Bature sai tayi laifi, haka tayi ta kuka, har dare bata fita ba, dan tace bazata bar gidan ba sai ya bar garin.

Mommah kuwa abinda yasa tayi fada gudun kar wani dalili ya b'allo musu tekune, shi yasa tayi mata iyaka don bazata dauki wannan kasadar ba, yadda ya saba dashi nan awayi

gari wata tayi mata Wuff da d'anta...

....... Washi gari.
Da wuri ya bar Abuja bayan yasha addu'o'in da kariya kar Allah ya raba shi da sharrin shaidaniyar mace.

Wacce zata iya ruguza mishi tunani.
Tunda ya isa kaduna dake jirgi yabi, Kungiyar su ta CAN ce ta turo aka dauke shi zuwa Zaria..

Yana isa ya samu an gyra da mishi ofishin sa, inda ya sami karin matsayi zuwa senior lacture, haka ya kara mishi daraja a idanun mutane dama ..

Sai dai matsalar yaki magana da kowa, sai da Dr Imran shima sabida case dina ne yayi mishi magana.

Haka ya cinye satin bayi da lokacin kan shi sai na aiki da wasu abubuwan, ranar asabar ba tare da yayi wata doguwar magana na ya kama hanyar bauchi.

....... Wannan karon ma ya gama yawon shi bamu hadu ba, haka kuma rabon a cire mishi kudi a cikin account ya jima, jikin shi yayi masifar sanyi, domin ya fara zargin ko anyi aurena ne, haka ya tattara ya dawo.

Bayan sati biyu yana son zuwa, ga Aahil da yazo mishi da zance, ya samu labarin inda nake a bauchi.

"Ai abu yayi kyau?!" Ya ce mishi a takaice.
"Gaskiya abokina tun da na rabu da ita, ban kuma samun nutsuwa ba, zanje koda zanyi Sa'a ta amince min, idan iyayen ta sun sa baki sai na watsa musu ita, kaga cikin sauki na maida ita karuwa me lasisi!"

Bai d'ago ya kalle shi ba, amma yaji zafin maganar...

"Kuma Abokina wallahi har yau ina rena matan da nake mu'amala dasu, domin Husnah tafi so kome,  Insha Allah nan da Weekend zanje na ganta, na kuma nuna ina sonta, domin mu karasa wasan"

"Allah ya bada sa'a?!" Dr yace mishi, dan bazai iya magana ba, idan ma yayi tabbas abinda yake cikin ranshi zai fito. Sai yayi shiru ya cigaba da aikin shi Har Aahil zai fita yace.

"Tana bauchi, can local government din Bauchi wato toro, tana wani dan kauye wai narabi, zanje a matsayin wakilin makaranta, idan iyayenta basu san da kome ba sai na rufa mata Asiri mu cigaba daga inda muka tsaya..."

"Hmm" kawai yace mishi. Aahil na fita, yaja tsaki, cike da bakin cikin Iskancin da Aahil yake kuma ana kallon shi ba atab'a dakatar dashi ba...."

---

Ina zaune, bayan na gama cin abinci wani yaro ya shigo da gudu yana haki yace.
"Malama mau! Wani mutum a waje yana kiranki! Kin ganshi ne yayi kyau Sosai......"

Toh Fa.....
An kusan gama Free pgs...
Gashi an kusan Fara Game?

Insha Allah.....
Page The Game yana zuwa.....

Domin shiga paid group....
08130269641......
[7/2, 9:00 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BAHAUSHIYAH□

*Hattara Yan Mata*

Manga!

Babi-sha-bakwai.

D'ago kaina nayi cike da mamaki, yo Allah na tuba tunda na shigo garin narabi, ko namijin fara bai tab'a zuwa inda nake ba balle namijin mutum.

Kallon Yan uwana nayi naga suma mamaki suke, can sai ga yara a guje, har suna shirin faduwa.
Sai ihu suke, Malama Kiga bakon da yazo ya bamu kudi mu raba.

"Waye??!"
Na tambaya a takaice,
"Wani me kama da mutanen cikin tv?!"
Dumm kirjina ya buga Dr Aahil?!

Cikina ne ya bada wani irin sauti, kululu. Kamar zan fasa kuka na dauki hijab Dina me hannu, sannan na kalli Luluh da tayi tsuru tsuru.

Mika mata hannuna nayi ta mike tare da shiga daki ta dauko hijab ɗinta, kallon su Innarmu nayi sai ga hawaye sharrrr.

Na rasa meke min dad'i.
"Toh kije mana!"
Innarmu tace min.
A hankali nake jan kafana, wata bakar audi 2018 na gani, ji nayi kamar zuciyata zata fito daga cikin kirjina.
A hankali nake takawa, har na isa gefen motar, kaina a sunkuye.

Ga uban kwalla da yake zuba da mugun gudu, daga Idanuna.
Sauke glass din gefen shi da nake yayi bakin shi dauke da toothpick, yana sarrafa ta. A bakin shi.
Juyowa yayi tare da zuba min ido.
Buɗe motar yayi sannan yace.
"Beautiful Girl! Zo Nan tunda Auntynki kuka ya zame mata, madubin dubawa ta."

A kagge na d'ago kaina, muka zubawa juna ido. Jikina ne ya dauki rawa, cikin tashin hankali da firgici nace.
" Dr Bature!"

Rufe bakina nayi jikina yana keerrma, duk sai na diririce. Ƙamar na zura da gudu.

"Shigo mota!"
Yace min a takaice,
Kallon su Baba Haruna nayi , tare da girgiza mishi kai,

Bai kuma min magana ba ya kalle ni, na wani lokaci, sannan yace.
"Baki iya girmama bakon ki bane?!"

Da sauri na koma cikin gidan, na dauki kofin silve na cika mishi ruwa, ajiyewa nayi na tuna muna da Faro a shago, na dauki. Kular abincin Baba wanda Innarmu tayi dambun Shinkafa.
Na saka a tire, tare da jerawa. Sannan na fito, kicibis nayi da Manga yasha gabana, fauce tiren yayi sannan ya watsar dashi, sannan ya riko suma na da karfi, yana jana, abinda ya fiddawa Dr Bature da sauri daga cikin motar shi tare da Luluh, wacce ta saka kuka itama.

"Manga sake Ni?! Manga ka bari idan na sallame shi sai kayi abinda ka saba na tijaranmu."

"Naga shegen da ya isa miki magana, tunda na fahimci ke din baki gane Yaren da nake miki baki san ke din mallaki.."
Ban san meye ya gani ba, domin Dr ya iso, yana jijjiga, Luluh.

Sake ni yayi da sauri ya bar gurin, cikin wani irin kuka nace.
"Kayi hakuri! Abincin da zan kawo maka ne."

Kusan a tare dashi muka durkusa, yana kallona. Ina share kwallar dake bin idanuna.

Daukar cokali naje yi, muka dauka a tare, da sauri muka kalli juna. Nice na fara janye idanuna da hannuna.

Sannan na kuma kai hannu zan dauki filet muka dauka a tare.
Kauda kai muka yi a lokaci guda, Luluh tace.
"Laaa! Addarmu yau sai kallon kuda kuke,"
"Ya labari?!"
D'ago jajjayen idanuna nayi, na dan kalle shi, kafe ni yayi da idanu. Sannan ya juyar da kan shi.
"Ohhhh! Manga ko? Kuma."

"Husnah! Wannan shirmen fa?!" Kin tsaya shiririta." Inji Baba,

D'agowa Dr yayi cikin nutsuwa ya gaida Baba, sannan ya mike da Luluh a kafad'arshi, ya koma gurin motar shi.

"Waye shi?!*?"
"Malamin mune?!" Na bashi amsa a takaice,

Shiru yayi ina bin bayan shi,
"Toh taya aka yi, abinci ya zube a hannunki."
"Baba Manga ne?!"
. Ajiyar zuciya ya sauke sannan yace.
"Ki nima mishi, abinda zai ci"
Shago naje na dauki cus-cus, tare da wasu kayan aiki na shiga nayi mishi kunun cus-cus, ɗin sannan na juye mishi a karamin bowl.

Ina zuwa na samu yana hira da luluh kuma kamar bankad'e mishi kome luluh,.
"Sauko ki wuce idan na shigo gidan sai fasa bakinki, tunda kin koyi gulma"

Zaro Ido tayi irinta yara idan sunji za a zane su ta kalle shi zata yi kuka tace.
"Bako nice na gaya maka Addarmu kullum sai tayi kuka?! Ince kai ne kake tambaya na, suwaye a can. Ni kuma na gaya maka sun tsanemu"

Dariya ya saka tare da sumbatar goshina yarinyar, juyawa yayi Bayan motar shi ya dauko wani katon kwali ya mika mata, yace.
"Daga yau ni ba bako bane! Ni Uncle Ba ne, kuma ki cigaba da min aikina ga chocolat, sannan Allah ya kai mu zan zo miki, kawo kunnenki na gaya miki kin san muna da yan sa'ido."

. Magana suka yi tare da fashewa da dariya har da tafawa.
"Zoki wuce ko na sab'a miki"

"Ya Haka Malama! Ko kina kishi da kawata ce? "

Tsuke fuska nayi cikin alamun da gaske nake, da sauri ta fito daga motar na sami keyarta na maketa.
"Sai nazo zaki gaya min yaushe kika zama haka, mara jin magana, ai sai."

Da gudu ta shiga gida tana dariya, dan sun manna min hauka shi da ita.

Saka mishi abincin nayi ina b'ata rai, ina ajiyewa. Meemah tana isowa gurin.

"Addarmu! Inji Baba wai ki shigo dashi dakin zaure."

"Toh! Zaka iya biyo ni."

"Inda baki yi tsammani ba, zan iya binki har can" kallon bakin shi da yayi maganar nayi, cire saman suit din shi yayi sannan ya bar na ciki fari me dogon hannu.

Lokacin da muka shiga gidan, na buɗe mishi dakin su Mubarak, dan addu'a nake Allah yasa a tsabtatace ne, muna shiga naji har da room fresh, suka saka,
Ajiye abincin nayi zan juya na ganshi jingine da kofa, ya hard'e hannunshi a kirjinshi.

Sunkuyar da kai nayi.
"Am sorry! Ban san yadda aka yi ba nayita kwasar kudin ka, and dashi nayi jinyar Babana sai kuma"
Na fashe da kuka, na cigaba da bashi labarin abinda ya faru. Takowa yayi gabana.

Ya mika min hanky, sannan yace.
"Saura sati nawa ki koma school?! Wannan lokacin na abu biyu ne! First Class! Da kuma, zaki iya ko kuma na juya abuna."

Kura mishi ido nayi ganin, shima kallona yake, amna ba abinda nake ganin ya faɗa bane, domin idanunshi wani yare na daban yake gaya min, zare ido na nayi cikin nashi, sannan nace.
"Bani da wannan halin!"

"You can do! Because Aahil is susceptibility" ya faɗa min.

Girgiza kai nayi murna na rawa nace.
"Hmmm! Am not strong enough!"

"Inji waye? Zaki iya"
"Ok kaci abincinka nagode!"
Na koma gefen shi na tsaya, juye da fuskar shi yayi,. Ya zuba min ido,
Jin kai fin idanun shi nayi har cikin zuciyata, takurawa nayi a gefe, jikina na rawa.

"Relax! Ni bada mugun nufi nazo gare ki ba! Dan haka jikinki ya daina rawa."

Jin shi nake kawai, yana matsa min ina bud'e kofar, carak naji ya riko hannuna.

A firgice na kalle shi kamar zan sake mishi kuka nace.
"Dr Haramun ne! Tab'a macen da ba muharramin ka ba, and Idan kayi dubi muna cikin addinin mabanbanta ne! Don Allah idan kana son na cigaba da ganin girman ka, stop."

A hankali ya janye hannunsa, a wuyar hannun na.
Sannan na fita, yadda na fitan haka na dawo na same shi da Littafin Ahlari a hannun shi, ajiyewa yayi, zai dauki Alkur'an ni nayi maza na dauka ina me tsare shi da ido.

"Kur'an ba gama garin books bane irinsu, Attarura, Injila,Zabure, tare da sufi Ibrahim. Littafi ne mai tsarki da daraja, dan haka Please karka nayi saurin tab'awa, tunda kai baka da tsarki."

Gyad'a min kai yayi sannan ya cigaba da cewa.
"Toh am sorry for the!"

"No ni ba fushi nayi ba" na faɗa mishi a takaice, ina tattara duk wani littafi me daraja a gurin, shima durkusawa yayi yana kallon yadda nake, cizon bakina sannan, kuma na lashe bakin, murmushi yayi sannan yace.
"Ina son tafiya kuma kinki muyi magana"

D'ago kai nayi sannan na kalle inda na ajiye abinci da ruwa bai tab'a ba.

"Taya zan saurari bakon da bazai ci abu daga hannuna ba?!". Na tambaye shi ina kallon fuskarshi,

Juyar da kan shi yayi zuwa gurin abincin sannan yace.
"Ban iya cin abincin ni daya bane!"

Kamar nace mishi toh ai sai ka zauna na baka, tunda haka ka zaɓa.
Sai na share shi nace..
"Hmm"
Zama yayi sannan ya koma kan abincin ya fara addu'o'in, juyawa nayi cikin jin haushi nace.
"Stop that praying, in ba zaka ci ba ka barshi dan na fara gajiya da abinda kake min, yau daya ka addabe ni, ka hanani."

Ayya tashi yayi daga kan abinci.
"Ko zaki min magana da su baba da Mama zan wuce yau."
Mik'ewa nayi na isa gaban shi.
"But the food?!"

Girgiza min kai yayi, cikin murmushi.
"Am ok!"
Shiru nayi ina tsaye a gaban shi, na rasa gane kai na, me yasa nayi mishi magana ai da na barshi yayi yadda yake so.

Cikin shashekar kuka nace.
"Kayi hakuri! Kaci koda one spoon ne"

Zuwa nayi gurin abincin na diba jikina na rawa na kawo mishi.
"Kayi hakuri, duk addu'o'in da yayi maka kayi, Domin addinin mu yana girmama bako."

Amsa yayi ya zauna a hankali, sannan ya fara ci. Kallona yayi sannan yace.
"Kece kika dafa ko Mama?!"

"Kaci abincin! Sunnar ce babba idan ana cin abinci ba ayi magana, gudun kar a kware." Na gaya mishi,

Sai da yaci sosai, sannan ya ajiye cokalin, mik'ewa yayi.
"Ka zauna! Idan kasha ruwa sai ka mike".
Komawa yayi, tare da zama, yana kallon gefen da hisnul musulin yake ..

"Karba ka sha"
Garin karba hannun mu ya hadu, kallon juna muka yi, sannan na janye nawa, ya sha ruwan.

Tashi nayi sannan nace.
"Tashi muje ku gaisa, dan nasan yau zaka koma."

Na riga shi fita, dan haka na samu tsakar gidan a gyare tass, ce mishi nayi ya shigo.

A hankali ya shigo da cewa.
"Gafaranku mutanen gida."
Kallon Juna Maryam da Mubarak suka yi, Innarmu ce tace.
"Lalle maraba, Barka da zuwa."

Da Hausar shi wacce kana ji kasan kabila ne shi yace.
"Yawwa! Mama mun ishe ku lafiya"
. murmushi Innarmu tayi sannan tace.
"Lafiya lau! Ya mutanen gidan!"
"Sai godiyan me ceto!"

Da sauri Luluh ta fito tare da hayewa jikin shi tana cewa.
"Uncle b! Kaga Addarmu sai da ta ja min kunnena! Wai sai ta yanka ni tabawa Dog da pig nama na Tunda bana ji"

Murmushi yayi sannan yace.
"Karki damu! Sai na mata bulala, nima"
Sannan ya juya ga Innarmu yace.
"Jikin Babanmu! Ubangiji ya kawo mishi Salama a cikin lafiyar shi"

"Amin! Jiki da sauki!"
Fitowa Baba yayi suka gaisa, sosai. Sannan yace.
"Nan da Sati biyu Husnah zata dawo makaranta, shine nazo naji ko zaku barta ta koma! Dan ni na zata ko tayi aure ne!"

Gyara zama Baba yayi sannan ya fara da cewa.
"Nayi bakin cikin da tayi rashin jarabar ta na karshe, toh Amma kasan Al'amarin Ubangiji, gashi mijin bai zo ba, amma muna nan muna mata addu'a, Allah ya kawo na gari! Toh badan kazo ba bana jin zan iya barinta ta koma jami'a, sabida a cikin watan nan naji yadda yaran suke abinda bai dace ba! Kuma kaga mace ce, su nake na kaita gidan mijinta cikin kwanciyar hankali. Amma tunda kazo, tabbas zata koma. Amma don Allah ka tayani tsare kimarta. Mace ce dan tsautsayin kadan zai iya jefa ta cikin damuwa, ba ita ba har mu iyayenta. Don Allah na baka amanarta. Daga ganin ka Na yarda da kai don Allah karka zubda yardan da take zagaye da zuciyata da idanuna!"

Jikin Dr ne yayi mugun sanyi, zufa na karyo mishi, tare da sunkuyar da kai yace.
"Baba! Nayi maka alkawarin ni da kaina zan dawo da ita idan aka yi hutu"

A gaban iyayena yayi musu alkawarin rike amanar da aka bashi, sannan da zai tafi muka taki shi yana dauke da Luluh,.

Yana isa gurin Motar sai ga Manga.
"Kai Dan iskan kauye!"
Ya kira Manga, jikin shi na rawa ya isa gaban shi, buɗe boot yayi sannan ya ce mishi.
"Sauke min wannan kayan dukka, ka kai cikin gidan su Husnah, sannan kazo ina son ganinka!"

Da sauri ya shiga dauka yana kaiwa yana dawowa, bugun Shinkafar, rabin bugun wake, manja galan da mangyad'a, kwalin kifi, kwalin taliya da makaroni, sai katan na manyan gwangwanin peak na gari me guda shida, 7000g da na milo, sai kwalin sigar me iyali, sai Indomitable.

Fitowa Baba yayi yace.
"Yaro meye kake haka?!"

"Baba! Albarka nake nima! Ka sanya min kawai."
"Allah yayi maka albarka, ya jibanci al'amuran ka duniya da lahira."
Baba yayi mishi Addarmu sosai, bugun semo Manga ya dauka, yana kallon yadda na rabe a

gefen.

"Ai wallahi kin more! Irin wannan mutumin idan ya aureki don Allah ki dauke ni, me miki aiki."

Tsaki nayi tare da share maganar shi.
"Nagode! Sosai! Bani da abinda zance maka!"

"Toh! Amma kinsan yanzun da can baya akwai banbanci, dan one Year challenges da kika fuskanta ya ishe ki, and ban san me zaki dauki zuwa na ba, amma ki fahimci wani abu daya.".

Shiru yayi tare da sauke Lulu, ƴace.
"Ina son ki koma Schl! A wayayyar mace! Me Class! Wacce zata iya kome dan kare kanta! Sannan ire irin Aahil suna nan da kawaye bila adadin, me kika shirya?!"

"Ban shirya kome ba! Sai dai wani karamin Game! Wanda zamu buga idan na shigo, Nagode da hidimar da kayi, sannan ban rike lissafin nawa na barnatan maka ba, amma zaka iya dubawa sai ka gaya min akwai kudin da na ajiye domin ina tunanin shine wanda na taba na."
Buɗe motar yayi sannan ya ciro wasu takardun, ya mikawa Luluh yace.
"Tun kafin na tafi! Japan na maida sunanki kai, toh ban ganki ba, amna wannan Atm ya daina aiki, ga naki nan."

Shiga motar yayi sannan ya kira Manga, Ina kallon su suka bar garin, bayan yayi mana hidima sosai........

The Game....... Loading 🌺
[7/2, 9:02 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BAHAUSHIYAH□

*Hattara Yan Mata*

Babi-sha-takwas

The Game..

Ina tsaye har na daina ganin su, ji nayi ance.

"Munafukai ina zai kai mana yaron mu!?"

A razane na juya ina kallon Baba Habu bakina na rawa. Na ma rasa me zance Mishi.

"Zaki bani amsa ko sai na falla miki mari!"

"Ni Ni Ni ma ban sani"
Kauuuu ya tsinka min mari, wanda ya gigitani. Har sai da hancina ya fashe.

Kuka na fasa tare da rike fuskana.
"Zaki min magana ko sai na takaki"
Wani irin shakurarren kuka nasaka mishi.

"H
Jar buhu me tsaba, me algarara, Hajiya Husnah gaya min me zanyiwa wannan tsohon kwanon"
Inji Manga,

Zaro Ido nayi, cike da mamaki, yaushe gayen nan ya sauya haƙa

Tsakani da Allah Manga yake shirin Baje Baba Habu.
Shan gabanshi nayi cikin tsoro nace.
"Don Allah ka rufa min asiri, kafata shaye shaye ne?!"

"Alqur'ani da kin barni na kaddamar mishi, Yasin ko tsohona ne tace zai tab'a inuwar Gidan Baba HABIBU sai na samface mishi keya, Hajiya shiga abinki baki da damuwa da kowa, ki taka Uban kowa ki kwana lafiya, Ni Manga sai na sare kan mutum da gariyo na"

Ikon Allah nace a raina, yaushe Manga ya koma haka?
"Dr mana! Shine yayi wannan aikin!"
Shigewa nayi cikin gida dan bazan iya jin haukar Manga ba, domin zantuttunkar shi yana niman sani ciwon kai.

Ina shiga cikin gidan, na same yan uwana, ana ta labarin Dr.

Wani Jaka Meemah ta bani, cikin murmushi, tace.
"Ehhee! Our Addarmu! Hmmm! Nima Allah ya bani like your Handsome "

Duka na kai mata, Mubarak ya kwashe da dariya, Abdul yace.
"Addarmu! Wallahi gayen karshen ne! Shiga dakin mu Kiga har yanzu da kamshin perfumes din shi, Gaskiya kin iya riko wuyar Gayu."

"Kuma Ya Muba! Sun dace da!"

Ina jin su, da suka isheni da yabon shi ban san lokacin da na buga musu tsawa ba da cewa..
"Dalla kuyi min shiru?! Kunga mutum duk hankalinku ya tashi, waye ya gaya muku soyayya muke dashi, malamin na ne. Kuma yadda kuka zake nan ba musulmi bane! Arne ne!"

Na fada musu a raunane wanda ni kaina ban san nayi hakan ba, sai dai na san kiran shi arne yayi tasiri a zuciyata sosai.

"Toh meye kuma na kuka? Tunda arne ne ai shikenan! Mu dai muna son shi haka." Inji Meemah,

Tsaki nayi zan shige daki.
"Toh mukan muna yin shi kuma Allah yasa ya musulunta a sanadinki"

A fusace na juya ina kallon shi nace.
"Idan kace tausayi na yarda! Amma musulunci! Ga members Christian Association of Nigeria! CAN! Kasan me kace! Toh ma taimakin shugaban CAN ne na kasa, shugaban matasan Catholic na arewa baki daya, zan iya yarda idan Ankita shi me ruwan musulunci, amma ya Musulunta is not easy! Domin zai ya zama fada tsakanin Musulmi da Christian."

Ina gama fad'ar haka na shige d'akin, ina kuka. Wanda ban san dalilin shi ba.

---

Shigowa Innarmu tayi ta ganni zaune da kayan da Meemah ta bani.
"Asma'u! Meye na kuka?!"
"Innah ban sani bani!"
"Toh ko dan anyi maganar malamin ku ne"
Gyad'a mata kaiai nayi,
"Toh baki son maganar shi ne?!"
Sunkuyar da kai nayi, naja hancina. Sannan nace,
"Inata musu bayani sunki su fahimce ni babu soyayya kamar yanda suke tsammani, shi ne ya bani haushi."

"Shine abin kuka amma ai kanenki ne! Kuma dole suyi miki musu, lokacin da yazo naga bakon yanayi a tare dake! Jikinki na rawa kika dawo dan ki karrama shi, idan na fahimta yana da wata muhimmanci a tare sake. Sannan naji kina cewa shi din Ahlun kitabi ne Ko?! Toh tunda babu soyayya don Allah ki tsare kimarki da addinin ki, koda akwai soyayyan dole ki kula da kanki. Husnah muna bukatar nutsuwarki da kamalarki don Allah karki watsa mana kasa a ido."

Innarmu tayi min nasihar da tasani kuka, sannan tayi min addu'a sosai, sannan ta bani shawara yadda zan kame kaina dan kar ya dauka abun hannun shi ne yasani nake bibiyar shi.

..... Bayan sallah isha muna zaune a tsakar gida.

Bayan mun gama cin abinci Baba ya kalle ni, sannan yace min.
"Dazun naji kuna shirme da kanenki shine har da kiran mutumin da yazo gurinki da arne! Husnah me yasa baki da harshe! Kullum harshenki yana yawan kaifi sosai, kome sai kin aibanta alkiblan shi.

Idan Arnen ne baki godewa Allah ba, mutum ya dibo tafiya tun daga kaduna ko nace zaria, amma bayan tafiyar shi ki bishi da maganar arne. Bana son haka domin kar wata rana kiyi kuskuren da bazaki iya gyarawa ba."

Haka baba yayi min fada sosai, sannan ya tashi ya koma dakin shi.

Nima dai Yau kukan dare ya kare tunda yanzun ina da tudun dafawa.

---

Karfe sha biyu ya isa zaria, kai tsaye gidan shi na staff ya wuce, yana shiga wanka yayi Sannan ya kwanta.

Bai tashi ba, sai da kiran sallarsa asuba ya tadda shi, ban daki ya shiga yayi brush, sannan ya dawo ya bude Bible, ya fara addu'o'in, har karfe shida, wanka ya shiga. A hankali yake jin wata Irin nutsuwa, tana shigar shi.

Yana gamawa yazo ya shirya cikin normal haf jamfa, sai wando brown kaftani, ya gyara gashin kan shi ya kwanta, kallon fuskarshi yayi sannan ya dauki kayan shi.
Yana fitowa kitchen ya shiga ya soya kwai da ruwan tea, ya had'a sannan ya, fito a nutse yake ci wani irin dad'i yake ji. Musamman idan ya tuna babu abinda Aahil ya isa yayiwa Manga.

Yana gamawa ya tattara kayan sannan ya wuce ban daki ya kuma brush, sannan ya fita.
A hankali yake jan motar shi, yana juya abinda ya faru tsakanin mu.

Murmushi yayi sannan yace.
"Cried lady!"
Murmushi ya kuma saukewa yana zare ido shima yace.
"Haka ta fida golder eyes dinta. Sai cutie lip's dinta, Nan dark brown. Short strawberry noise dinta nan!"

Shi ɗaya sai dariya yake yana fada yana dariya.
"Kayi hakuri kaci wani abu sabida kai bakona ne! Addininmu tana girmama bako! Wowwww! Ga mace nan Devanah! Wacce tasan kanta."

Haka yayita surutu shi daya har ya isa makarantar, yana parking Aahil Yana shigowa.

Kusan a tare suka fito, sannan suka rungume juna. Suna gaisawa.

Kowa wucewa yayi inda yake da zama.

Karfe ɗaya sai ga Devanah, a fujajan, ganin shi yasata zuɓewa akan kujerar dake kallon shi tace.
"Bature! Mafarki nayi wai ka You Fall in Love! Da wata musulim lady, shine nazo gani ko dagaske ce! Ashe mafarki nayi."

"Hatred is as blind as love!" Kura mishi Ido tayi kamar zata saka kuka tace.
"But! Ni da kai we are in love! Kuma bana jin tsanar, sai dai A Danger Foreseen Is Half Avoided"

"If you are prepared to face a problem or difficulty, it will be easier to deal with. Devanah ni na gaya miki a gaban kowa Ni bana sonki, ni babu so a zuciyata, Please ki bar min Office. Kuma kiyi hakuri ga ring din Engaged dinmu"

Mika mata yayi sannan ya tattara kayan shi, ya fita zai bar Ofishin sa.

"Bature! A bada excuse is better than none!"

Bai juyo ba, yace mata.

"Am always give you my excuse, even if it's a poor one! Please zoki fita!"

"Because God bless you with many miracles!  Ba komai amma i promised you babu wata macen da zata zauna da kai mark my words!"

Tana gama fad'ar haka tazo ta tsaya a gaban shi zata wuce, tace.
"You! Ka cutar da son da nake maka! Allah sai kayi danasanin Betrayed dina da kuka yi, bazan tab'a barin ka kayi farin ciki ba, sai na zame maka fitina a rayuwar ka, muna nan da kai."

Goge kwallar dake sauka daga idanunta tayi, sannan tace..
"We shall see how you with get successful in your life"

Da kuka ta bar A.B.U tana me alkawarin sai ta rama abinda yayi mata, a can bakin get Suka haɗu da Aahil ya bata hakuri kamar shine Baturen da ya lalata mata rai.

Yayi mata alkawarin zai mishi magana.

....

Tunda  ya rage saura kwanaki sha biyu na koma Zaria nake hada kayana, sai dai da na duba sai naga duk sun sha ruwa, dan a salla munyi kala hudu, kowannen.

Duk da ban san kowa a bauchi ba, Amma nayi kasadar. Shiryawa nazo na sayi kayan irinsu material, kananun atamfofi, sai na kai wunti, dan akwai wata da ta kaini shagon telanta da na gaya mata ni bakuwa ca.

Aikuwa ya amshi kayan, ya bani kwananki da zan koma.

Sai takalma da bags da kuma veil da wasu abubuwan na amfani na. Nayi wasa da kudi sosai. Sannan na dawo gida.

Anan kuma, cincin da dambun nama, tayiwa Dr sai soyayyar zabuwa da Baba yasa aka mishi.

......

A can Zaria kuwa Dr Imran Shaikh Abdul, suketa shige da ficce domin a bude min file dina, da wasu abubuwana.

Duk da hannun Dr ake kome amma yaki shiga dan baya so, Aahil ya fahimci abinda yake aikatawa.

Yau jumma'a, suna zaune a baranda, dukkansu Malaman nan suke tattaunawa, suna cikin haka sai ga Aahil ya iso, zama yayi suka gaisa dukkan su.
Sannan ya kalli Dr Bature cikin murmushi yace.
"BYC! Ko zaka rakani ne bauchi."
"Bauchi!!!" Duk yan gurin suka hada baƙi. Cikin izza yace.
"Eh! Wani abu ne?!"
"A'a! Allah ya dawo da kai lafiya.". Suka ce mishi.
Kallon Dr yayi sannan yace.
"Baka ce kome ba!"
"No friend! Gobe zan shiga Abuja" ya faɗa a hankali.

"Ok bazaka rakani ba?!"
Kauda kai yayi cikin murmushi yace.
"Kusan haka!"
"Toh karka je, gurin Yarinyar nan zanje"
Murmushin mugunta da takaici Dr yayi yace..
"Kace ina gaida ita! Kace Aljuhun baya yana kewar tsiwarta"

Dake bai kira sunanta ba, babu wanda ya kawo Husnah ce.
D'aga kafada yayi sannan yace.
"Oho zan gaya maka kasan ta tsane ka, but idan muka shirya zan tuna mata kai. Yau ina jin ƙishirwanta ne."
.
Girgiza kai Dr yayi bai ce mishi kome bai, sai sunkuyar da kan shi da yayi, kwana biyu nan yana wasa da zuwa service, dan shi kanshi bai san dalilin shi naki zuwa Church ba, ya danganta haka da, aikin da yasha kanshi. Mabiyan shi sai kiran shi suke ya dawo.

Bayan lafiyanta shi kau.
"HUSNAH!" Itace damuwar shi, domin kuwa bazai yi su cigaba da mu'amala yana Kirista tana musulma mebin tafarkin ta ba, abinda zai yi tana dawowa, zai yakince damuwarta ya zuba a kwando shara, sannan ya mai da goben shi da addinin shi sama da kome, dan idan yana bibiyar ta zuciyarshi zata iya sanya shi sabon Yesu.

Wannan itace dogon nazarin da yake kwana da ita yake tashi.

......

Washi gari...
Asabar cikin shigar Alfarmar Aahil ya taso motar shi, sai bauchi.

Ya iso da tambaya, sai dai tun kafin ya iso cikin garin mu, Manga da Abokan shi suka mishi rashin mutunci, na fitar hankali, kamar zasu kona shi da ranshi,

Labari yazo mana cewa su Manga sun hana wani mutum zuwa garin nan,

Allah sarki haka Aahil ya koma,(☹️🤔 Karka damu wannan sharrin wancan kafirin ne zamu jone)

......

Ranar da zan tafi makarantar, Baba ya turani cikin gida, abin dariya. Sai gashi har da cewa.
"Muna jiran tukwaicin boko"
Inji Matar Baba Yawale, sai kuwa suka saka dariya.

Dariya nayi musu sannan nace.
"Allah ya tayani tsare kimata"
Wannan maganar ta sanya su shiru har na fita suna zaune sake da bakinsu.

Har mararaba suka rakoni, abin mamaki sai ga Dr, zuba kayan yayi. Muka koma cikin gari.
Ya gaida baba, da yan uwansa. Sannan yayi musu wankan hannun cikin aljuhun.

Sosai ya kashe bakin mutane, sannan ya dawo dani gaban baba suka min fada sosai.
Sannan Baba ƴace.
"Malam ga Amanar ta nan!"
"Nayi maka alqawarin da ruhin Yesu me tsarki zata dawo cikin amincin sa."

"Ni kuma na baka amanarta cikin amincin Allah"

Sosai iyayena suka yarda da Dr, sannan da zai tafi yace.
"Mubarak! Zaman gida bafa na maza bane! Ka bani takardarka mu nima maka aiki da SS."

Shafa kai Mubarak yayi sannan yace.
"Da ina son na cika federal Poly ne na nan Bauchi shekara biyu."

"Toh duk yadda kuka yi kayi min magana,, ina tare da kai"

Haka ya gama zai tafi ya kalle Abdul sannan yace.
"Malam Abdul! Kaki makaranta, zan dawo next week ka shirya Military school Jos!"

"Meemah kema Addarmu Zaki biyo ko school of nursing Zaki"

Tsalle tayi sannan tace.
"Yaya duk wanda ka zab'a min ina so"

"Toh shikenan! Zan zo Next!"
Ni dai ban ce kome ba, har muka gama, sannan muka yi sallama zamu bar garin, zuwan manga Naga ya fita sunyi magana can ya koma cikin mota ya dauki abu, yana zuwa ya mika mishi, key yace.
"An jima zasu kawo maka, amma kayi ƙoƙarin zama na gari"

Godiya har da ihu
Haka muka bar garin naga yana kallon gurare, tare da gyada kan shi.
Bai ce min kome ba, kaina na kallon tagar motar, ji nayi ya ajiye min abu akan cinyata na juya.
iPhone12 pro ce, ya daura min kwalinta, bai ce min cikanki ba, Nima ban damu na tambaya ba, sai can naji kunya ta kamani nace.
"Na waye?!"
Banza ya bawa ajiyata, sai yanzun na tuna tun da yazo sannu bai hadani dashi ba.

"Kayi hakuri!"
"Me aka min?!"
Juyawa nayi na kalle shi, sannan na mai da kaina titi.
Daga haka bai kuma ce min kome ba.

Bamu tsaya ba gaskiya sai a kaduna, inda ya kaini Sadau beauty aka min gyaran fuskan da zaba min man shafawa, sai kaya da yayita jida min, tare da takalma, kai duk wani abinda zan saka nafito yar yayi ya saya min.

Gurin cin abinci muka je, na kasa ci sai da yayi mana takeaway.

Bamu iso Zariya ba sai karfe uku, ya kawo ni wani state. Sannan ya fito ya fara shiga da kayana, ina bin gidan da kallo.

Muna shiga ciki naga an saka kome, har da kayan kallo karamin friji, duk abinda zan

bukata akwai  a gidan.

"Gobe zaki shigo school, sabida kuna da Class. Akwai Driven da zai zo yana kai ki da dawo dake. Wannan gidan ki zauna har ki gama sauran lokacin da ya rage! Bazan tuna miki kome ba, sai dai kuyi kokarin kare kimarki, batun wancan gayen ki manta dashi, ga kome na bar miki."

Gyad'a kai nayi kawai dan wallahi bazan kyale Aahil ba, yana tafiya na rufe gidan na cigaba dayi kimtsa gidan ina duba abinda zan ci.

Tunda nayi sallah, na kwanta. Ina tashi na tuna da kayan shi da zan bashi.

Ban kira shi ba dan bana son yayi tunanin wani abu.

......
Washi gari..
Karfe tara Driven yazo, doguwar rigar baki na saka wanda yake da ratsin Golder a jiki, na nad'e kaina da gyalen golder, sannan na fito rike da jaka, na fito.
Zama nayi a cikin motar, ina duba waya na lokaci ya tafi.

A hankali muke tafiya, har muka isa makarantar, wata mota ne tayi ƙamar zata buje mu, muka bari ta wuce, parking space muka je, na gama daukar kome na bude motar na fito.
Yayinda shima ya fito cikin motar shi, cikin wata kafiran shadda, ash color, sai gaban shi Dr sanye da Canada suit.

Kamar Ance ya juyo Fuskar shi sai a kaina, bakin shi na rawa yana nuna ni da yatsa yace......

So min tab'i ango ya dafa Amarya 🤩😍

.08130269641.....
.na kudine

Saura page daya na gama free
[7/2, 9:03 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BAHAUSHIYAH□

*Hattara Yan Mata*

Impossible.

Babi-sha-tara

"Husnah HABIB Manga!!!"

Dafe goshinsa yayi tare da juya inda Dr yake yace.
"Ka ga abinda na gani!"

Cikin halin ko ina kula ya rab'a gefen shi Dr yayi ya bar gurin yayinda nima na wuce kamar ban san halin shi ba.

Mamaki ne ya kama shi, kamar wanda aka dasa shi a gurin ya cigaba da tsayuwar, cike da mamaki.
"Husnah HABIB Manga! Anya ba ita bace! Kai itace mana, taya haka, ina bazai yi ba."

Da sassarfa ya shigo cikin department din su, lokacin har nayi abinda ya kawo ni zan fita.

Tsare hanyar yayi cikin murmushin sa, na salon yaudara, yace..
"Kamar HUSNAH ko?!"
Juya idanuna nayi akan shi tare da girgiza kai nace.
"Excuse me!"
Matsa min yayi na fita, cikin ji da kai nake taku, dayawa daliban da suka sanni sai gasu suna ta d'aga min hannu, haɗuwa ta da Aahil ya fama min ciwon shekara daya!
Am just keep smile in my face! Deep inside my heart amma feel bada, domin sai gashi a cikin makarantar ana nuna ni, tare da d'ago al'amarin ya kuma zama trending again.

Koda na shiga aji kowa kallona yake musamman da na kasance yar gaba dasu da aka dawo dani baya.

Wata yarinya ce itama yar kwalisa, na zauna a kusada ita.

Kallona tayi tare da mika min hannu!
"Zahrah Almustapha Chinade"
"Daga Bauchi?!"
Na tambaye ta!
Murmushi tayi sannan tace.
"Eh! Amma mazauna kaduna!"
Murmushi nayi mata sannan nace.
"Asma'uh Muhammad Habib, from Toro, amma kauyen Narabi "
Zaro tayi sannan ta saka dariya, tace.
"Wowwww! Daga state daya muke"
Nan muka gaisa sama sama, muna cikin tattaunawa ne, Mutumin ya shigo, cikin isa da jin shi wani ne!

Fito da jotty dina nayi, sannan na fidda birona.
"Barkan ku dalibai! Sabin zubi da tsofin hannu, toh gamu nan a wani tafiya i hope zaku yi abinda iyayenku suka ka turo, ban da... Ok muyi abinda ya taramu"
.

Yana magana idanun shi na kaina, ban kula shi ba na cigaba da ɗaukar abinda yake mana,

Sai da ya kwashi awa biyu curr tun 10 bai fito ba sai 12, tare da Zahrah muka fito, itama tana murmushi tace.
"Muje mu can mu jira"

Karar wayata ce ta sani duba jaka.
Sako aka turo min, shaf na manta da Dr.
***Ina fatan babu wata matsala***?

Tab'e baki nayi cikin gajiya na tura mishi.
***Fine***! ***Idan ka sami lokaci akwai aikanka a gurina***!
Kashe wayar nayi, sannan muka zauna. Muna hira da Zahra.
Muna d'an hira sama sama! Aka zo daukarta.
"Asmy kizo mu ajiyeki mana!"
murmusa mata nayi sannan na nuna mata driven. Mikewa nayi sannan nace.
"Anzo dauka na, ma"
"Toh sai gobe kenan?!"
"Eh da Yardan Ubangiji!"
Na gaya mata,
Tana shiga motar su nima ina shiga.
Nima shiga nayi, kamar ance ina daga kai sai ga Dr ya zuba hannun shi a cikin aljuhun.

Juyawa yayi abinshi ciki, ajiyar zuciya na sauke, sannan na jingina kaina, ina girmama alamarin Dr Bature, ya zame min rumfar sha shirgi, ya shigo rayuwata a dai dai lokacin da ya dace.
Lumshe idanuna nayi ina girmama rashin kunya da tsana ƙarara da na nuna mishi, yau shine min wani tsanni rayuwata, ban dashi da bazan dawo nan ba, ban dashi da na zama tarihi.

Ban dashi da nayi haukar gayawa iyayena korata akayi, haduwata dashi. Itace abu mafi daraja da na tab'a samu a rayuwata.
Sai dai kash.....
Yarena Addini na ya min iyaka da shi, kasancewar shi bahago daga wata duniya na daban ni kuma ba damiya daga wata dinuya dan haka fatan Alkhairi itace a tsakaninmu.

Ban san mu iso gida ba, dai da Driven yace.
"Madam mun iso!"
Fitowa nayi na shiga cikin gidan. Na bude d'akina na zuba kayana.

---
"BYC! Ina maka magana kana share ni, ko baka ga yarinyar bace"

D'ago kai yayi a fusace, amma bazaka fahimci hakan ba, sabida ya toshe idanun shi da wata sun glass! Shi burin shi tunda ta bar cikin makarantar, ya ishe shi.

"Wacce  yarinya kenan?!" Yayi mishi tambayar renin hankali.

Tsaki yayi  sannan yace.
"Husnah mana!"
"Ai na manta da ita!"
Yarinyar da muka dan yi soyayyar shan minti" ya faɗa a fusace.

"Haba easy! Mutumin! Wallahi na manta ne! Amma yanzun na tunata! Ince kwanaki kaje gurinta?!".

Tsaki yayi sannan yace.
"Ina naje! Ai ina ganin ba yar garin bace! Domin naje wani mahaukaci ya kusan illatani shi yasa ban gaya maka ba."

"Ai sabida kaje cutar da yar mutane ce shi yasa ta kare maka, Wallahi ka daina abinda kake tun kafin lokaci ta kure maka"

Kyalkyalewa yayi da dariya sannan ya ce.

"Allah gafuru rahim ne! Dan halal har yanzun kofafin tuba abude suke ba a rufe su ba."

Baki sake Dr ke kallon Aahil, sabida don zuciya irin tashi ya rufe ido yana kiran Allah gafuru rahim ne, shi yasa baya sha'awan musulinci, idan akwai abinda yake bashi mamaki yadda musulmai ke aikata kuskure su nuna Allah nasu ne, su kadai.

Haka yayi ta hauka a cikin ofishin Dr bai ce mishi kome ba baya daga abinda ya faɗa mishi.

......
Tunda na shiga gida, na zube a falon, cikin Sa'a suka kawo wuta, har barci yayi gaba dani.

Karfe biyu dai² na farka, miƙa nayi sannan na nufi cikin dakin nayi alola, nayi sallah ina idarwa nazo na kwab'a garin dan wake, na fara jefawa. Dake nazo da garin yaji.

Zafi ya dame ni, na shiga daki na cire kayan jikina, zani na daura a kirjina sai dan hular da na saka, na cigaba da aikina.

Ban gama ba sai uku Sara, mangyad'an kuli nazo da ita amma na samu ya kawo min Oky.

Zama nayi na zuba a filet, na koma gefe na yanka albasa, sannan na zauna na fara ci, ina binshi da yaji.

Buga kofar aka yi, na mike ina tura baki dan nasan ba Lallai bane na kuma komawa akan abincin.

Ji nake idan na buɗe ba fallawa wanda ya daga ni a cikin abinci na mari, cikin yar hasala na bude kofar.

Idanun mu ne, suka harde da juna, na wasu dakikai. Nayi maza na janye.

Da sauri na rufe kofar cike da mamaki, tare da wata muguwar kunya, ji nake kamar na bude kasa na shige.

Daki na koma na saka kayana sannan na fito ina sunkuyar da kai na kasa,

Kamar babu abinda ya gani, dan da na buɗe mishi kofar shigowa yayi yana, shakar kamshin mangyad'a, sauke idanun shi yayi a filet din dan wake, janye idanun shi yayi sannan ya cigaba da tsayuwa.

Fito da wayar shi yayi, yana ta danne danne, a raina nace.
Shi kuma haka Allah ya halicce shi bai gajiya da latse latse.

D'ago kai yayi tare da zuba min Ido, sannan ya mai da kan wayar.

Komawa daki nayi na dauki jakata, na ciro wayar sannan na kunnata.

Ina rike da ita, sako ta shigo.
**Karki kuma irin wannan shigar zamanin rashin ilimi akayi**, **pls ki tayani kare amanar sa aka bani**|

Kallon shi nayi, sannan na tura mishi.
***Bazan kuma ba***!
....
Satar kallon juna muka yi, sannan ya turo min.
***Ina sakona***! ***Yau nake son shiga abuja***

Shi kan sa bai san dalilin gaya mata ba, ya dai tsinci kanshi da gaya mata inda zai je.

***ok***!!
Shi ga dakin nayi na dauko mishi aikan shi, sannan nazo gabanshi na ajiye mishi.

Sannan na juya, zuwa inda Abincina yake na zuba mishi, zan saka yaji.
"Kad'an bani ci pepper"

Maggi na fasa mishi, sannan na ajiye mishi dan karamar kular.

"Da fatan babu matsala?!"
"Hmm," nace mishi.

Fita yayi bai kuma juyowa ba.

---
Washi gari....
Zaune yake a tsakiyar manyan Pastors da Bishop Yohana!

"Abraham! Muna jinka, meye Matsalar ka da baka son Aure?!" Inji babban su.
Shiru yayi. Can Baban Devanah yayi magana cikin b'acin rai yace.
"Ba yau ba! Devanah take haukar son shi, but yaron nan ido da ido ya gaya mata baya sonta. Haka ma bai mishi ba, sai da taje inda yake ya wulakantata. Sabida kaf....."

"Ezra! Ka daina aibanta min Yarona! Nasan Abraham mai biyayya ne, kuma zai auri Devanah shi kenan!"

"Doris dole nayi Magana, ban san meye Manufar ku akan shi ba, amma ai dole wata rana ungulu zata koma gidanta na tsamiya, ko kunso ko kunki. Dole ya tsallake line of destiny din shi. Abinda na sani, Y'ata tana son shi, about rayuwar shi kune kuka sani but bazamu iya changing destiny din shi bane, zamu yi iya yi mu."

"Ezra! Domin yarinyar ka shine kake irin wannan maganar! Eyye don't forget ba ayiwa namiji auren dole, idan yace yana. Kuma nace maka zai aureta me yasa kake mana haka ne?"
Sosai tashin hankali ne sosai ya bayyana a cikin Family din dakyar wasu manyan suka dakatar da haka, sannan aka kuma baikon Devanah da Bature zai ayi bikin november.

Sai yamma likis ya dawo, ban ganshi ba tunda bai zo ba, sako ya turo min.

***Da dawo***! ***But bazan sami zuwa ince babu matsala***?!

Ina karatu naji sakon shi, dubawa nayi, sannan na tabe baki nace.
***Barka da hanya***/ ***sannu da gajiya***.

.......
Bai kuma bin takaina ba, sai dai yana cike da damuwa sosai.
.....
Washegari.

Karfe biyu muka shiga ajin, Shi ya shigo mana aji, ya nutsu sosai yana mana bayani, cikin gogewa da kwarewa.

Sab'anin Dr A A har ya gama yan mata ne, a gaban shi.

.......

Shigowa yayi ya kalli Dr yace.
"Friend! Excuse me. Idan kun gama ina son gani HUSNAH."

Dr bai ce mishi kome ba, na kauda kaina fuskata a daure nace.
"Bazan sami zuwa ba!"
Har ya juya zai fita na fadi haka.
Takowa yayi, har gabana ya kura min ido, yace.
"Idan nace ayi abu! Ina nufin ayin ne! Dan haka kizo Office dina kina jina"

Banza nayi da shi, sannan ya fita a fusace, d'ago kai nayi naga yanayin Dr amma fir yaki ya juyo min, sai da ya gama zai fita ne naga fuskar shi babu annuri!

Murmushi nayi nace.
"Kalabi tsakanin rahuna, nake!"

Haka muka tashi, ofishin Aahil naje, ina shiga na same shi yana matse wata yarinya, ban damu ba. Domin nasan halin shi.

"Malam ina da abun yi!"
Kallona yayi, sannan ya sake murmushi, yace
"Am sorry for what i did!"

Juyawa nayi ina niman inda yake magana.
"Dake nake?!"
"Ai na zata da wancan kake? Amma ina nice bayawa! Ai zaman duniya iyawa ce, idan ka iya ka huta."

Murmushi yayi sannan yace.
"Bari na sallami wannan!"
Kallon yarinyar yayi ya nuna mata hanya.

Da sauri ta fita, takowa yayi gaba na, nayi baya kadan ina kallon shi nace.
"Excuse me! Meye haka"

Murmushi yayi a karo na biyu, sannan yace.
"Ina me baki hakuri abinda ya faru, idan da hali ina mu koma kamar da! Kuma ina son ki kaini

gurin Parent dinki, nayi magana dasu."

***Ka fado***? Nace a raina, ina kallon shi.

Shiru nayi ina kallon shi kamar me nazari, kafin na kuma ce mishi.
"Ok! Ka bani nan da sati!"
"Haba Hussy! Kin san yadda nake ji dake! Don Allah kwana ɗaya ma!"

Kallon sakarai nake, ina mamakin yadda yake nuna min sallamar shi a fili.

Mik'ewa nayi zan fita ya taso kamar zai riko ni, na wani saka fuska. Dole ya san yashi fasa kudirin shi, ina fitowa, na hango shi daga bakin kofar ofishin sa.

A raina nace.
***Indan guguwar masifa ta tunkaro babu me iya dakatar da ita. Kuma takan shafi me kan uwa da Wabi***

***Ga masu bukatar sayan book din nan zasu iya biyan ta wannan acc***

Acct: 0472282105
***Ramlat Abdul Rahman Manga***
***GTBNK***.....
200 ***ta bank***
300 ***ta katin mtn domin biyan ta tana ga wannan number zaku turawa***/.+2347035133148👈🏻
***Domin shiga VIP*** 500/ ***ta bank***/600 ***ta katin mtn***....

***Idan zaka sayi Kuma Inuwar Gajimare ne*** 200 ***ta bank idan katin mtn*** 300.......

Nagode 🤝
[7/2, 9:05 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BAHAUSHIYAH□

*Hattara Yan Mata*

*Babi-ashirin*.
Betrayed-Last page..

***Ga masu bukatar sayan book din nan zasu iya biyan ta wannan acc***

Acct: 0472282105
***Ramlat Abdul Rahman Manga***

***GTBNK*****.....**
200 ***ta bank***
300 ***ta katin mtn domin biyan ta tana ga wannan number zaku turawa***/.+2347035133148👈🏻
***Domin shiga VIP*** 500/ ***ta bank***/600 ***ta katin mtn***....
Yan Niger Republic...
Zaku tuntube wannan number ne +227 84 50 64 76👈🏻
***Idan zaka sayi Kuma Inuwar Gajimare ne*** 200 ***ta bank idan katin mtn*** 300.......

Nagode 🤝

Lallai maza basu da kunya, yanzun duk tilin Iskancin da Aahil yayi min har ya iya kwaso jiki yazo mu dinke ƙamar da, hmm.

Ban yi mamaki dan na san za arina.

Dan haka tun da ya shigo rayuwata a karo na biyu ya hadu da masifa.

Ai bayi wasa da Damana ba na shiga bashi ciwon kai ta hanyar ajiye shi na manta dashi, ko yana aji ko baya aji sai ya turo a kirani, ni kuwa naki zuwa koda na fita wata tsabga na nake zuwa.

Kamar da wasa, sai naga Dr ya dauke wuta. Dama yana cikin damuwa, sai dinkewar mu da Aahil ta kara mishi sabon tashin hankali.

Sabida ido da ido na fita hanyar shi, yaje Narabi, kuma suka min aika. Bai kawo min ba ya bawa Driven ya kawo min.

A church ma bawai gane mishi suka yi ba, amma dake suna matukar son service din shi haka suke lallabani.

......
Na nutsu sosai ina barcin gajiya saboda yau Asabar ce, buga min kofa akayi na tashi. Na saka hijab dina,

Buɗe kofar nayi, Aahil na gani tsaye. Yana latsa wayar shi, sanye da Shadda sky blue.

Rike kofar nayi tare da zuba mishi ido, nace.
"Wani abu kake noma?!"

"Please zan iya shiga?!"
Ya tambaye Ni,
Girgiza kai nayi cikin wani irin tsume fuska nace.

"No way, muyi magana a waye"

"Amma ai..."

"Zanje na kwanta fa!"
Na gaya mishi a takaice,
"Ok amma zaki iya rakani, muje mu karya"

"Idan zaka iya jirana nan da sha biyu maybe muje"

Kallon agogon hannun shi yayi, cikin kaguwa yace.
"Amma!"

"Kai jeka babu inda zani!"
Na ja baya na rufe kofar na,

Na koma uwar dakin nayi kwanciyata.
Kamar wanda aka zarewa lakka haka yake bin kofar dakina da ido, ban san lokacin da ya bar gurin ba. Ni dai na cigaba da barcina.

Wani buga kofar ake kamar za a b'alla min, tsaki nayi, sannan na fito ina karamin tsaki. A raina nace.
Mayye yaki tafiya, kallon agogo nake naga karfe sha biyu saura. Sake buga kofar aka yi na fito. Nima cikin masifa na bude zan balbale shi.

Turus nayi ina kallon jar fuskar Dr Bature, cikina ne ya hautsina bakina na rawa nace.
"Dr!"
Sanya hannu yayi ya bude kofar ya shigo, sannan ya tura kofar ya jingina a kai.

"Bazan hanaki yi abinda kike so ba! Sabida ban isa ba. Ni din waye Christian."

Daga yadda yayi maganar ya sani fahimtar yana cikin damuwa.

"Amma zan cigaba da kallon ki, idan na gaji zan gayawa Parent ɗinki su sannan meye faru. And kar na kuma ganin kafar wancan dattin a Estate dina, in ba haka ba zan iya yin komai! Which mean zanyi abinda dukkan mu zamu yi kuka har iya karshen rayuwarmu!"

Har gabana ya iso yana kallon cikin idanuna, dan ji yaƙe Kamar ya min mugun duka ko zai samu sauƙin abinda yake damun shi.

Ni dai ban e kome ba har ya gama zai fita, idanun shi ya sauka akan wayata da nasaka cahji tana kawo wuta.

Zuwa yayi har gaban wayar, ya duba, ranshi ne ya kara ɓaci.

Cire wayar yayi ya mika min.
"Code"
Cirewa nayi na mika mishi, shiga cikin wayar yayi tare da blocking Aahil, sannan ya ajiye min wayar a saman frij.

Ko kallo bai isheni ba, ya bani takaici, yana fita naga har number ya goge, kuma bafa nice na bashi number na ba, tsabar masifa ce, sai da ya nimo ni.

Bayan tafiyar shi. Garin kunun tsamiya na hada tare da soya dankalin turawa.

.....
Yadda kuka san bindi haka Aahil ya koma min, ni kuwa naki kula yin shi. Ina sane da hakan.

Ban san me ya faru ba, sai ga Dr ya shigo aji dan wayancewa yayi sannan ya fita.

A raina nace.
"Kaji da gulmarta"

Bayan wani lokaci sai ga A.A, ya shigo. Kafe ni yayi da ido, har gaba na ya iso.

Zai min magana na mike da sauri na dauki kayana zan fita.

Ya kuwa biyo ni yana min magana.
Karo muka yi da Dr, yayi maza ya dakatar da Aahil.

"Ka rabu da ita! Domin iyayenta karatu suka turota! Kai kuma bata mata suna zaka yi a karo na biyu, pls Aahil ka bar musu yar mutane ta sami sallama."

Ture hannun shi Aahil yayi sannan yace..
"Wallahi bazan iya ba!  Ita ce sai dai ni! Kome nata dai sau nawa ne, idan na kyaleta nayi asara babba, Allah kayi wani abu zan aureta."

Janyo shi yayi suka koma Office d'in Dr.

"Baka da hankali, me zaka cewa VC, akanta sannan kai baka tunanin idan akawa kanwarka ko yar ka zaka ji...."

"BYC! Ina ruwana damu?! Musulmace yar uwata! Ba kada matsala a cikin wannan yanayin, don Allah bana son shiga abinda bai dame ka ba, Husnah kuwa ko tana so ko bata so, sai na kwanta da ita, Kum......"

Ture shi Dr yayi har waje.
"Baka isa ba! Kuma zaka gani, Husnah tafi ƙarfin ka har abada, ita ba irin wawayen mata nan bane tasan me take yi "

Abin mamaki, sai ga rikici ta kunno tsakanin Bature da Aahil abinda ya matuƙar daga hankalin mutane da yawa, domin ta kai har sai da suka gayawa junansu kalmai masu zafi.

Dakyar aka shiga tsakanin su, tare da nima na.

Ina kwance bayan na gama shan garin kwaki, kawai naga sakon Dr.

***Meye tsakaninki da Dr A.A Mai tama***?!

Shiru nayi kafin nayi nazarin abinda zan gaya mishi.

Tura mishi nayi da sakon na yi tsammanin zai iya zuwa ba.
***LOVE***!

Banji dadin haka ba, amma bani da zab'in dole nayi haka, Dr nada Zuciya me kyau, sannan shi ya banbanta da sauran Kiristoci, zai yi wuya ya mara min baya akan aikin gabana.

Ji nayi an daki kofar, dan an murda yaki buɗewa, shine aka daki kofar, tashi nayi na bude kofar, shigowa yayi kamar zai yi kwallo dani.
Tsayawa yayi a gabana ya nuna min kan wayar, jikin shi na rawa yace.
"Gaya min! Ki mai maita min naji da kunne na?!"

Na bude baki zan yi magana Aahil ya shigo.

Komawa gurin Aahil nayi, tare da tsayawa a gefen shi.
Ina murmushi nace.
"Yes muna son Juna! Kuma banga amfanin shigowa rayuwata da kayi ba, karka manta Aahil Musulmi ne! Kuma ko babu dangantaka tsakanin mu, akwai dangantakar musulunci, Pls ka rabu damu, dan na amshi tuban shi kuma nasan nan da wata uku zamu zauna a karkashin inuwa d'aya. Ko Dr Aahil."

Kallon mu yayi bakin shi a sake, jikin shi yayi mugun sanyi, a hankali ya juya zai fita.
"Ina muku fatan Alkhairi!"

Murmushi nayi mishi, sannan ya fita.
B'ata rai nayi sannan na nuna mishi hanya.
"Fitar min a gidana, lokacin da ka wulakantani, a gaban makaranta kayi min haka, matuƙar kana son mu koma da kake ka fada a cikin makarantar a bani hakuri da abinda kayi min."

Kamar zautacce ya fita, da mugun sauri, har yana tuntube.
Rufe kofar nayi tare da zamewa na fashe da wani irin kuka, har jikina na rawa. Innalillahi wa'inna ilaihi rajioun!

Nayi butulci, nayi mishi rashin adalci, ya damu dani nasaka mishi abinda yafi kome muni. Nayi kuka har naji idanuna suna niman yi min ciwo.

Ban tab'a tir da halina irin na yau ba, na wulakanta mutumin da ya damu dani.

......
Allah ka dai ya kai shi gidansa, amma bawai dan yana da nutsuwar tuki ba.

Yana shiga gidan shi ya zube a kan kujeran falon ya dunkule, jikin shi na mugun rawa, ga wata zazzabi da ta rufe shi.

Dakyar ya lallubi wayar shi ya kira likitan shi, cikin yan mintoti sai ga Likitan, ganin yadda ya same shi ya daga mishi hankali.

Da sauri ya kira motar asibitin shi, aka zo suka tafi dashi.

Suna isa aka shiga sanya mishi ruwa da isar zukar numfashi, cikin damuwa suke aikin domin jikin shi birkicewa take.
Kiran Bishop likitan yayi ya faɗa mishi halin da dan shi yake ciki.
.......
Bayan awa biyu suka shigo asibiti har zuwa lokacin, suna fama da numfashin sa.

Mommah kuka Devanah kuka, sam Daniel da Bishop ne basu cikin tashin hankali, suna cika awa daya da zuwan su. Numfashinsa ya tsaya. Jona mishi na wata computer, sannan suka turo shi zuwa cikin dakin da za a barshi.

Kallon su Mommah Likitan yayi sannan yace..
"Ki biyo ni!"
Abin tausayi yana ce musu, su biyo shi suka bi bayan shi kamar zasu kifa.

Zama yayi sannan ya fara, rubuce rubuce, sannan ya kalle su. Yace.
"Taya kuka bari damuwa tayi mishi yawa?! Gashi nan yau kamar akwai abinda ya gani ko yaji wanda ya firgita shi, gaskiya zuciyarshi tana cikin kokonto, matukar aka cigaba da tafiya zata buga! Kun fi kowa sanin ciwon bawai ta bar zuciyarshi bane baki daya, tana tare dashi, karfin Soyayyarku itace, samun lafiyar shi.

Indai bai rage damuwa ba, toh sai dai a kaishi India su mishi aikin zuciyar, ko da wani ƙarfe su saka mishi, domin ko wani irin yanayi zuciyar zata kumbura.

Ni a tunana tun muna can Rome ciwon ya laffa ashe tana nan. Toh ku tambaye shi meke samun shi.".

"Ba komai bane, sai takura mishi da muka yi ya auri Devanah. Ni dai don Allah ku taimaka min Yarona ya tashi."

Surutun da Mommah tayi ba iyaka dan gani take auren Devanah da aka kakkaba mishi itace solar fad'awarshi matsalar.

Haka suka wuni a cikin asibitin suna addu'a. Kwana suka yi a kanshi, suna addu'a.

.....

Nima haka na kwana cikin tashin hankali da damuwa. Da safe muna da ajin shi karfe biyu. Koda na shiga makarantar sai na samu wai ashe bai da lafiya, ba zai samu shigowa ba.

Ban tab'a shiga mafi girman tashin hankali ba irin na yau, dan ji nake kamar zuciyata zata buga. Da sauri na juya zan fita.

Wannan dan wahalar ya tare ni, wai nazo muje hutawa.
Murmushin bakin ciki nayi mishi na kalli agogona nace.
"Bazan je ba! Ko akwai matsala?"

Ina gama faɗar haka nayi wuccewa na, tare da barin shi a gurin.

Bai fasa ba dan har gida ya biyo ni,

Zan shiga cikin gidan yayi wuf ya fito yana magana.
"Haba Hussy! Don haka ai kece kika ce we are in love;"

"Oho! Really! Toh na fasa!" Na gaya mishi tare da wucewa na,
"Please Please! Hussy don Allah karki yi min haka! Wllhy am fall in love, with you"

"Are You sure?" Nayi mishi tambayar renin hankali,
"Am seriously"
Ƙamar zai fashe da kuka,
"Hmm! Zan yi tunani akan haƙa, excuse me!"

Ƙamar ya saka hannu a kanshi yayita zuba ihu,

Ina shiga, ban san hawaye na zuba min ba sai da na shiga ban daki naga ashe kwalla ne yake jike a fuskana, dan ina shigo wa sai da na jingina da bango tare da rintsa idanuna, kuka na sake me mugun cin rai. Meye matsalata,.meye na aikata mishi.

Innalillahi wa'inna ilaihi rajioun! Dan bamu Yarena Addini daya me yasa nayi amfani dashi dan na kusanci Aahil.

Innalillahi wa'inna ilaihi rajioun! Tun ban yi nisa ba, kome ya wargaje min. Me yasa bani da sa'a....

Haka nayita kuka ina watsar da kayan wakana.

......
Karfe takwas na safe, ya buɗe idanun shi. Ganin familyn shi tare da Devanah, sai tausayinta ya kama shi for the first time, yaji irin yadda take ji. A gaya maka ba ayinka. Ashe haka Devanah take ji a lokacin da yake gaya mata magana cikin harsh's tongue, Mika mata hannu tayi ta kalli bayanta taga itace yake dai kira.

Da sauri ta isa gare shi, rike hannunta.
"Am sorry!"
Kifa kanta tayi a gefen hannunshi ta fashe da kuka,

Murmushi me ciwo ya sake, yana kara godiya ga Yesu da ba son Husnah yake ba, kawai yana jin ba dad'i ne sabida shi ya daukota. Daga gaban iyayenta.

A haka suka sanya shi a gaba da tambayar meke damun, murmushi yayi kawai domin bayi da amsa, idan ma ya faɗa tabbas sai kowa yayi mishi tofin Allah tsine. Kuma shima abin kunya ce yana Pastor guda, me jagorantar church guda, dan haka yayi shiru yana biye musu suna mishi magana zai ce ALLAH ne ya daura mishi.

.....
Lokacin da me kaini makaranta yazo, har nace mishi bazani ba, sai na tambaye shi wani asibiti yake.
Cewa yayi na shiga ya kaini, banyi kasa a gwiwa ba, na bishi...

Kash...... Alkalamina na free ya kare! Nayi nayi ya tashi ya tsaya...

Bishop!
Mommah!
Devanah!
Tohfa.... Me zai faru 😲

Aahil..... Is fall in love with Husnah! Or fall in betrayed.

Narabi....
Baba Yawale... Etc...

Yoland.....
Imam Moddibo
Muhmood Dan Kasa
......

🤔🤔🤔 Chakwakiyya na nan fa....
[7/2, 9:05 PM] BAHAUSHIYAH🥰: Babi-As-biu

Zahrah M Chinade 🌺

Zazzaɓin da ya dame ni ya sani tashi dole, na rarrafe zuwa ban daki. Alola nayi sannan na fito, a zaune nayi sallah. Sannan na kwanta a gurin wani sabon zazzafar zazzabi yace min bismillah.

Na gigice, bana fahimtar kome. Dole na tashi na shiga niman wayata, dakyar na samu. Sannan na shiga Nima kowacce layi domin bani gani sosai.

A tunani na shi nakira, ashe number Zahrah ce.
Tana dauka na fara cewa.
"Idan na mutu! Karka ga nayi gaggawar tafiya, pls say something. Dr kayi min magana na gaji da shir.."

Daga hakan ban kuma fahimtar kome ba, sai bayan wasu awowi na buɗe idanuna naga karin ruwa. Ina duba gefena na ganshi zaune yana rike da wata yar karamar Bible.

Tashi na fara kokarin yin, ya zuba min rikitattun idanun shi, tab'e baki yayi sannan yace.
"Welcome back! Daga duniyar matattu"

Ji nayi Kamar ya watsa min ruwan sanyi, idanuna ne suka cika da kwalla. Na juya mishi baya.
Bai ce min kome ba, illa fita da yayi, can sai gashi da likitan. Yana zuwa ya cire min ruwan sannan yace.
"A bata abinci koda tea ne"
"Ok!"
Daga haka likitan ya fita, shi kuma ya koma gaban dan drowe ya fara zuba min tea, sannan ya bude jikata ya ciro maclean, da brush. Ya bani,

Zan sauka ya kalle ni, komawa nayi na zauna, shi kuma ya shiga ban daki ya dauko. Min wani silver bowl ya samin a gabana.

A hankali na fara wanke baƙin, ina gamawa ya mika min ruwa na dauraye bakina, kaiwa yai ya zubda sannan ya dawo.

Ya mika min tea, kai Dr Bature halin shi sai shi, har yanzun shiru. Sai wani karatun da ba fahimta yake ba, rike tea din nayi ina matsar kwalla.

Can na fara jan hanci, kallona yayi tare da zaro ido cike da mamaki.
Kallon tambaya yayi min, aikuwa kamar jira nake, na bare baki zan saka mishi kuka yace.
"Wait! Me aka miki kuma, ke idanunki basu gajiya da kuka ne"

Dama ba kukan zanyi ba, dan kuma na gaji da kuka sai kace baure, tura baki nayi, sannan nace.
"A maidani gurin su Innarmu da Babanmu! Dan nasan da sune da sunan nan suna jigila dani, bawai a sani a gaba ana karatun Bible ba"
Kura min ido yayi, sannan ya bude baki zai magana sai kuma yayi shiru.
Ya cigaba da kallona. Ina rike da tea.
"Kisha dan akwai yunwa a jikinki"
Kallon tea nayi, sannan nayi rau-rau da idanuna ina niman kwallar fitina.
"Toh kuma meye?!"

Ya kuma tambaya na a dame, tura baki na kuma sannan nace.
"Wancan ranar da nazo wacece wannan da ka daura kanka a kafad'arta?"

Gyara zama yayi inda ya daura daya akan daya.
"Matar da zan aura ce! Devanah Ezra Chibok!"

Rike cup din nayi ina kallon, tea din.
"Allah ya tabbatar da Alkhairi!" A sanyayye nayi maganar, sai yaji ba dad'i.

A hankali yace .
"Amen!"

A hankali nake kurb'an shayin bawai dan dad'i ba, sai dan bani da zab'i, gefe guda ina sauke ajiyar zuciya.

Ina idarwa na sauka a gadone, kallon kayan jiki na nayi ina kuma kallon shi.
Murmushi yayi, sannan yace.
"Don't criticism, kawar ki ta kirani da wayar ki, kin kirata kina ce mata Dr zaki mutu ba"

Bata rai nayi cikin jin haushi, nace.
"Ni yaushe nace zan mutu!? Zata gamu dani, Wllhy idan sharri junarta ne dani take maganar"

Shikam dariya na bashi, amma amadadin yayi sai ya wayance da murmushi.
Yana zaune na fito daga alola nace.
"Waye kuma ya dauko ni? Lokacin da."

"Duk kina da su, Amsar da question din!"

"Ni wallahi mutum kar ya kuma dauka na."

Na fada a rikice, d'aga kafada yayi sannan yace.
"Ok! Na manta ne da nakira Boyfriend dinki maybe next time zai iya daukar ki"

Shiru nayi, ban kuma magana ba, dan nasan yab'a min magana yayi Allah na tuba, meye zanyi da Aahil kuma"

Sallah asr da magirbi sai Isha nayi su, sannan nayi addu'o'in, tashi nayi na zauna, can likitan ya shigo, kallona yayi sannan ya mikawa Dr hannu, yana gama duba ni yace.
"Dama damuwa ce, zaku iya tafiya."

Kallon shi nayi, ya kalle ni a sace sannan ya mike ya dauki flast ya fita, kallona likitan yayi sannan yace.
"Yan mata! Ke Bahaushiyah ce ko!?"
Gyad'a mishi kai nayi, gyara tsayuwar shi yayi, sannan yace.

"Ina me baki shawara! Ki fita a rayuwar shi! Domin muna muna bukatar shi a rayuwar mu! Pastor din mu ne! Don Allah kiyi nesa dashi, shekaru ashirin ina lura da shi, ban tab'a ganin rikicewar shi ba, sai da ya kawo ki? Muna son shi a cikin addinmu! Kuma bazamu laminci a maida mana shi wata addini ba, idan baki ji ba! Kiyi kuka da kanki"

Zama nayi a bakin gadon, tare da sunkuyar da kaina, jikina yayi sanyi.

Har ya shigo muka fita tare sai lokacin na lura da yadda ake girmama shi tare da niman albarkan shi.
Koda muka fito shi ya buɗe min motar, wanda ya amshi kayan hannun shi ya buɗe mushi.

A hankali ya shiga ya fara jan motar.
Bai min magana ba, nima ban Mishi ba har muka isa gidana.

Yana isa nayi wuf na ficce, sannan na shiga  dibi dibi, dole shi yazo ya bude kofar tare da ajiye min kayana, bayan fitar shi can sai gashi da magani, mika min yayi sannan ya kalle ni.

"Drama queen" ya faɗa a ran shi, sannan ya min sai da safe, rufe kofar nayi tare da saka Kaina a cinyoyina, ina nazarin maganar mutumin nan.

Ina zaune a gurin har sha biyu da rabi, tashi nayi tare da alola na fara nafilla. Na jima ina kai kuka na gurin Ubangiji, Ban kwanta ba sai daya saura.

Ina kwanciya barci yana gaba dani, wajen karfe biyu naji ana buga min kofar dakina, kuma ina jin kaman muryan Driven da yake kaini makaranta da likitan nan ne!

Shafo wayata nayi na shiga niman layin shi, banyi mamakin jin shi a bude ba.

"Hello! Hussy!"
"Wasu ne suke buga kofar dakina?!"

"Jesus! Don't go out! Kiyi zamanki gani nan zuwa!"

Yace min, kashe kiran yayi.
Ni kuwa na takure a gadon jikina Yana rawa,
(Karku manta Wannan book din na kudine)

Sai buga kofar suke, tare da kiran sunana, curewa cikina yayi tare da rawan sanyi. Ga wani shegen fitsari da ya kamani.

Muryan shi naji, ban san me yake fada ba, amma tabbas magana yake cikin b'acin rai.

Sosai yake musu Bala'i. Hakuri suka shiga bashi.

Buga min kofa

Na diro daga gadon, na fito.

Shigowa yayi yana kallona, kunna wutar dakin yayi, yana had'iye yawu me daci, sannan ya juya yace.
"Daga yau! Karki na zuwa wani waje, sai da permission dina, koda school ne, dole sai kin jirani in ba haka ba, don't blame!"

Gyad'a mishi kai nayi, sannan ya fita, rufe Kofar nayi. Duk tsoro ya dabaibaye ni.

Daga nan church din su ya wuce, anan akayi ta Bala'i har gari ya waye.

Sun kafe yana soyayya ne dani, shi kuma ya kafe akan babu komai, mutuncine a tsakanin mu. Daga karshe suka mishi iyaka dani, ta hanyar fada mishi kai tsaye zasu kashe ni.

Kura musu ido wani babba a cikin su yayi sannan ya girgiza kai yace.
"Ba laifi bane! Yayi soyayya da hausa lady, babban Matsalar kuma tab'a yarinyar abin zai zama fadar Addininmu da nasu, Ni shawara da zan baku shi ne, ku zuba mishi ido, karku kai Maganar ga iyayen shi, sannan kai kuma ka fita hanyar ta, idan kuma kaki babu ruwana. Kana da daraja a church din nan dan haka ka kiyayye abinda zai kai da yadda husuma."

Nan dai aka rabu cikin salama, damuwa ta kuma karuwa, domin yasan suna bibiyar al'amarin shi, sai ya fita harkata baki daya.

Ko zuwa nayi Office din shi a rufe yake, idan na buga nace nice zai ce baya son ganina.

Gefe guda, ga manniru! Wato Aahil dan banza ya takurani, sosai fiye da kima ina dalili.

Naje Office din Dr yaki barina na ganshi, mara mutuncin nan ya tare ni sai jin hannun shi nayi ya riko nawa, yana fadin.

"Attention every body! Ina son kushedai ni da Husnah mun shir..."
Bai karasa ba na juya na falla mishi mari, na kuma kara mishi. Dama ina cike da Dr ne sai laifin ya koma kanshi.

Sannan ya wuce shi, abin ya bawa kowa mamaki amma bani da zab'i.

Cike da kunya tare da bakin ciki ya bar makarantar, ni kuwa naje na hau bus ya maidani gida.

Na turawa Dr sako, bai dawo min ba. Dan haka na shiga damuwa sosai.

Kai tsaye na wuce Gidan su Zahrah.
Duk yadda naso rike kuka na na kasa, kawai zama nayi na fara kuka sosai. Domin a gidan Yayarta take zama.

Dariya na bata, sannan tace min.
"Waye kuma?!" Ta tambaye ni.
Fyace hancina nayi, sannan na cigaba da kuka kafin nace.
"Dr mana! Baya daukar kirana! Baya reply text dina, Idan naje Office din shi baya barina na shiga korata yake. Nayi Deserve abin da yake min"

"Me yasa ke baki san Uzuri bane?! Ke kin san meke damun shi ne?! Ko kawai abinda yayi miki ne damuwarki!"
Tashi tayi ta kawo min ruwa, sannan tace.
"Duk inda yake yana dame da rashin ki! But Dr yana yinki ove, koda ace yau bai sonki, yana matukar ji dake, balle ni naga abubuwa da yawa akanku, ba iya hakan ba, kome ma."
Kara wayar ta tayi, tace.

"Gata nan!"
Mika min waya tayi ina Kallon ta, sanyawa nayi a kunne na, nace.
"Hmmm!"
"Drama queen! Yau ba kuka ne?!"

Ban san me zance ba, sai na yi shiru! Can yace min.
"Me yasa baki gaya min zaki zo ba"

Yadda yayi maganar sai da jikina ya amsa, a hankali na bi pillow na kwanta akai.

"Bayan kana korata a Office dinka!" Na fada mishi muryana na rawa.

"Eh sabida na kusan aure ne nake miki haka bana son matana ta ganki"
Ya fada min a sanyayye.
Tab'e baki nayi sannan nace.
"Hmm! Ai sauya cinye ka"
Wata yar dariya yayi sannan yace.
"Kin tabbatar ta cinye ni, dukka"
"Idan ita mayya ce ba!"

Shiru yayi sannan yace.
"Baki ganta bane baturiya ce fa"
Cikin jin haushi nace.
"Ok! Ina bolar bakakke! Malam fari tass tass"
Dariya yayi sannan yace.
"Lallai baki taba ganin Devanah bqce"
"Itace matsalar ka?! Domin zan kashe wayar!"

"Toh kashe mana! Bayan gulmata kika zo"

Shiru nayi can nace.
"Kai ina akan me zanyi gulmar ka! Kaga mijin baturiya sai anjima!"

"Toh kashe mana!"
Yadda yayi maganar, ne ya kashe min, jiki.

Gabaki d'aya sai na rasa yadda zan kashe, sai na cigaba da sauraron shi.

A hankali barci yayi gaba dani, me cike da ban tsoro, dake la'asar tayi, shi yasa nake wannan shirmen, buɗe idanu nayi. Sakamakon wani ihun da anji, ana cewa a mafarkin baki isa ba.

Tashi zaune nayi ina kallon, addu'o'in nayi sannan na tashi ina me son tuna meye ya faru.....

***Ga masu bukatar sayan book din nan zasu iya biyan ta wannan acc***

Acct: 0472282105

***Ramlat Abdul Rahman Manga***
***GTBNK*****.....**
200 ***ta bank***
300 ***ta katin mtn domin biyan ta tana ga wannan number zaku turawa***/.+2347035133148👈🏻
***Domin shiga VIP*** 500/ ***ta bank***/600 ***ta katin mtn***....
Yan Niger Republic...
Zaku tuntube wannan number ne +227 84 50 64 76👈🏻
***Idan zaka sayi Kuma Inuwar Gajimare ne*** 200 ***ta bank idan katin mtn*** 300.......
[7/2, 9:05 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BHSY23

Sauka nayi a gadon, tare da shiga ban daki nayi alola, sannan na fito na tadda sallah, koda na idar abinda nafi maida hankali akai itace Du'a', nayi sosai har Zahrah ta shigo.

Abinci ta ajiye min nayi murmushi, sannan nace mata.
"Rabona da Abinci na manta ranar"

"Saboda kin sanya damuwa a ranki! Kin manta akwai Allah. Ni dai ki nutsu muyi maganar gaskiya."

Gyara zama nayi muna cin abinci.
"Hussy!  Kina son Dr ne?!" A rud'e na kalleta,
Girgiza mata kai nayi, sannan nace.
"Kawai Abokina ne! Kum...."

"Na zata mahaifarku daya ne?!  Dalla tafi can kome sai kin saka shirmen yan fari. Kina son Dr ko baki son shi?!"

Girgiza mata kai nayi kirjina yana bugawa, da karfi.
Tsame hannuna nayi daga abincin. Na koma gefe..
Na rasa me nake ji akan shi amma presently ina ji kamar idan bashi ba, toh bazan iya damuwa da wani ba.

Shiru nayi mata duk yadda taso muyi maganar Mali bata fuskar.

Dan haka har muka rabu, ina ta tunanin abinda tace min.

---
Tsakani da Allah! Dr ya yakince ni, daga jikinki shi wanda hakan ba karamin tashin hankali na shiga.
Yana da mugun dabara, sai da ya cire baki d'aya. Har na fara tunanin ko dama ba sona yake ba, toh ai bai gaya min ba.

Lokacin muna dabda tafiya hutun mu na farko.

Ina zaune nayi shiru, ban san zuwan shi ba, sai ce min yayi.
"Gani nan tunanin me kike yi?!"
Kallon shi nayi sannan, na mike.
Rike jakata yayi sannan yace min.
"Zauna! Muyi wata magana!"
Komawa nayi na zauna ina nazarin abinda zai fada Min.

"Kina fushi da nine?!" Ya tambaye ni a sanyayye,
. "Dr zan tafi gida!" Ta gaya mishi a takaice,

"Ok! Toh jeki tunda bazaki saurari abinda zance." Shiru ne ya gifta a tsakanin mu. Can na tsinkayo muryan shi yana cewa.
"Dalilin!"
Sai kuma yayi shiru kafin yace.
"Tashi ki tafi gida, yamma nayi"

Ya fadi haka ne sakamakon hango Aahil da yayi wanda tunda na na kafta mishi mari, ya kwaikwaice min.

Kuma dake mayye ne, bina yake ina wulakantashi. Amma bai fasa ba.

Ina barin gurin, Aahil na isa.
"Wato dan abu kazan kazan ka, shine ka rabani da yarinyar da nake so. Munafuki anamimi."

Banza dashi Dr yayi, dan a yanzun bai cika damuwa da haukar shi ba.
Ganin zai wuce shine yaki magana ya sanya ya finciko rigar Dr.

Tare da zabga mishi naushi a gefen idanun shi, Allah ya so da ya tab'a mishi ido, tabbas Dr yaji ciwon abinda Aahil yayi mishi, amma dake ya iya siyasa konace dabi'ar Christian yabi jikin shi sai yaki ramawa, karshe sai ga wasu dalibai musulimai sune suka shiga mishi fadar.

Ba a bawa arne Amana, amma ni nasan Dr ba gama garin arnan nan bane, Ban san yadda zan muku bayani kan fahimta ba, domin zaku iya tunanin, ina cikin barasar soyayya ce.

Abubuwan da idan kaga Dr dashi zai sanya ka kaunace shi sun hada.
Sanin Yakamata, nutsuwa, Dattaku, sanin darajar duk wanda yake kusada shi, sai iya magana, dan shi idan ya fahimci zai gaya maka magana me zafi ya gwammace yayita kallonka.

Dan haka duk yadda Aahil yaso suyi magana, yaki tanka mishi.

Washi gari.
Ina shiga makarantar sai nuna ni ake duk inda na shiga, har aji. Nan na zubawa Zahrah ido ina

son sanin me ke faruwa.

Murmushi tayi, lokacin da da malamin farko ya shigo, har ya gama zai fita ya kalle ni.

"Husnah! Ki same ni a Office d'in VC." Yadda yayi maganar sai da cikina ya kad'a.

Kallon Zahrah nayi, rike hannuna tayi cikin kwarin gwiwa tace.
"Bana son kina tsorata ko razana".
Haka na fita zuciyata tana wani irin bugawa, ajiyar zuciya nayi sakamakon hango shi yana shigowa makarantar.

Kasa tafiya nayi na jingina, ina jiran shi.

Yana zuwa bai kula ni ba ya wuce.
"Ni! Wallahi idan za a cigaba da min shiru toh Allah zan yi kuka"
"Allah ya baki Sa'a! Tunda kukan abin alfahari ne ba"

Sam ban kula da fuskar shi ba, yadda yayi maganar, yasani jan hancina.
Cak ya tsaya tare da juyawa ya kalle ni.

"Meye nufinki!"
Wasa nake da yatsuna wanda na sanya musu lalle, "sunyi kyau. Yar fara tass tass." Ya fada tare da juya abin shi.

Rike habbana nayi ina nazarin abinda yace har yayi min nisa, na kara sauri da sarssarfa na isa gare shi. Ina haki,
"Me yasa kike wahalar da kanki?! Ji gudun da kika yi kowa na kallonki, baki san idan kin.."
Shiru yayi kamar ruwa ya cinye shi, juyawa nayi naga matar nan ce dana ganta dashi.
A hankali na koma bayan shi na tsaya tare da rike rigar shi.
Dan ta bani tsoro, tawowa tayi da sauri ta fad'a jikin shi. Kauda kai yayi tare da nuna min hanya.
Kamar wacce aka dasa, na kasa motsi, kallon su nake.
Tsabar tashin hankali, tap din bayanta yayi tare da rarrashinta dan kuka take har ina jin sautin kukan, a hankali na zame zan bar gurin ya rike hannuna yana me girgiza min kai, cire hannuna nayi. Cikin sauri na bar gurin.

Sai da nayi tafiya kadan na tsaya tare da sauke wasu irin kwalla masu zafi. Sabida naji zafin rungume shi.

Share fuskana nayi, na wuce har Office d'in shugaban makarantar, ina zuwa na sami malamai.

Kafin Dr ya shigo, suka hadu dukkan su, suka zage Ni tass tare da nuna min Kuskurena na

soyayya da Dr, Ni dai na kasa magana domin kuwa kuka nake, suka kuma nuna min, irin abinda Dr yasa aka yiwa Aahil.

Sun ci mutumcina fiye da kima, sun zage ni, na fitar hankali.

Wallahi tsabar kuka ina tsaye sai da na durkusa, kuma karku yi tunanin kome, dukkan sun Hausawa ne, matsalar Aahil ya saye su, koda Dr ya shigo ya manta inda muke gani na a durkushe ina kuka, yasa shi zuwa ya daga ni tare da tambaya ta, hakika ni abinda ya faru.

Kasa magana nayi ina kuka, domin ban san me zance mishi ba.

Jan kujera yayi sannan yace.
"Husnah jeki"

"Bamu sallameta ba! Domin zamu bata hut..."
Dukar table din Yayi da mugun karfi, ya kafe VC da ido yace.
"Kalle ni nan! Meye laifinta? Meye Yarinyar ta tsare muku?! Kusan karfin tsayawa ta a nan? Toh ai sabida itane, bani son Magana shi yasa har yau nake shiru. Badan ban iya maganar bane sai dan ni nabarwa kowa yayi abinda yake so!."

Cizon leben shi yayi tare da kurawa VC idanu.
"You can change any one! But whatever You change your self is ok"

Jikin sune yayi sanyi, sannan ya cire glass din fuskar shi. Ya nuna musu.
"Kunga abinda yayi min! Yau badan mun san juna ba, tun yaranta babu abinda ya isa hanani mishi abu. Sannan ya kira yarinyar da zan aura ya gaya mata hauka da shirme."

Shiru yayi, cikin jin haushi.
"Bana son tashin hankali, shi yasa tun kafin ya lalata musu tarbiyyar Y'AR mutane, na dakatar da shi, amma yaki. A yanzun ma ya dawo zai kuma cutar da ita, VC kaji a ranka yar kace ta faɗa track din Aahil, ya zaka ji.

Ka turota karatu, ta koma maka a korarriya, ya zaka fahimta, sannan ku ba musulman gaskiya bane, domin kuna iya tozarta wanda kuka san bai da galihu a tsakanin ku, dan biyan buƙatar kanku, irin su Husnah ake tallafawa ba a kore su a makarantar ba, ku ajiye duk wata damuwarku VC kudi kake so.
Toh ka duba wayar ka sun shigo, sunyi maka?! Akwai na yan korar ka suma ka basu nasu. Bani son hayaniya shi yasa bani shiga rayuwar kowa. Kai kuma ka fita harkokin Yarinyar nan ko kuma mu cigaba da samun sab'ani da kai."
.
Cikin d'aga murya Aahil ya ce mishi.
"Toh sonta kake ne?! In dai sonta kake ka musulunta mana sai mu buga wasan amma kana arne ai baka da..."

Dawowa yayi gaban Aahil, cikin murmushi yace..
"Idan na fara son Husnah! Toh ba iya makarantar nan ba, duk inda zata shiga babu wanda ya isa tsayawa a gabanta! Idan ina son Husnah. Ba zan musulunta dan ita ba, sai dan rad'in kai na."

Riko hannun Aahil Dr yayi sannan ya mika mishi wata yar botiri, sannan ya cigaba da cewa. "Wannan camera! Da kasaka a dan kunnen Devanah na cire, Aahil ina garin girmanka karka bari nayi maka magana irin yadda kake min bazaka ji da dadi ba, don Allah ka barni na huta.".

Yana gama fad'ar haka ya fice abin shi. Ina aji na kifa kaina ina kuka.

Buga kujeran akayi na d'ago kai.
"Wai kije Inji Dr Bature."

Kamar bazani ba na mik'e, sai gashi abinda ya faru ya zama, abin yayatawa.

Koda na isa Office d'in shi a tsorace na tura, kofar.
Yana zaune ta mai da hankalin shi aikin da yake yi.

Da sallama na shiga ya amsa, fuskar shi a sake.

Kallona yayi sannan yace.
"Kun kusan fara jarabawa dan haka ki nutsu, sannan saura wata uku."

Shiru yayi ban san me yasa yake jin nauyin fada min ba, amma koma meye zan ta zuba mishi ido.

"Bikina da Devanah! Ina kuma nazarin zan ajiye aiki na, me kika gani"

Kura mishi ido nayi kafin nace.
"Allah ya nuna mana lokacin."
Daga haka ban kuma ce mishi kome ba, sai dai na b'ata shiru.

Mik'ewa nayi tare da barin ci
Office din,.

Tun daga ranar na fita hanyar shi. Tare da kame kaina, amma nasan ina matukar cutuwa,

A yanzun mun mai da hankalin mu, kan jarabawar da yake gaban mu,ajiye kome nayi an fuskanci gabamu.

Jarabawar da ya dauke mu, sati biyu. Muna gamawa tun kafin yayi wani yunkuri tuni

na isa sabon Garin Narabi, cike da kewar Innarmu da Babanmu..

Abin mamaki garin da na bari babu ruwa me kyau sai gashi na sanie su da solar.

Ko ina yayi kyau, Manga yake bani labarin ai, duk aikin Dr ne.

A gaba da unguwar mu ana aikin saka Network.

Dan da sai kafita bakin titi zaka yi waya.
Abincin da aka aka ajiye min kamar wata sarauniya.

Haka akayita riritani ta nan ajiye ni ta nan!

---
Lokacin da yaje gidan da nake aka ce mishi ai na tafi bai wani ji Dar Ba, shima ya wuce Abuja.

---
Yana zuwa ya samu labarin Baban Devanah bai da lafiya. Suna asibiti.
(Karku manta Wannan book din kudi ne)

Kuma bikin su ya kusa, sosai dole aka daga bikin zuwa nan da wata hudu gaba.

Jikin dai yaki dole aka fitar dashi zuwa kasar waje, daga karshe ya naushi bokiti aka dawo dashi gida,'.

Mutuwar ya daki kowa, amma babu yadda suka iya, anyi mishi addu'a. Inda aka ce ya sauka a kofar Aljanna Yesu da tawagarsa zasu zo daukar shi.

---
Hutun sati Uku muka yi, gidan mu ya canza ga katon gen da aka saka mana kai abubuwan da yawa gasu nan dai.

Ana gobe zamu koma na shirya kayana, zan fita aka ce min gashi yazo.
Ban yi mamaki, dan nasan zai zo dan haka na kau shi dakin zaure tare da abinci ya zauna yaci kadan sannan ya shigo ya gaida su Innarmu da Babanmu.

Yabi sauran yan uwan Baba ya gaida su, sannan muka tattara, sai Kaduna.

Anan yake gaya min maganar mutuwar da aka musu, nayi mishi ta aziya sannan na kara mishi godiya da irin taimakon da yake bawa yan garinmu dani kaina,.

---
A yanzun da ya rage min sauran watannin na gama karatu sai na nutsu sosai, har nake mmkin

kaina, Dr ma ajiye shi nayi dan nasan auren shi zai yi burina archieve din jarabawata, Mantawa nayi da dr.

Shima sabida yace min zai yi aure shi yasa na fita hanyar shi, kuma ina cutuwa domin ko kirana yayi zai wuya na daga idan na daga toh bana iya cewa kome.
Haka muka cigaba da tafiya.

***Ga masu bukatar sayan book din  nan zasu iya biyan ta wannan acc***

Acct: 0472282105
***Ramlat Abdul Rahman Manga***
***GTBNK*****.....**
200 ***ta bank***
300 ***ta katin mtn domin biyan ta tana ga wannan number zaku turawa***/.+2347035133148👈🏻
***Domin shiga VIP*** 500/ ***ta bank***/600 ***ta katin mtn***....
Yan Niger Republic...
Zaku tuntube wannan number ne +227 84 50 64 76👈🏻
***Idan zaka sayi Kuma Inuwar Gajimare ne*** 200 ***ta bank idan katin mtn*** 300.......
[7/2, 9:05 PM] BAHAUSHIYAH🥰: Babi-As-daya

Silent

Sun zagaye shi kowa da abinda yake bashi, shi kam banda murmushi babu abinda yake, hannun su na sarkafe da juna shi da Devanah.

"Assalamu alaikum!" Na tura kofar, cike da tsoron abinda zai faru.

Zuba min idanu suka yi kamar zasu cinye ni, banda shi da ya kauda kanshi.

"Hey!" Inji Matar da take jingine da kafad'arshi, cikin tsoro tare da zare ido, nace.
"Am sorry! Banan nake Nima ba, maybe next room ne! Allah yabawa mara lafiya sauki"

"Amen! My daughter! Thank you! God bless you"

Yake nayi wanda yafi murmushi ciwo, na juya zan fita, sai lokacin ya juya muka hada idanu, kwalla ne ya cika idona, sannan na fita da sauri.

B'oyayyen ajiyar zuciya ya sauke tare da daura kanshi a na Devanah, kallon cikin idanun ta kawai ya tabbatar mishi jiya bata samu barci ba.

"B! Ni Yarinyar ban yarda da ita ba" Devanah ta faɗa a shagwaɓe.

"Me yasa Devah!" Daniel ya tambaye ta.

"Sabida yadda naga idanunta! B, akwai abinda take nuf.."

Cikin fada Mommah ta kwaɓe ta tare da cewa.
"Lallai baki da hankali, toh bazaki zauna Bama balle ki fara tunanin wani abu nadaban, mutum na fama da kanshi kina shirmen banza."

Shiru yayi tare da lumshe idanunshi, har yanzun Fuskar me cike da nadama yake hangowa, yadda yaga kwalla sun cika mata ido, by now ya san tana can tana sana'arta na kwana biyu wanda bata yi ba.

Amma dole ya kaurace mata, domin ya nuna mata shima yana da wacce zata iya bada rayuwarta domin shi.

Zamewa yayi daga jikin Devanah, dan yasan yau barcin Husnah ragagge ne. Dukda baya son tuna abinda ya faru, amma yayi mata uzuri, har yanzun bata zama cikakkiyar mace me hangen nesa ba. Kuma matsalar mata ba wani katon lissafi ne dasu ba.

Duk abinda yazo kwakwalwar su, ciro shi suke su faɗa. But har ta iya yafewa Aahil.

Kirjinshi ne yayi wani irin nauyi yayinda numfashinsa ya shiga kokuwa da zuciyar shi.

Ai gani haka dasu Mommah suka yi nan aka shiga kiran Jesus Christ!
"Ohh God! Jesus Christ. My Son don't close your eyes, am is me your mother"
Inji Mommah, da gudu Daniel ya fita, can sai gasu tare da likitan.

Cikin tashin hankali aka mishi allura tare da sanya mishi na'urar taimako, fita suka yi daga dakin, kowa na bawa Devanah laifin itace musababin tashin ciwon shi, abin tausayi kuka take sosai ta rasa me zata ce, domin defend kanta amma ina sun ki sauraranta asalima korarta suka yi daga asibitin.

Devanah tayi haukace akan Bature shi yasa duk abinda zasu mata bai damunta, the worst abinda suka mata shine kiranta da Witch. Ƙamar ta ciro zuciyarta ta fidda musu gaskiya amma bata da hali, dan haka ta bar cikin dakin ta fito waje.

Ta zauna tana kuka. Kamar Ance ta d'ago kai sai ta ganni Nima ina kuka a kasar wata bishiyar maina.

Tab'e baki tayi dan ita bata da son shiga damuwar kowa.

.... Da nayi kuka na ya isheni na mike tare da barin asibitin.

Karshe ajiye zuwa makarantar nayi, abuna domin ko naje bani fahimtar kome, ga baki

daya rayuwata bata min dad'i. Kuma kullum sai naje asibitin.

Idan zanje haka zan tsaya nayi sayayyan fruit, na bada akai mishi. Ranar farko basu karba ba, kuma na tafi.

Na biyu ma haka, sabida mutumin ya gaya min, murmushi nayi sannan na rubuta.
H²M, da aka kai yana zaune shi da Devanah, tana karanta mishi story of aledin, wani gurin yayi murmushi wani gurin ya tab'e baki.

Shigo da kayan marmari mutumin yayi sannan ya mikawa Dr yar karamar takardar, mika hannu Devanah tayi ya kalleta. Dole ta janye hannunta, ya amsa.
Bai buɗe ba, ita kuma tana zargin mace ce ta turo mishi takardan,

Har mutumin zai fita, yace.
"Nace ba!"
Juyowa mutumin yayi, Dr ya ciro kuɗi a cikin wallet din shi ya mika mishi sannan yace.
"Nagode"

Godiya mutumin yayi sannan ya kalli Mommah yace.
"Mommah! Ki cire min apple da aya ba, ayi min shi slice a zuba madara a ciki ina son sha."

"Mommah! Karki yanka mishi sai ya gaya mana waye yake kawo mishi wannan fruit din.,"

Zuba mata ido yayi sannan ya kalli agogon bango yace.
"Mommah ku tafi da ita, domin itama ta isa tasa zuciyata ta buga "

Aikuwa Mommah ta buga tsalle tace tafiya dole, dake sunga jikin da sauki shine Bishop ya koma, ya bar Mommah, da Daniel.

Sai Devanah,  musu suka fara har Devanah tayi fushi ta fita.

Daniel mugu dariya yake, dan yana son ganin rikicin Mommah da Devanah, bayan karfe biyar Mommah ta bar zaria.

Dayawa yan school sun zo duba shi, har da A.A, wanda yayi ta mishi. Maganar banza a fakaice, murmushi kawai yayi mishi dan ko humm bai ce mishi ba.

Abinda Dr ya fahimta Aahil so yake ya fadawa Devanah abinda yake faruwa, amma ganin shirun da Dr yayi sai ya bashi tsoro, domin ance shiru ma magana ce.

..... Bayan tafiyar Aahil ne yake nazarin abinda Aahil din yace.
**Ka tsaya iya hurumin ka? da ake na non musulim, domin olrdy na kama zuciyar ta, kana yunkurin wani abu! Mu musulmai bazamu zuba ido pastor ya shiga rayuwar musulma yar uwan**

**mu ba. Nayi maka kashedi ne amatsayinmu na abokai, shi yasa naki gaya maka a gaban yarinyar da zaka aura! Idan kuma kana son iyayenka su sani? We shall see**

Gaskiya abin ya dame Dr sosai, wanda yasanya shi kinyiwa kowa magana na tsawon awa biyu da rabi.

Kuma an tambaye shi yaki magana, Daniel ya kira Mommah a waya tayi ta tambayar shi, amma yaki bata amsa sai ma murmushin da yayi, kawai.

Yau ina shigowa Asibitin naga yan uwan shi zasu fita, suna barin asibitin na shiga cikin da sauri.

Har dakin da yake, ya bawa kofa baya, na buɗe.

"Assalamu alaika"
Shiga nayi dan nasan ba lallai bane ya amsa min, zuwa bayan shi nayi na tsaya.

Bai juyo ba, kuma bai min magana ba.
"Am sorry for what i did for you! Please firgice me! I no am wrong. But"

Yadda ya juyo ya zuba min jajjayen idanunshi a kaina ne ya sani yin baya, ina matsawa yana bina, har muka iso jikin kofar dakin saka hannun daman sa yayi ya bude kofar na juya da sauri.
Kallona yayi sannan ya kuma hade fuska ya nuna min kofar da ido. Hada hannuna nayi guri daya fashe da kuka. Na kasa furta koda kalma daya ne, jikina har wani irin rawa yaƙe, juyar da kanshi yayi ya nuna min kofar.
"Don't throw me out! Don Allah, daga Allah sai kai nake dashi a cikin garin nan."

D'ago idanun shi yayi, sannan ya sake murmushin takaici ya finciko hannuna ya turani waje. Buga Kofar nake ina cewa.
"Don Allah! Ka saurare ni! Wallahi ban san zan bata maka rai bane! Please let me explain."
Shiru nayi sakamakon hango yan uwan shi suna dawowa.

Da sauri na bar kofar na kara gaba, kowa kallona yake.
Na koma kamar mahaukaciya.

Koda suka iso sai da suka masa magana ya tashi a jikin kofar da yajingina bayan shine.

Koda suka ga yanayin shi sun kasa tambayar shi, amma tabbas Dr B yana cikin matsala.

......
I zuwa yanzun daga ni har Dr, mun shiga kunci sosai, dan shi jikin shi kullum sai ya motsa mishi, ranar nake jin Aahil yake fada min, ashe cikin zuciya ce dashi tun yana shekara daya da wasu watannin a duniya, kuma matsalar tunda ya sami wannan ciwon bazai tab'a fadan abinda

yake so ba, sai dai ciwon taci ta cinye shi.

Dake sun saka ido sosai akan shi, shi yasa ciwon yayi kaman ya rabu dashi domin kuwa suna kokarin noma mishi abinda yake so!

Ganin haka yasa Mommah tace a kawo shi, gida su kai shi India.

Kin amincewa yayi sai da yazo da kanta suka tafi dashi.

Ranar da Aahil ya dibo jiki da gulmar zai gaya min, na birkice mishi dole ya hakura ya koma.
A yanzun ina tafe ne kawai karatun ma ba wani fahimtar shi nake ba, amma ina ƙoƙarin shiga makarantar.

Satin shi biyar ya dawo, amma bai dawo makarantar ba sai da yayi wata biyu.

Koda ya iso, abinda yake gaban shi kawai yake yi. Baya ko damuwa da ni, yaki bani fuskan da zan bashi hakuri.

Haka ya cigaba da min, shiru, yana kuma rakani da ido.

Nakan zauna wani lokacin nayita nazarin me yasa na damu dashi? Me yasa nake kuka sabida shi.
Ba shakka nayi Kuskuren gaya mishi magana kai tsaye, sannan kuma nayi abu babu shawaran shi, shi yasa lokaci guda kome ya lalace min tunda yayi advise dina kar nayi wani abu naki ji, gashi sakamakon abinda ya faru bai min kyau ba, tunda gashi daga ni har shi.

We are suffer, sabida bani da Manner of approach, babu wata azancin magana daga gare ni, gashi nan abinda Baba yayi min magana kafin muzo, sai da yace Min kar nayi, amma dake bani magana, sai da na aikata.
Because am stupid child, bana ji na wawance.

Gashi garin niman gira na rasa idanu baki daya.

Kuma abin takaicin, yadda Devanah ta maida makarantar gurin zuwanta, akala zata bani shekaru hudu zuwa biyar, dan tana niman talatin da wani abu.

Idan sun gama abinda za su yi sai ya rakota har inda zata shiga motar ta.

Ina ji ranar yan course din mu suna fada cewa anyi baikon su.
Allah ne ya kaini gida. Sabida bakin ciki da tashin hankali.

Haka zan zauna nayita kuka, rashin iya magana ya ja min tashin hankali....

Abinda na fahimta shi babu ruwan shi dan ya manta dani, nice nake ta dawainiyya dashi.

Ana haka ya bamu group Assigment, wallahi Ni kaina ban san me na rubuta ba, dan yace matuƙa Assigment din bai yi kyau ba. Toh babu ruwan shi.

Ina zaune na saka abinci a gaba.
Hawaye na zuba a cikin abincin aka buga min kofa.

Goge kwalla nayi na mike, ina bude kofar na ganshi, kafin nayi wata Magana ya watsa min takardun a fuskana, yana kallon cikin idanuna.

Har ya bude baki zai magana sai kuma ya share yayi tafiyar shi, da sauri na bi bayan shi.
"Don Allah kayi hakuri! Wallahi na tuba, wannan shirun yana hurting dina Pls am sorry! Wallahi idan baka kula ni ba yau zan koma naje su aura min Manga!"

Har zai magana sai kuma yayi tafiyar shi fasa wata ihu nayi wanda yasan sauran makotana fitowa ganina a durkushe yasasu komawa, kuka nake har da shasheka.

Yana bakin get bai tadda motar shi ba, dan ya jingina da kofar gidan.

Sai da nayi kuka ya isheni z sannan na koma ciki.

Zama nayi a falo ina zuba da hawaye tare da watsi, da kome.

Kallon takardun nayi naga RUBUTUN shi manya, jikina na rawa na dauka.
....
***Wannan hauar fa? Me kika dauki kanki ne? toh ki gyara ko kuma, ki fuskanci caring ove.***

Rungume takardun nayi ina wani irin kuka, cikin tashin hankali.
Ina faɗin.
"Wallahi zan yi me kyau, sai kayi proud dani, wayyo Allah karka yi fushi dani. Innalillahi wa'inna ilaihi rajioun! Ya Rabbi me nayi ne haka. Me na aikata hakan, Wayyo nayi abinda ya dame ni, hasbinallah waliman wakil,"

Kwanciya nayi a gurin, zazzabi ya rufe ni, a gurin.

A nan nayi barci sabida na ci wahala, sabida nayi.

***Ga masu bukatar sayan book din nan zasu iya biyan ta wannan acc***

Acct: 0472282105
***Ramlat Abdul Rahman Manga***
***GTBNK*****.....**

200 ***ta bank***

300 ***ta katin mtn domin biyan ta tana ga wannan number zaku turawa***/.+2347035133148👈🏻

***Domin shiga VIP*** 500/ ***ta bank***/600 ***ta katin mtn***....

Yan Niger Republic...

Zaku tuntube wannan number ne +227 84 50 64 76👈🏻

***Idan zaka sayi Kuma Inuwar Gajimare ne*** 200 ***ta bank idan katin mtn*** 300.......

[7/2, 9:06 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BHSY24

Wato idan kana niman mugun dan sa'ido just find Bahaushen mutum,. Da farko ana ganina da Dr anan jin haushi. Toh yanzun suna ganin mun sami matsala sai ya zamana ana min dariya, wasu ma har da cewa Dr yaci moriyata ya guje ni.

Karku manta bada wasu suke irin wannan Halayyar ba, Hausawa mu na makarantar, dan haka sai na kara kame kaina.

Na kuma cigaba da addu'a.

---

"Don Allah! Mommah! Kiyi wani abu Ni bana son auren nan!"
Ya fada a shagwaɓe, kamar zai yi kuka.

Shafa kanshi tayi cikin damuwa tace.
"Amma kasan bazai yu ba, sabida Kaine babban yaron mu! Kuma mu ya dace muyi maka auren da wacce muke ganin zata gyara maka miracles dinka, kai daban ne a cikin mutane."

Kara wayar shi yayi ya duba, kashe wayar yayi baki daya, tare da kwantar da kanshi a kan cinyarta.

"Mommah! Toh yaushe Ni zan auri wacce nake so."

Rufe mishi baki tayi cikin damuwa tana gyada kanta Kamar kadangariya.

"Son! Allah ya albarkaci rayuwarka ce domin kazama mercifully a gare mu, please son ka bar tunanin wacce zaka so domin zata iya Amfani da sonda muke maka ta rabamu da kai plss son".
Yadda tayi maganar sai ta bashi tausayi sosai,

Haka tayi ta mishi huduba da karya nemi wacce zai fada sonta, idan ya lura Allah ya bashi Devanah ne kamkar rahama, dan haka ya riketa da hannu bibbiyu, zai ji dadin zab'in da suka mishi.

Shiru yayi daga kwance yana saurarон abinda take cewa.
A ranshi kuwa ayar tambaya ya daurawa musu.

*Me yasa basu son na hadu da wacce zan so? Me yasa suke gani na kamar rahama ne a gare su? Me yasa bana jin kome akan Devanah? Me yaasa yafi jin Husnah a ranshi?*

Shiru yayi kafin ya sake murmushi a ranshi ya kuma cewa.
*Uwar rikici! ko sai yaushe fushin zai kare.!*

Mik'ewa yayi daga jikin Mommah, ya bar falon yana haurawa dakin shi ya kunna wayar shi, zama yayi ya jira wayar wani sabon sakon ne ya kuma shigowa.

*Nagode.....*

Shafa kanshi yayi zuwa fuskar shi yace.
"Husnah!"
Tura mata yayi...
*Hey! Ina gaban Mommah ne, kuma bana amsa waya a gabanta!*

Ajiye wayar yayi cikin jin dadi, dan har ya na hango yanda hancinta yake buɗewa, idan tayi fushi

---
Chibok.....

Kallon Eshaya Dan kasa yayi bayan sun gama tattaunawar su.
Fitowa yayi Mr Eshaya Yana biye da Dan Kasa.
"Alhaji! Kasa a ranka kome yazo karshe. Kamar yadda nima Moddibo ya lalata min rayuwa dole shima tashi ta lalace, sai yayi danasanin yafi cikin kwando"

Murmushi dan kasa yayi sannan yace.
"Ina fatan kun yi min kome yadda ya dace? Bana son asami matsala, kuma bana son wani destiny ya ratsa tsakanin su biyu, idan hakan ya faru zan iya rasa kujeran da zan samu na takarar gwamna jahar Adamawa zan iya rasata."

"Ka yarda dani! In dis week zan je ziyara, kuma kome ya faru zan gaya maka"

Yana fitowa aka bude mishi motar shi ya shiga, sannan yace.
"Domin ganin bayan makiyin ka, kome ta kama ayi za ayi."

Yana fad'ar haka yaja murfin motar ya rufe, sannan suka bar garin baki daya.

---
Da wuri yau muka shiga makarantar, sabida akwai text da Aahil zai yi kuma harin shi gabaki daya akai na yake. Ni kuma Dr yaki bani damar nayi mishi wani abu dan yace ana bibiyar alamarina, dan haka nayi watsi da rigimar da ke tsakanin mu, na fuskanci rayuwata.

---

Wata Rigima da ta fito, a cikin Family Dr, ya kuma daga mishi hankali. Wanda ta sashi zazzabi me zafi.

Gashi muna tsakiyar shekarun mu na karshe, dan haka yayi kokarin boye min dukda yana da matuƙar zurfin ciki, zai yi wuya ya fada maka abinda ke damun shi.

A hankali rayuwa take Gara mana, har muka gama makarantar cike da nasara,

Ban ganshi ba, ranar da muka gama jarabawar sai ranar da aka bikin sallmaar mu,abinda Aahil yake b'oyewa sai da ya gaza rike shi a ranshi.

Bayan an karrama ni da sakamakon First Class, ga kyaututtukan da nasamu, kasancewa ta yar arewa kuma Bahaushiyahr da tasami matsala zangota na karshe Bara.

Ina kamar aka bani damar nayi magana. Bayan nayiwa Ubangiji godiya, wanda na fara yiwa Dr. Sannan nayi mishi yabo akan tsaya min da yayi.
Na fadi wasu abubuwa dangane dashi da halayyar shi, da kuma bashi hakuri abisa abubuwan da ya fuskanta sabida Ni.

Daga karshe na juya ga Aahil nace yayi hakuri nasan bai so na amshi wannan sakamakon ba, amma ya gane wani abu a lokacin da kake son ganin  bayan wani a lokacin Allah ke kara mishi nisan kwana.

Daga nan nayiwa Hukumar makaranta, tuni da wasu kusakuran da suke aikatawa, sannan na rufe da addu'a.

Jikin kowa yayi sanyi ban da Dr da Yan uwana da suka zo min, sai murna muke.

Duk inda ka ga mutane yabona ake, sabida nayi abinda ba kowacce ya zatayi ba.

Ai tunda muka koma gidan da nake ban ga Dr ba, duk yadda naso mu hadu abun yaci tura dole muka shiga hada kayana.

Muna gama hada kayan mota na zuwa, na kira layin yaki shiga, ta tura mishi text har na rasa yadda zan yi.

Koda muka shigo garin  Narabi, sake baki nayi dan na tafi babu makaranta sai gashi har da babban Central Mosque.

Muna shiga cikin gari na ga har da asibiti, dariya nayi nace.
"Baba yaushe gwamnati ta tuna ku?"

"A'a! Asma'u! Allah ya tuna mu dai! Kinga kuwa sai mu gode mishi. Babban burina a kullum, idan nayi sallah Ubangiji ya karkato mana hankalin Yaron nan Bature ba. Domin ta ko ina hidima yakewa Musulunci da muslmai."

Abinda Dr yayi a garin ba iyaka, sai da muka shiga naga ana titi sosai.
Gidan mu kuwa, an rusa wani gefe anyi wani hadadden flat.
Daya gefen ana kan aikin shi.

Kunci ne ya ziyarce Ni, gashi bamu hadu ba, har muka dawo.

Kowa sau zuwa yake ana min Barka da zuwa, tare da dubawa ko na kwaso tsaraba boko, ina son ku fahimta. Wannan kadan ne daga cikin halayyar Bahaushe ne, bazai kashe damuwar shi ba sai na wasu.
Dukda ina cikin murna amma a zuciyata ina cikin damuwa sosai, a yanzun na yarda da abinda Zahrah ta gaya min na ina son Dr.

So irin me tsafta nan ba irin wanda nayiwa wancan sakaran ba.

---

Yana gama ganin fitar mu daga school, ya nufi Office din VC ya ajiye mishi takardan barin aiki,

Anyi juyin duniyar nan fir yaki, yace abinda yazo yi ya gama. Tunda ya samu abinda yazo nima.

Daga nan gidan shi yaje  ya kwashe kayan shi ya tura abuja, dama tun ana saura kwanaki ya tattara kome.

Yana gama kwashe sauran ya tattara ya bar gidan duk yadda zuciyarshi ya azzazzale shi yaje ya ganta, ya danne haka.

Da yamma ya isa Abuja dan mota yabi.

Sau uku ana saka bikin shi da Devanah.
(Karku manta da wannan book din na kudine)

A na karshen ne tace ayi musu aure ko ta kashe kanta, jin haka yasa kowa ya shiga halin shi, aka fara shirin bikin, dan tace kashe kanta zata yi.....

Ana cikin wannan yanayin na bikin su, Kawai ciwon shi ya tashi wanda yayi ta aman jini, abinda yayi mugun daga musu hankalin kenan, dole aka kuma daga bikin.

Wannan karon Dr sai da yayi sati biyu me kyau yana coman kafin Allah ya d'aga kafadar shi.

Kowa ya tambaye shi amma fir yaki magana sai dai yace ba komai.

Aka bikin yasha ruwa, babu wani Magana, domin ana mishi maganar auren zai fara shiga damuwa.

---

Yola...

Shiru yayi sannan ya kuma d'ago kan shi, yace.

"Wannan kamfanin da kuke magana akai nifa bani da wata damuwa akai, domin na kai takardan barin aikin. Gwamna da Mai martaba yaki, sannan a cikin mutanen da zasu yi aikin ni bance sai musulmai kadai ba, kowa yana da damar yin aiki a cikin kamfanin, dan haka sun ga zasu iya ne yasa suke zanga-zangar."

. Abin yayi muni fa, domin rikicin takai an dakatar da aikin Kamfanin.

Haka bai ishe su ba, sai da suka shiga ficce har Kungiyar su ta CAN tayi magana, akan ana bawa musulimai dama arewa, shi yasa ake wulakanta su. Abinda yakai har yan kudu suka fara magana.

.........

Alhamdulillah a yanzun abinda ya saura yanzun tafiya service.

Kusan wata uku kenan tun dawowana babu Dr babu alamar shi.

A wannan halin ne aka kiramu, haka na tura mishi sakon.

An kiramu a camp, babu reply. Sakon karshe da na tura mishi shine,

*_My feeling love you, and my. heart just far you. I will love you forever. I miss you ‘mydear. _*

Ni kaina ban san na tura abin har hka ba, sai da naga an kira ni.

Ina dauka aka fara surfa min Ashariya.

Dake wayar a hannun Devanah yake, kuma bai sanya sunan da zata gane ba, sai yasaka Hbauchi.

Dan haka da ta gama min Bala'i ta koma kanshi da yake barci.

A fusace ta shiga dakin shi ta zuba mishi idanun ta masu cike da kishi.

"Husnah Bauchi" ya faɗa kai tsaye.

"Meye alaƙar?!"

Ta faɗa a fusace, kura mata ido yayi, kafin yace.

"Budurwata ce!"

Kura mishi ido tayi bakinta na rawa,

"Your girlfriend!!" Kuka ne ya kwace mata tana shasheka tace.

"Haba ai dole kak'i aurena ashe kana kuma soyayya da Muslim lady"

Murmushi yayi tare da mika mata hannu, yace.
"Na shigar da ita! Zo nan muga ashe tana sona haka."

Kura mishi ido tayi taga gaske manna mata hauka yayi haurawa gadon tayi ta dauki pillow tana buga mishi, rikota yayi tare da sanya kanshi a kafadar ta yana dariya.

Aikuwa ta birkice mishi, sai da ya matseta a kirjin shi, shasheka ta sauke, tace.
"Kasan yadda nake sonka? Me yasa zaka daga min hankali. Kuma wacece wannan hb."

"Ai wata yar wahala ce, amma ina tare dake meye matsalata da wata mace"

Wato dai sakaryan haka ya lallaba ta, daga nan ta shiga bijiro mishi wata rayen na daban..

Ganin zata sanya shi a mugun yanayin yayi maza ya kwace kanshi, dan ta haye kan shi
(🙄😂 yar banza)

Kafin ya tsare mata sai. Da ta sanya shi fidda abu a jikin shi, tsabar shaidanci.

.......
Da haka ya kashe bakin yar banza, kuma yaji zafin sanya shi asarar da tayi.

---
Tunda nasha Ashariya ban kuma kiran shi ba, dan wani mugun tsoro.

Kuma dama matsoraciyar ce, amma fa karku dauka bani kwatar kaina bane, a'a sakon da na tura masa naji kunya sosai.

....
Dake wayar shi iPhone ce sakon na nan, murmushi yayi sannan ajiye a laptop din shi.
Cike da jin dadi.

Duk yadda yaso ya danne abun a ranshi ya ƙasa..
Turo min sakon yayi ran shi fari.
*_I can’t never let you go from my heart, I will love you until the end of my life. _*

Ga sakon ba sabida ina hanyar Yola domin bautar ƙasa. Tafiyar da ta maida duniyoyin mutane da dama tarihi, wasu mafarkan da akayi su na rufe su, boyayyun sirri na bankad'e su......

Yola shine tushen labarina.........
***Ga masu bukatar sayan book din nan zasu iya biyan ta wannan acc***

Acct: 0472282105
***Ramlat Abdul Rahman Manga***
***GTBNK*****.....**
200 ***ta bank***
300 ***ta katin mtn domin biyan ta tana ga wannan number zaku turawa***/.+2347035133148👈🏻
***Domin shiga VIP*** 500/ ***ta bank***/600 ***ta katin mtn***....
Yan Niger Republic...
Zaku tuntube wannan number ne +227 84 50 64 76👈🏻
***Idan zaka sayi Kuma Inuwar Gajimare ne*** 200 ***ta bank idan katin mtn*** 300.......
[7/2, 9:07 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BHSY25
Garin Yola! Tun da muka shiga naji garin yayi min, wani irin son garin da shaukin garin ne ya dibe ni, wanda yasani kasa buyewa.

Inyamurar kusadani sai da ta min magana, sabida yadda taga ina murmushi.
"Da alamu kina son garin nan."

"Kinyi gaskiya, ina son Yoland!"   Yuuuu suka min da ido, cike da mamaki.

Bai dame ni ba ni dai burina na sauka naga garin. Shaƙar iska nayi naji wata nutsuwa ya tasaukar min.

Murmushi nayi tare da duba jakata na ciro wayata, ina budewa naga sakon shi.

Na mai-maita yafi sau goma, can wani ya sake shigowa.
*Welcome to Yola....*
*The Land of Beauty*/ *you're so beauty more than them*

Wani irin murmushi nayi, tare da tura mishi.

Tura mishi!
*Hmmm! you are my...*
Ban karasa ba, na tura mishi.
Can sai gashi ya kuma turowa.
*Pls stop short de words...*
*Ki karasa haka zai sanya ni jin nutsuwa.*

_When I Could be any part .of you, I wish ti be yours forever, to be conCeived in your soul._

Cusa yatsuna nayi cikin gashin kaina.
Tare da cizon lips Ina me lumshe idanuna, bud'e su nayi tare da juya su akan wayar, Wani irin iskar kauna yana fincikota.....

Tura mishi nayi.

*'Tsakanin wuta da ruwa akwai, rashin jituwa! Dan kowanne su idan ya hadu da dan uwansa, so yake ya rinjaye shi, ban san iya adadin lokutan da za'a dauka ana wannan wasan kusa gidan ba! Dr kai Malamin addinin Christian ne! Dr na fito daga hausaland! Taya relationship dinmu zai tafi, idan muka cigaba da haka anya bazamu zalinci zuciyoyinmu ba_*

Murmushi yayi sannan ya turo min da sakon murmushi sosai kafin yace.
*Kina tsoro*
_Yes ina tsoro_
*Toh Kinga Ni bani tsoron kowa! Sai My creator*
*Nima Ina tsoron Allah*
*Toh ki daina tsoron kowa!* *My love for you is true and it's surfaced the day I first saw you. I love you more than I will tell you. *

Murmushi nayi sannan nace.
_Tunda nazo ko hutawa banyi ba sai ciyar dani kake da_

Turo min emojin zaro ido yayi, dariya nayi dan nasan bai fahimci Yaren ba.
Sai da na mishi dalla dalla.
Sai ga sakon shi.
*Bafa Yola suka turaki ba*
*Kamar ya*
Nima tura mishi sakon nayi tare da cewa.
*Toh me ya faru*
*Bye*
D'aga haka koda na kira shi ya saka number na, a black list.
Sabida gujewa tashin hankali, dan yasan sarai katon laifi yake aikatawa, duk da son da lallaba shi da ake bazai hana a karta mishi rashin mutunci ba.

Tashi nayi na fara niman abinda zanci, dambu namar da nazo dashi na hada da burodi (Gaskiya nayi kewar Parisa 🤣😂kaunarta da burodinta ba iyaka)

Haka na tura sannan na sha ruwa, dake ina hutun sallah, ban wani damu kaina ba. Sai dai har ga Allah a takure nake, sabida rashin Wadatacce ruwan amfani, na saba ko nace na fito inda ake wasan ruwa kamar kifi. Allah sarki Innarmu har gori take min wai na kiyayye zuwa inda babu ruwa sai naji tausayin kaina.

Nifa tsabar wasa da ruwana bani rabuwa da mura, sai kace kwaduwa.
......
Abuja....

Zaune yake ya zubawa wayar ido, bayan ya maida sakon kan kan Email d'inshi. Shigowa Mommah tayi sannan ta zuba mishi ido.

Kallonta yayi sannan yace.
"Sannu! Mommah"

Zama tayi a kusada shi tana kallon shi.

"Son kana boye min wani abu a mind dinka! Son Ina maka kallon you fall in love! Sannan d'azun Dr Joshua ya gaya min ka ajiye aiki ne! Sabida wata Hausa lady gaskiya ne?!"

Gyara zama yayi sosai, sannan yace.
"Mommah! Mutane basu son zaman lafiya! Kuma ni da kike gani na bani soyayya da wata mace! Mommah!"

Rike hannunsa tayi sannan tace.
" Munyi magana a church! D'azun na gaya musu reasons dinka na rashin zuwa church, but sun ce ka huta nan da wasu lokuta zasu turaka yola aiki"

Jingina yayi da allon gadon, sannan ya kuma zuba mata ido. Kamar zai magana sai yayi shiru.

Sam bata kaunar wannan shirun domin yana mugun damunta.

"Son! You keep quiet!"
. murmushi yayi sannan yace.
"Babu komai! Ni dai na rasa me yasa baki son ni nazabi macen da nake so ba! Mommah shi rayuwar aure daddaiton ra'ayi ne! Idan ban da ra'ayin wani abu ita kuma tana dashi an cuci yar mutane, ni gaskiya bani da lafiya."

Tab'a wuyar shi tayi cikin damuwa sannan tace mishi.
"Meke damunka? Ina kake jin ciwon?!"
Shiru yayi kawai amma ya fahimci ba wai ta fahimta bane, sauka yayi daga gadon sai da yaje kofar ban daki yace.
"Mommah nifa bana miji bane"
Sannan ya shige ban dakin da sauri.

Aikuwa da sauri ta fita, can sai gasu tare da Bishop da Devanah.

Kowa yana jiran abinda zai ce, yana kwance ya lullube kanshi, sunyi maganar duniya nan gayen nan yana jin su. Karshe fita suka yi Mommah a dame,  sai Devanah ce ta rufo kofar.

Kwaɓe kayanta tayi ta haura gadon, tare da shigewa bargo, Shaidaniya tana shiga, kafin ya ankara. Ja'ira ta riko(Father Christmas din shi 🤣😂😆 zillo zandariya tayie)
Da sauri ya buɗe kan shi tare da mik'ewa yana zare mata idanu, bai san me yasa Devah tayi masifar rena shi ba.

"Ke wacce irin macece?! Sam baki san kunya ba a rayuwar ki, dalla fitar min a daki"

Tashi tayi zaune tana kallon shi, kafin tace.
"Ji min fa! Kai da baka da lafiya, bincike nazo yi! Kuma naji plaintain dinka, is so bi....."(🤣🤣🤣😂😹🙈 I like romantic names)

Wani mugun tsawa ya buga mata, wanda yasata had'iye sauran kalaman. Da sauri ta kwashi kayan ta.

Ban d'aki ya shiga ya sakewa kanshi ruwa, bakin ciki ne kamar zata karshi.

Ina zai iya da zallamar Devanah, idan ya biye mata toh ba makawa tun kafin a sanya musu zobe zasu cinye dadin su a waje.

Shi idan ba dole ba, ko hannun mace baya son rikewa.

Balle kuma ita da yana sake mata, toh ba makawa fyade zata mishi....

Tafita, tana me cin alwashin dole ma yau tazo mishi kwana.
(Karku manta Wannan book din kudi ne)

---

Lokacin da muka dauka muna daukar horo sati shida zuwa huɗu. Kuma an kai ni, wani asibitin wajen garin Yola ne, daga Yola zuwa garin 300 ne.

Idan na tafi tun safe sai Yamma likis, dakyar yau na sami abin hawa napep ne.

Irin jarababbun mutanen nan masu shegen fada ne, da farko yace bazai kai ni a dari uku ba sai dari biyar.

Ban damu ba nace muje, munyi tafiya me nisa, wanda har mun kusan shiga garin yola sai muka ga wani mutum yana gudun ceton rai.

Mafarin Matsalata..
Tare mu yake me Napep yace bazai tsaya ba, Ni kuwa nace.
"Sauke ni! Wallahi bani binka."
Karshe tsayawa yayi. Yayi na fito da gudu. Naje inda mutumin yake na d'ago shi muka taso da gudu dan ina jin suna cewa.
"Kai Guys fito kafin ya gudu."

Aikuwa ya tashi, dakyar muka isa gurin napep din, jin karar fitar abu nayi ta gefen cikina na samu na tura shi ciki, hannun dama na, naji kamar an kuma soka min abu.

Janyo ni mutumin yayi yace.
"Muje karka tsaya domin dukkan mu baza mu kai ba."

Da gudu me Napep yaja muka tafi. Kamar zasu yi hauka.
mutanen, ID card Dina suka samu.

Ni kuwa jini ne yake zuba min, daga gefen cikina, hankali na zaro wayata.
Niman layin shi na fara, mutumin da muka taimaka yace.
"Karki gayawa iyayenki!"

Dan shima yaji rauni sosai.
Girgiza mishi kai nayi domin na fara ganin duhu, a hankali na saka wayar a kunne na, domin yadda nake jin zafin inda aka soka min abun wallahi kamar bazan kara minti biyar a duniya ba.

A lokacin suna cin abinci, yaga wayar tayi haske.

Dan kar a zarge shi sai ya cigaba da cin abincin.

.... Sake kira nayi bai dauka ba, girgiza kaina nayi, cikin bakin ciki.
Na mikawa mutumin dakyar nace.
"Whatsp"
Shiga yayi ya mika min, "pls check B love!"
I zuwa yanzun bani ganin inda muke ma, mika min yayi kaina a kife akan kujeran.
Karba nayi sannan na tab'a inda ake Voice, Amma sai da na girgiza kai na.

"Belove! Be for me! Be my lovely! Be my first choice nd my last choice, My so sorry! But I love you!"

Ni kaina ban san zan kai labari ba, sabida bullet biyu duk da nasan al'amarin Ubangiji ya wuce haka.

Me Napep kuwa kuka ya fara tare da cewa.
"Wallahi kin cuce ni! Haka kawai kinsani jin zawo, gashi garin fitinarki kin tafi lahira, yanzun haka wad'ancan masu babaken kayan zasu sakani a gaba da tambayar k'ak'aba uwarka ta haife ka. Wayyo talatule.

Wannan yar kafiran da tsayi kamar isha, yar banza me kama da kadangariya. Gashi nan kin macce min a keken mutane, shima ba nawa bane, karba shift nake, domin kula da Yarana da Matana, amma wannan me kirar agwagwar taja min, iftila'in rayuwa, domin aka kwace Napep din zaman tagumi, ya ishe mutum.

Yar banza wallahi bani yafe miki, ina dalili zaki sani na shiga tara ba uku. Ba wannan yan bindiga bala'in kadai sun ishe mutum ya sheka lahira."

Haka yayi ta faɗa yana kuka. Mutumin da ya muka taimaka yace mishi.
"Malam kai mu Jauro Usman Moddibo Hospital!"
Da Mugun gudu yake tafiya, domin ba gane gabanshi yake ba, kuma ba fahimtar kanshi yake ba.
Burin shi kar yan sanda su samkame shi ya shiga halin rayuwa, ina dalili. Tsinuwa da Allah ya isan mishi nasha ba iyaka.

Har suka shiga asibitin,  kowa cirko cirko dan an gaya musu Imam Moddibo anyi garkuwa dashi, hankalin asibiti ya tashi, cewa me Napep din yayi "shiga cikin karka damu"

Dake ta bayan gari suka shigo,

Aikuwa suna shiga kai tsaye aka ga me Napep ya shige ciki. Asibitin kai tsaye nan aka mike ana mamakin wannan al'amarin.

Suna shiga akawa Me Napep caaaa,  ganin Mai asibitin aka kawo, cikin hanzari aka kawo gadon majinya aka fara fidda ni, sannan shima, domin jini ya zuba mishi sosai.

Nice dai nafi jigata,...

---
Yana lura da yadda Devanah ta kura mishi ido, bai sanya shi jin ko Dar Ba.

Gashi a gaban abincin amma zuciyarshi babu daɗin ko kadan faduwar gaba yake ji tare da mugun tsoro, tashi yayi ya bar dinning room din.

Yana shiga dakin shi yabi kiran.
Amma ba a dauka ba, kasancewar yabar data a buɗe sai yayi maza ya bude sakon.

Zai saurara, aka kira shi. Dauka yayi suka fara hira da wanda ya kira shi.

Sosai suke tattaunawa, har zuwa lokaci me tsayi, yana idarwa Daniel yana shigowa, nan ma suka shiga wasu tattaunawan

Suna cikin hirar sai ga Devanah, itama ta shigo cikin su, amma zaka ga yadda ranshi ya b'aci dan shaidancinta yafi karfinta.

Koda suka gama hirar ya manta da Sakon Husnah!!!!!

Allah Sarki......Me Napep HUSNAH taja maka masifa🤣😹

***Ga masu bukatar sayan book din  nan zasu iya biyan ta wannan acc***

Acct: 0472282105
***Ramlat Abdul Rahman Manga***
***GTBNK*****.....**
200 ***ta bank***
300 ***ta katin mtn domin biyan ta tana ga wannan number zaku turawa***/.+2347035133148👈🏻
***Domin shiga VIP*** 500/ ***ta bank***/600 ***ta katin mtn***....
Yan Niger Republic...
Zaku tuntube wannan number ne +227 84 50 64 76👈🏻
***Idan zaka sayi Kuma Inuwar Gajimare ne*** 200 ***ta bank idan katin mtn*** 300.......
[7/2, 9:08 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BHSY26

Koda Daniel ya fita Devanah kin fita tayi ta tsaya tana kallon Dr k'asa-k'asa, burinta ta wurga mishi kwayar da zai kara mishi karfi.

Shima fakotanta yake yana son ganin me zata mishi, kamar baya dakin, kamar ance ya d'ago kai sai yaga ta jefa abu a cikin ruwan shi.

Mik'ewa yayi yazo gabanta durkusawa yayi ya amshi ruwan, yana kallon ta.

Kallon kwayar yayi yadda yake narkewa, ajiyar zuciya yayi sannan ya cigaba da murmushi yana juyawa kafin yace.
"Duk yadda kika kai da son na miki wani abu! Ni nafiki. Ina matukar bukatar mace a rayuwata. Musamman irin macen da take da kunya tare da kamewa.

Devanah tun ina Secondry school mata masu aji, suke kawo min hari, kinsan me? Ba halittar jikin mace nake nima ba. True love nake nima.

Soyayyan gaskiya nake bukata, idan na kwanta dake, har abada ba zan tab'a dokin ki ba, amma idan wata Dalili ya faru zan amsheki a hakan babu yadda zan sauya kaddarata.

Please ba wai ni ba koda gaba, karki kuma min haka,dan ga kika kuma min tallar kanki, zan more ki kuma nak'i aurenki babu yadda za ayi dani. Ni ina son ci daga halal ne."

Daga haka ya nuna mata hanya fita tayi, jikin ta a sanyayye. Domin ya gama kashe mata jiki.

.... Tana fita ya shiga ban daki yayi wanka, sannan yazo kwanta tare da kashe wayar dan ranshi.

Makala wayar yayi a chaji, sannan ya kwanta bayan yayi dogon addu'o'in shin

Tunda ya kwanta HUSNAH ke yawo a ranshi, murmushi yayi cike da jin dad'i, kafin daga bisani barci yayi gaba dashi.

---

Yola...
Anyi nasarar cire min harshen, shima mutumin da na taimaka haka, sai me Napep da yaki tafiya wai shi baya zuwa ko ina yan bindiga bala'i su kashe shi.

Shigowar Imam Moddibo tare da Hajja Kubrah sai Fatimah da Aminah wanda suka shigo suna kuka.
Dakin da aka kula da Fa'iz Imam Moddibo ya shiga, kallon shi.
Ganin bai jigata sosai ba yafito.
Akala ranshi yana ɓaci sai dai bai isa yace. Wani abu ba,

Shigowar Dadah da sandarta yana dogarawa. Kowa sai gaisheta yake, tana basar dasu.

"Kai Mala'ikun duniya? Zo nan ina fakizun yake? "
. Ta tambaya tare da watsr da hannunta,A iska.

"Hajiya yallabai Fa'iz yana ciki ana kula dashi, yarinyar da ta taimake shi ne dai take cikib wani irin yanayi, domin jiki ne yake zuba daga jikinta,"

Niman guri tayi ta zauna, tare da saka kuka.
"Yanzun Fakizun ma bazasu bar
Min shi ba,sai sun ga bayan shi.... Allah ka zama gatan mu. Allah duk me hannu a cikin wannan al'amarin Ubangiji tun daga duniya kafata nuna mishi kasawar shi. Ubangiji ka zame mana garkuwa, kuma wannan aikin Zabba'u ce, munafuka, algunguma sai ka ganta kamar na Allah amma zuciyata babu Allah sai Ula, uwar shaidanun."

Babu wanda ya dakatar da ita, sabida sun san fadatarta sai ta juye kansu.

An sami fito da Shi, mutumin nice dai sai da aka nimo jini aka samin....

---

Kallon shi suka yi jikin suna rawa, hankalin su a tashe, domin wannan karon sun fadi.

Ya juya musu baya sai harbi yake, sosai.

"Yallabai mun sami! Id card din yarinyar da ta taimaka mishi, yar bautar k....."

Tusssss! Aka sake mishi dalma "Asarar da kaja min na miliyan dubu goma be! Tsinanan ne!

Kuma wallahi duk sai na kashe ku..."

Kafin su yi wani yunkurin an zauna musu dalma, sannan ya kona ya cigaba da ajiyar zuciya.

.....
Abuja...

Sam Dr ya manta dani, bai nime ni ba sai da safe bai ga sakon da nake tura mishi safe da maraici ba, sam ya manta kome nice kawai yake buqatar na kirashi.

Shiru shiru, can ya kasa hakuri ya kira ni, anan ne yaji wai bani kusa da wayar.

Kai duba wayar yayi abin tashin hankali yaji sakon da na tura mishi a firgice ya fita a gidan, dan b'atar basira kawai yaje zai bi motar kasuwa.

Tunawa yayi da akwai jirgin sama ya tafi airport, ya kira layin a a kashe.

Ji yayi kamar baya da sauran amfani dan koda ya isa Yola haka ya gama yawo bani ba labarina.

Kuma kiran yaki shiga, dakyar ya dawo da sabon zazzaɓi.
(Karku manta Wannan book din na kuɗine)
.....
Wato kuwa abinda ya faru muna shiga asibitin wayar tana cikin Napep din bayan a fidda mu, shine aka sami wani mara imani ya sunkuce yana dauka ya cire layin, ya zuba a Napep din yayi gaba abinshi..

...... Sai da nayi kwana Biyar, lokacin yan sanda sai sunturi me Napep yaki yarda a saka shi acikin maganar, dan mai da Napep yayi ya bar garin.

Kin report akayi sai zuwa ofishin yan bautan kasa aka gaya musu.

...... Mika min tea tayi tana murmushi, tare da cewa.
"Sannu! Ya jikinki?!"

Sai da na mata murmushi sannan nace.
"Da sauki! Amma meye ya same ni"
"Ai lokacin da kika taimaki Yayan mu aka harbeki a gefen cikin ki da bayan hannunki."

Zan bude baki nayi magana aka turo kofar, dai dai na kai kofin tea din bakina na ban san lokacin da na furza ba, tare da kwarewa.

Zaro idanu nayi waje, jikina na rawa.

Kafe ni da ido yayi, Nima ma son yi mishi magana nake amma ban san yadda zance ba.

Rudani na shiga, Dr. Kallon shi na kuma yi kafin na gyada kaina nace mishi.

"Kayi hakuri! Banga phone suna bane."
Irin kallon da yake min ya hanani Magana.
(Karku manta Wannan book din na kuɗi ne)
Kallon mamaki, da al'ajabi. Ni kuwa na cigaba da bashi hakuri. Da yaki kulani na saka mishi kuka.
Fita Aminatu tayi me jinyata wai zata kira likita.

"Don Allah! Kayi hakuri ka daina min shiru wallahi bani jin daɗin shi, nasan nayi kasassabar shiga wannan lamari, amma halin taimak..."

Gama duba file dina yayi, sannan ya zuba min wani irin kallo, me cike da tsana.

Takowa yayi. Cikin b'acin rai yace.
"Kee! Kin hanani abinda yake mallakina, idan turoki akayi. Zaki gaya musu. Har yau babu wanda yake iya banbanta kamanina dana Fa'iz, kin lalata  min shirina, amma zaki amshi hukunci dai dai dake!"

Bakina a bude na zuba mishi ido da hanci, koda suka shigo, rud'ewa nayi sakamakon shima wanda aka kira likitan kamar su ta b'aci. Kafin su min magana na sulale na suma.

Nan shi wanda ya fara shigowa, yake cewa.
"Abinda ya faru ina ga ya shafi brain ɗinta, domin daga shigowa na ta fara surutu. A kaina dakin duba marasa lafiyan brain."

"Yan Sadeeq! Ina gani...."

"Toh shi Kenan, amma duba sakamakon ta, akwai bugawa a kai."
. Haka suka dauke ni, aka kai ni. Inda akayita gana min azabar lantarki, sabida Kuskurena.

....... Dr ya shigo Yola yafi sau a kirga, sabida sha'anin tsaro anki gaya mishi inda nake. Kamar mahaukaci ji ya koma.

Dalilin da ya matukar tayar mishi da ciwo, aka fita dashi zuwa India.
...... Haka Narabi babu wanda hankalin shi bai tashi ba.

Abin bakin ciki babu waya ta.

--

Karfi da yaji Mutmin nan ya mai dani, mahaukaciya. Aka ware min d'akina.

Ina zaune na cusa kaina a tsakiyar cinyoyina, ya shigo.

Jan kujera yayi yana kallona, kafin ya sake murmushi,
"bani da burin cutar dake, zan kyaleki. Tunda baki san kome ba, toh amma taya zan kyale ki haka babu moruwa, gaki mace har mace amma yar baka."

Tashi yayi ya rufe kofar, sannan ya dawo gare ni, "

"Husnah HABIBU Manga. Ina son gwada atisaye na, na musamman akan ki yake nan.? Kinyi min shishigi, shi yasa na miki horo da cutar hauka, aka ta zubawa kwakwalwar ki wuta. Toh ba wannan ba, kin tsallake mutuwa ne sabida surar jikinki, na manyan mata ne!"

A dai dai lokacin da ya nufi Ni. Kwalla ne masu zafi suka zubo min.

Bakina ciwo yake min sabida, saka min wani roba.

Matsawa na fara yi, yana bina. Take kafana yayi sannan ya durkusa a gabana, ya kifa min mari.
Tare da ture ni, na fadi.

Kai hannun shi yayi tare da tura kayan jikina sama, mugu a cinyoyina kawai ya sussuce.

Ai kamar wawa ya fara kokarin, ketare iyaka.
Sai dai kash..... Oga me jar mota ya hanashi yin komai, dan babu Always kuma na b'ata jikina.
Marina ya fara yi, tare da saka min sarkar dake hannuna ya shake Ni.

Kai Wannan mutumin mugu ne, sai da yaga na kusan mutuwa ya kyale ni. Ya kuma bar dakin.
Bayan tafiyar shi, can suka zo duba ni. Aikuwa suka ganin a mace zance kenan.

Dake da Iyayen su ne, take aka fara yiwa daya likitan fada.

Kiran nurse aka yi suka kaini ban daki, tare da min wanka. Aka dawo dani bayan sun kimtsa min jikina.

Ruwa aka sanya min, sannan Baban su yace.
"Gaskiya kar a kuma sanya mata karfen, domin zata iya kashe kanta. A lura da ita sosai. Idan bazai samu ba, za a fitar da ita waje."

(Karku manta Wannan book din na kuɗine
"A'ah! Abba ina ga a barta ma zata ji sauki..."
"Toh algungun algumgumi, jibe shi kamar mutumin Allah nan kuwa ko tsure ya sallama maka, munafiki! Ince dan kwal Ubanka kaine ka fara kira mata sunan ciwo. Yarinyar nan ranar da nazo ban ga hauka a jikinta ba, amma dake ka tsotse makirci sai da ka daura mata ciwo, mugu me kama da tubabbun arna, katara uwar suma kamar shikar angulu."

Inda take shiga ba nan take fita ba, ga baki daya ta birkice musu, ita lallai a fitar dani kafin wasu su kashe ni, dan ita har cikin zuciyar ta nake. Sona take ƙamar ita ta haife ni.

Abun dariya abin tausayi, dan dole aka shirya min tafiya, shigowar wata mace.

Me matsakaicin tsayo da shekaru, amma sabida hutu ya boye shekarun, tsaki Imam Moddibo yayi tare da kafe daya likitan da ido kasa yayi da kai, yace.
"Afuwa ! Abba ban san zaka ji ba dad'i ba, amma kuma asibitin muna bukatar Ummi."

"Kai tafi can bar bashi hakurin, ita kanta hakurin taci uwatai, ke Zuhrah duba min yar mutanen daga abin arziki, sai aka saka mata da Sharri. Eh mana ban da halin tausayi irin baki ba, har wata munafuka ta isa rabaki da mijinki, wallahi Moddibo, idan baka dawo da Zuhrah ba, zan sab'a maka. Kai Fakizu Allah ya shimaka albarka. Kai ma dan banza kaki aure sai tara uwar gemu, ana asuwaki.

Gefe guda ana bin yan mata masu duwaiwai da nonuwa da ido, bar sunkuyar da kai .
Fitsararre kayiwa wancan munafukar wiki-wiki da ido.
Moddibo kamo min, Dan matar ka naci mutuncin sa da sanda na."

Wannan matar yar Bala'i ce, domin kowa sai da ta zage shi tass sai Hajja Kubrah da Ummi Zuhrah ne bata zage ba, hatta danta sai da ta mishi tass, har da mishi gorin arzikin shi ta dokar auren Zuhrah yayi shi, sannan yar aiki taci amanar su. Nan da ta gama ta dawo kaina tana fyace hancinta.

"Yarinya sai Allah ya bi miki hakkin ki, dan nasan lafiyar ki kau. Kawai cutarwa ce aka miki, gashi, babu hanyar da zamu sadaki da danginki, tunda ance kar a sanar da kome,. Kai ma Fakizu. Mugu ne taya aka sakewa yar mutane alburushi baka taimaka mata ba, bayan kai taimaka gaskiya Moddibo makiya na kewaye da kai, sun lullube masoyanka, abinda za ayi ka zuba min ido nayiwa wasu munafukai tofin Allah tsine"

"Don Allah! Dadah kiyi hakuri mana, fadar ya isa haka. Mara lafiyar bata son hayaniya, idan kika cika fada ciwon tashi zai yi tunda Kinga an hana mu shigowa d'azun."

....... Wai me Dadah zata mayar Allah ya kare likitocin.....😹

***nan zasu iya biyan ta wannan acc***

Acct: 0472282105
***Ramlat Abdul Rahman Manga***
***GTBNK*****.....**
200 ***ta bank***
300 ***ta katin mtn domin biyan ta tana ga wannan number zaku turawa***/.+2347035133148👈🏻
***Domin shiga VIP*** 500/ ***ta bank***/600 ***ta katin mtn***....
Yan Niger Republic...
Zaku tuntube wannan number ne +227 84 50 64 76👈🏻
***Idan zaka sayi Kuma Inuwar Gajimare ne*** 200 ***ta bank idan katin mtn*** 300.......

Don Allah kayi hakuri na saka chaji ashe bai dauka ba....
[7/2, 9:10 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BHSY27.

D'ago kai tayi ta kalli Imam shekeke! Ta tab'e baki sannan tace.
"A dauri kashi ko a b'ata igiya, turancin taci kaniyarta, kaji min yaro zaka mai dani hudu ila taro sisi! Gani nan jarababbiya ina muku ihu a cikin asibitin ku! Wato Moddibo!"

"A'ah  Dadah lalura irin wannan baiwar Allah ba acika son ana hayaniya akan su ba, muje a barta." Inji Ita Zuhrah.

Wacce Hajja Nenneh take Binta da mugun kallo.

Rubuce rubuce tayi sannan, ta fito har zata wuce, taje dai-dai fuskar Imam Moddibo tace.
"Usman! Ayi gaggawar fita da yar mutane! Kuma ayi kokarin bin diddingin mutanen da suka aikata hakan, in ba haka ba za a cigaba da aiki ta kusakuran baya, kalleta innocent lady. Daga taimako za a saubanta rayuwarta! Don Allah ba dan nima ba dan kowa ba. Kodan soyayyar ka da Siddiqu!"

Tana gama fad'ar haka, ta kalle Hajja Kubrah wacce fusakarta babu damuwa sab'anin Hajja Nenneh, wacce take cika har da hura hanci.

"Kubrah! Sai hakuri fa, dan na kusan dawowa gurina."

Murmushi tayi sannan tace.
"Addah Zuhrah Allah. Ya dawo dake lafiya!"

Cikin dariyar kular da mutum kyalkyale dashi tace.
"Mai Water melo! Sai nazo hira dan wannan zuwan nawa bana kome bane! Mai taburama yazo...."

Aikuwa Dadah tace.

"Me guri ya naɗe."

Haka suka yita yada magana daga Dadah har Dr Zuhrah, idan kaganta ta girma amma tana da matuƙar wayewa, na zamani da na addini.

Fushi da b'acin tai yasan ta yin karatun addini da na boko, dan dama na bokon tafi bada himma akai, kimanin shekaru talatin da bakwai, da rabuwan su da Imam amma har yau bata ji arangama tayi aure ba.

Tana aiki a wani asibiti a can garin su Gyambo ne!  Fa'iz dama ya jima da son ta dawo asibitin, amma Imam Moddibo yaki fir.

Yanzun ma Dadah ce ta Fa'iz yaje ya dauko ta.

---

A gida kuwa hukumar bautar ƙasa ce ta tura musu, da cewa Allah yayi min rasuwa.

Aka kawo musu kayana, tare da kome nawa.
Duk karfin halin Baba sai da yayi kuka sosai, ga Innarmu da sai da jininta ya haura.

Ba iya iyayena suka shiga damuwa da rashina ba hatta yan uwan Baba sai da suka yi kuka sosai.

Haka aka min Addu'ar bakwai da raina aka min Addu'ar bakwai.

---

New Delhi!

An sami nasarar sakawa Dr wani karfe kasancewar zuciyarshi bazata iya daukar nauyin wasu damuwa ba, sabida tayi rauni.

Yau aka fidda shi daga aikin karshe wanda ake da tabbacin Successful.

Kullum Mommah suna church. Addu'a Allah ya daga kafad'arshi.

---

An fitar dani zuwa Egypt. Anan likitocin suka yita fada, taya zasu saka min abin duba kwalkwalwa, gashi badan Allah ya takaita ba, da yanzun na samu matsala a kwalkwalwar dan da an cigaba da samun lantarki a kaina.

Dake an zuba kudi sosai, sati na Daya, na fara gane mutanen da suke kaina.

Tunda na dawo hankalina, naki musu magana sai bin su nake da ido, abinda na fara

nima waya ta.

Burina Mutane biyu. Iyaye na, sai Dr.

Shigowar Iyalin Imam ya sani kara firgita, rike kaina nayi. Na fashe da kuka.

Wanda narasa yadda zan yi. Ja da baya nake sai da na kai can karshen gadon.
Sannan daya daga cikin masu kama da Dr yazo bakin gadon.
"Sannun! Hmm kiyi hakuri yanzun ina ke miki ciwo."

Ciro kaina nayi, hawaye na zuba. Na kura mishi ido, banbancin wannan da na ranar shi bayi da magana da sauri. Fuskar shi a sake yake.

Ina d'ago kaina muka yi ido biyu da wancan mai da kaina tsankankanin cinyata, na fashe da kuka nace.
"Ku kaini gurin shi."

Murmushi na bayan yayi sannan yace.
" Na gaya muku yarinyar nan tayi hauka, ku kaita gidan mahaukata kawai."

Tsoro ne ya kamani tare da zaro Ido na waje.
"Idan dan taimakon shi da nayi ne nayi laifi ku gafarce Ni! Wallahi zan bar garin baki daya na koma inda na fito ni dai don Allah karki kaini ko ina, lafiyata lau."

Shigowar Dr Zuhrah da wasu likitanci yasanya ni, dadda tsorata. Ashe haka yana kuma karawa mutum shiga halin tab'in hankali.

Ga baki daya na gigice, sai zare ido nake. Na rasa abinda ke min dad'i.  Nasan da yau Dr yana kusadani da babu abinda zai same ni, kuma wadannan mutanen masu kama dashi, kara tsorata ni, suke.

Daure ni, akayi da wasu belt aka turani a keke. Ina ce musu ni lafiyata lau, amma fir suka ki yarda.

Haka suka kai ni, dakin duba kwalkwalwa, aka duba babu komai sai tsabar tsoro da firgici yake sanya ni shiga wani yanayi.

Bayan a dawo ni, suka min alluran barci,

Duk abinda kaga ya sami bawa toh tun asali mukaddari ne! Haka Allah ya tsara mishi.

A fahimtana akwai abinda yasa wannan mugun me kama da Dr Bature yake nufi dani, kuma na kasa fahimtar kome.

Abin mamaki, duk shigowar shi zaka same shi yana murmushi.

Da dadare ina kwance ya shigo, zama yayi tare da kura min ido.
Wurga min id card din yayi cikin murmushi.

"Zan baki dama daya! Idan kika gaya min gaskiya zan kyaleki, kuma zan tabbatar da lafiyarki lau, idan kuma kika min karya. Gobe zan sanya su ta sanya miki lantarki har sai ya lalata miki kwalkwalwa. Sannan shima mai Napep din da ya dauke ki, an bi an kashe shi.

Muna goge hujja a kanmu ne dan gudun fadawa matsala.
A ranar da kika dauki. Dan uwansa a hanyar ki na dawowa daga gurin da kike bautar ƙasa, sunan waye aka kira?!"

Wallahi na manta kome a ranar dan tun daga ranar ban kuma tuna kome ba, hawaye ne ya zubo min masu mugun zafi.

A hankali na fara magana.
"Dukkanku uku! Kamarku ta b'aci! Bani da abinda zan iya cewa? Iya abinda na tuna sakon da na turawa My Been! Daga nan wallahi ban san kome ba, ka yarda dani!"

Na karshe maganar cikin Kuka, tasowa yayi zuwa gabana, ya tattara gashina zuwa baya. Sannan ya sake murmushi kafin yace.
"Husnah HABIB Manga! Yar karamar hukumar toro! Kece babba a gidan ku! Motsinki da walwalanki shine farin ciki iyayenki! You fall in love! With da Wani Kirista!! Sannan Fa'iz ya faɗa Soyayyarku! Abbanah ya kuma bashi goyan baya, Abbana da Fa'iz, sune fuskar da ya hanani nuna nawa fuskar! Kina da kyau! Sosai just ke bak'ar ce! Idan hakan nasan kome akanki! Tun wancan watan akayi addu'o'in mutuwar ki!"

Kura min ido yayi sannan yace.
" Baki ji wani abu ba a ranar?!"
"Wallahi ka yarda dani! Ban ji kome ba! Idan da naji Allah zan gaya maka!"

Fuskar shi ya kawo dab nawa, sannan ya ciro wayata, ya mika min.

Da sauri na mika hannun zan amsa yayi baya. Yana kallona.
"Na tura hukumar ku! Nasa ace kin mutum! Nima bayi na bane daga sama ne aka sani! Kisan sabida me? Don min wancan mutumin da yake daukar nauyin ki! Ji nake kamar nadauki wukata nayita caccaka mishi har sai ya daina motsi! Sabida shi ya kashe min gobe na! Ya kuma tab'a min Ji kimata!

Zaki koma garin ku! Amma abisa sharadin bazaki amshi tayin soyayyar wancan kanin Nawa ba! Domin nima ina son naga na ajiye classic lady irinki! No karki dauka aure, zan ajiye ki

ne dan jin dadin kaina.

Kalle ni ban haɗu bane? Nasan na hadu iya haɗuwa. Sai mun ma Cancare a gado zaki gane ni na mijin gaske ne! Ya zski bi sharadina ne ko sai na yanka miki ticket din zuwa lahira kyauta ba sai wani yazo ya karb'a ranki a wahale ba "

Tun da naji haka na fahimci babu addini a cikin rayuwar shi. Ji nake kaman na tambaye shi akan me zai kashe uban shi, sai naja baki na nayi shiru, domin na fahimci bai da mutunci duk mutumin da yake tunanin ya kashe Uban shi dan wata janabi na rayuwa toh ya kwala asara. Taya zan kashe mutumin da ya kawo ni duniya.

Gyad'a mishi kai nayi, daka min tsawa yayi yace.
"Kiyi magana! Da bakin ki not body language."

"Na amince!" Na fada mishi ina kuka.
Murmushi yayi tare da jan hancina, yace.
"Wannan da alamu gayenki ya saba miki da rarrashi ni kuma ban iya ba"

Takurawa nayi guri guda, sakamakon yawon da ya fara da hannun shi a jikina.

Ganin har zuwa lokacin kuka nake, tare da kame jikina.. yasa shi yin murmushi, kafin ya cigaba da cewa.
"Ina son mace me tsoro kamar ke! Ina son inga taji tsoro tana fidda idanu a tsorace. Kamar dai ke! Bani son mace Matsiwaciya, nafi son matsoraciya, wacce da zaran taji tsoro zaka ga hakan a fuskar ta da idanunta. Ina son ganin tsorona a idanunki!"

Tura kaina nayi, a cikin cinyoyina. Ina shasheka. Sai da ya gama razana ni sosai sannan ya dauki allura yayi min yana fadin.
"Ni likitan kwalkwalwa ne, ni nafi dacewa da zama likitan mata, aka dauka aka bawa wani banza can, mu kwana LAFIYA sleep beauty!"

Yana ganin nayi barci ya isa gabana ya dauke ni a hoto babu iyaka, sannan ya shiga niman wata layi a watan shi.

Sun jima yana gaya mishi babu abinda Husnah ta sani, don Allah a kyale ni, kawai tunda ban san kome ba. Yadda yake maganar zaka san yanayi ne, da wani na shi. Tare da kaskantar da kai.

Yana gama wayar ya fita, cike da jin dadi.

.......

Kusan wata guda tunda aka mishi aikin zuciya yana nan da halinshi na rashin son magana, sai bin kowa yake da ido, hatta likitocin baya musu magana. Sai da Mommah ta sashi a gaba

da kuka, rike.
Hannun shi tayi cikin kuka da damuwa tace.
"Son! Don Allah ka fada min meke damunka? Son I can't tolerate halin da kake ciki dan ji nake kamar zuciyata zata bugawa idan baka gaya min abinda ke damun ka ba!"

Kwalla ne suka cika mishi ido, sosai sannan yace.
"Ba zaku bani abinda nake so ba! Ba zaku min yadda nake so ba! Tsanata ne zai maye gurbin soyayyar da kuke min! Mommah ina sonta! Tab'a kiji duk wani beating da yake da sunanta yaƙe fita. Duk wani fitar numfashina da HUSNAH yake fita, Mommah zaku hanani sonta shi, Mommah....."

Kauuuu ta tsinka mishi mari cikin fusata, ranta na kara b'aci.

Idanun shi jajjur ya kalleta, murmushi yayi mata sannan yace.
Kashe min jiki yayi, idan da sabo yaci ace na saba da karatun B,.Amma Kullum najini a kirjin Sadauki maza mantawa nake da wacece ni, domin shi kaɗai na sani a duniya ta.
"Muje na gaisa da Zarh! Har da my lovely wife!"

Dawowa hayacina nayi, tare da barin jikin shi ina tura baki nace.
"Wallahi ban isa ba! Kaje kayi min wani cikin, ce maka aka yi, aikin da sauki ne, toh har yanzun ban warke ba."

Saka bakin shi yayi a hankali yace.
"Wallahi muna zuwa bazamu jima ba, kuma nasan yadda zan miki bab...

***nan zasu iya biyan ta wannan acc***

Acct: 0472282105

***Ramlat Abdul Rahman Manga***
***GTBNK*****.....**
200 ***ta bank***
300 ***ta katin mtn domin biyan ta tana ga wannan number zaku turawa***/.+2347035133148👈🏻
***Domin shiga VIP*** 500/ ***ta bank***/600 ***ta katin mtn***....
Yan Niger Republic...
Zaku tuntube wannan number ne +227 84 50 64 76👈🏻
***Idan zaka sayi Kuma Inuwar Gajimare ne*** 200 ***ta bank idan katin mtn*** 300.......
[7/2, 9:17 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BHSY47

Shiru nayi zuciyata na lugude, sabida, Juyowa yayi ya amshi yar shi, yaja hannuna muka fita.

Munyi yar tafiya sabida akwai tazara a tsakanin gidan shi da mall din.

Kai tsaye dakin shi ya wuce damu, wani katon hoton Zar-minah ce an nad'e ta da pink showel. Tun ranar suna da aka ɗauki hoton ban kuma saka mata showel din ba, dan suna dayawa.

Sauke idanuna nayi, akan dan rubutun da yayi, cikin roma language.

Hannun shi naji a waist Dina na juya a hankali, tare da zuba mishi idanuna. "Nooruz zaman!"
"Yes Mahnoor! Me kike bukata!?" Ya tambaye ni, tare da sumbatar yatsun hannuna da na saka jar lalle.

"Hmm! Dama"
Na fada a hankali. Janyo ni yayi jikinshi yana fad'in.
"Ina jinki!"

Shiru nayi, na rasa ta yadda zan gaya mishi hannuna na kai botirin rigarshi, ina ballewa da rufewa.
"Kinyi shiru kuma!"
D'ago kai nayi ina kallon cikin idanun shi? Kafin na sunkuyar kasa ina jin babu dad'i, kafin nace.
"Hmmm! Dama akan matar can ta naij...."

Murmushi yayi sannan ya sumbaci bakina, sakewa yayi sannan ya kai bakin shi haɓɓana, yana tsotsa a hankali, kafin ya kama lips Dina yana taunawa cikin nutsuwa.

Rike rigar shi nayi, domin na fara jin kome yana sussuce min, janye jikina nayi, tare da. Kallon yadda Zar-minah, take barci yarinyar da ko a gida bata kaunar ka shimfida ta, ta bude ido, gaban gadonta na tsaya. Ina nazarin yaushe rabona da muyi magana dashi, shiru nayi ina nazarin abin kafin na juya idanuna na kalle shi.

Shima Ni yake kallo, sam idan ba ta kama dole, bai cika tsawaita zantuttunka ba, sabida hakan ba damuwar shi bace, idan har zaka ga kwarewa shi, toh akan Headquarter ne, yanzun zaka ga rawan jikin shi.

"Muje muyi wanka!"
"Haba ina nayi, ka bani amsar tambayar da na maka, meye matsayin Devanah?!"

Zuba min ido yayi na wani lokaci kafin yace.
"Wannan matsalar bata shafe ki ba."

Wani irin kallo na mishi, kafin na gintse fuska nace.
"Ta shafe ni! Kalli wancan Yarinyar, nice na sauke maka ita, ashe kuwa babu abinka da bata shafe ni ba, sai dai idan ban da niyyar shiga ciki."

Rike kafaduna yayi ya jijjiga ni, sannan yace.
"Allah bani son rigima! Muje muyi wanka."

Ture hannun shi nayi duk biyu ina me kara tsuke fuska nace.
"Zaka gaya min matsayinta ko sai na dauki Y'ata na kara gama!"

Sake bakin shi yayi cike da mamakina, kafin ya tsuke fuskar shi fiye da lokacin baya da muke A.B.U.

"Bazan fada ba! Husnah! Indai dai sai kinyi threaten ɗina, akan hakkina shine zan gaya miki gaskiya wuce ki fitar min a d'akina, kuma wallahi kar na kuskura na ga kafarki a waje, ina ba haka ba zan sab'a miki, fitar min a daki."

A fusace na juya zan dauki D'iyata, cikin jin shi din wani ne yace.
"Ajiye min Y'ATA! Sabida da zan dauko ki daga Sokoto, babu cikin ta. Sannan sai da kika zama mallakina nayi cikin ta, dan haka fita kafin fushina ya ribanya kanshi na shayar dake danasani, kije ki rike abin da kike da iko akan shi, a yau idan ina bukatar biyu a take zan same su."

Fuuu na fita daga dakin, na shiga daya dakin na kwanta, cikin bakin ciki.
Kuskuren mune fa! Da zarar munga miji yana ɗokin mu sai mubi mu shiga jin kai ai mu din bazamu tsaya a nan ba, sai fangima da fankama ya kara hawa! Kuma duk ba kome yake janyo haka ba sai akan kishi mara hujja, ina ruwa na da Devanah, zama da miji da iyawa ce, amma ban fahimci hakan ba gani tunda muna addini daya dole ya rabu da Devanah, dan nice nafi dacewa dashi.

......
Wato B yayi fushi sosai, dauke min wuta yayi, ga nono ya cika amma ya hanani yar shi na bata nono, wunin ranar fita yayi ya kaita Gurin Ummi, ita ta ansheta ta Bata madara, sannan ta bashi ya dawo min da ita, dan tun da taga bana cikin mall din tasan ya dauke ni.

Taga ranshi a b'ace amma bata tambaye shi, sabida bata son ta same mishi, asusun ajiye duk wata damuwarshi.

Gani take matuƙa ta shiga al'amarin gidan shi tabbas, zata iya zama mara adalci. Shi yasa har zai tafi tace mishi.
"Kayi hakuri! Indai laifi tayi maka, tana da dadin zama kuma tana da hakuri. Ajizanci ne irinta dan adam, domin babu wanda Allah ya halicci shi cikakke, dole sai ya samu tawaya. Ka gaida min ita, kace Dadah na kewar kawarta!"

Yake yayi sannan ya fito, daga inda yake zama idan yazo, koda suka iso ina kwance a falo.

Sam ban karb'i laifina ba, sai kawai yana shigowa na fashe musu da dariya. Kamar wata mahaukaciya, abun ya kashe mishi jiki, sai ya muzanta gashi dai daga Ni sai shi.

Juyawa yayi ya kalle ni, cikin sanyin murya yace.
"Ni mahaukaci ne?"
Ya ajiye Babyn! Ya taso kaina.

"Ki gaya min! Ni mahaukaci ne? Meye nayi miki da nayi Deserve haka! Meye laifina! Toh bari kiji wallahi nafi son Devanah sau dubu akanki? Sabida idan itace bazata min dariya ba, wato dan ina damuwa da alamarinki shine bari ki min dariya! Sai kin gane baki da hankali, dani kike zancen."

Ya fusata sosai, kuma ya daina zaman gidan da yarinyar nice dai ya hanani fita, dan ko da Dadah ta nime ni. Gaya mata gaskiya Ummi tayi ina tare da Jauro!

Nan ta balbale su da masifa taya zasu barni na tafi gurin su ba tare da na gama jego ba.

......
Ban san me yake ciki, ba sai dai naga ya ajiye min yar not.

_Ki fita zuwa gurin su Ummi, za a zo a gyara gidan_

Dama zazzaɓi ya dame ni,dan kwana uku kenan, rabona da yarinyar.

Da murna na shirya na tafi, acan gidan na same su, dan haka na sameta tana ta, zunduma ihu, ina shiga Dadah ta Harare ni, tare da nuna min na shiga ban daki na wanke nono nazo na bata.

Da sauri har ina cin tuntube. Ina wankewa na dawo na bata, kamar wacce ta shekara bata ci komai ba, take sha.

Aikuwa Ammih ta rufe ni da faɗa, inda take cewa.
"Me kika mishi da yake shirin dawowa da wancan matar shi, garin shirmen kin rasa damarki!"

"Devanah!"
Na fada da karfi kirjina na amsawa.
"Oho can miki! Tunda kin zab'i yar daba ce ko dabana oho! Nan muka yi miki fada akan karki sake ki dawo da halin kishi idan kina tare dashi, ya faɗa min kome! Dubeta a ido kamar tana da hankali, amma a zahirance kinfi kowa wauta. Toh yayi miki kyau, dan wancan kafiran ta musulunta, kuma da alamu dawo da ita nan zai yi dan naji yana cewa nan da sati me zuwa. Domin yau ya tafi can zungwagwuwe,"

Hankalin Ummi yana kan Laptop, Amma tana kallon yadda nake zubda hawaye, masu mugun zafi.

Bata min magana ba, ta cigaba da abinda take, daga fada suka dawo yi min nasiha, yaushe kome ya juye haƙa, kamar wanda aka mishi! Kunji ba sabon Kuskurena.

Ban yarda nice na kunnowa kaina rikicin ba, yanzun na fara zargin an mishi wani abu.

Sai da na koma dakin Ummi bayan isha, tana rike da Jikarta tana wasa da ita.
"Mutane irin Sadeeq! Basu son aja musu rai da abinda suke da mallakin shi, kuma basu son titsiye. Taya zaki ce mishi sai ya gaya miki matsayin Devanah!"

Shigowa da abinci Fatimah tayi, tana me son amsar Zarh, mika mata Ummi tayi.

Sannan ta buɗe abincin dan tunda nazo na kasa cin kome sai Kunun tsamiya.

"Lokacin da ya amshi musulunci! Bazai yi zaman shi a kasar ba, kuma garin da kuka tsaya ba garin mutane ba, Sharri aka kula muku a hanyar ku ta dawowa gida, shine Imam Nawaz ya sanya yaran shi suka bude muku, idanu.

Kuka shigo ta alkaryar su, sannan yanayin gurin su, da ruwan da ake ya haifar mishi da tsananin bukatarsa.

Husnah! Abubakar ya amshi musulunci ne sabida rabon takwaran Dadah bawai dan yana son Addinin bane, zuciyarshi babu addinin a cikin sa. Koda ya amshi musuluncin burin shi idan ya same ki, zai dawo addininshi da ya sauka a kai, wannan itace asalin yaudaran da ya shirya miki, amma Allah ba Azzalumin sarki bane, domin yi kuka a wancan dakin da yake Tsakiya duniya. Nayi tawassali da sunayenshi tsarkakka, nayi imani dashi, sai gashi a cikin daren da ya amshi musuluncin, Allah ya shafe mishi tunanin shi akan yaudaran mu da zayi, sabida Allah ya matsi bakin shi ya gayawa Imam Nawaz gaskiya, shi kuma yayi mishi fatan nasara. Domin yasan Allah ne yake shiryawa ba mutum ba.

Shi yasa bai damu ba, ya barshi a wannan daren da ya hadu dake zuwa wayewar garin da zuwan shi sallar asuba wanda yake ganin kamar takuri ne, yaji duk wata burin shi ya ƙare, tun daga nan yake jin ya kamata ya nisance ki, domin kece matsalar shi ta farko!

Kisan sabida me yasa? Sabida kina da zafin kishi. Wanda yake iya rufe miki ido shima ki mishi rashin kunya. Da ya gaya min burin shi, mice na bashi shawaran yazo nan yayi karatun addinin musulunci.

Zuhrah, har yau Kungiyar CAN, zuba mishi kudi take dan ya dawo gare su. Saboda baiwar da Allah yayi Mishi.

Kinsan kuwa idan da zai tsaya yayi taron su na Church, a kauye guda sai duk mutanen cikin kauyen sun bar Musulunci. Da hannun shi yayi ta bada kyaututtukan dan musulmai su bar Musulunci, kuma yayi nasaran hakan, sabida ya iya magana irinta masu hikima!

Kinsan me suke ce mishi a cikin kungiyar su, Man of God! Sabida idan yayi magana sai an saurare shi.

Ranar da ake wunin nan ya gaya min kudirin shi, nason karo ilimi. Nace mishi nan ya dace yazo.

A cikin wannan daren da suka fito. Har sun kai shi airport. Suka dawo.

Ashe daga nan Kaduna suka kai shi, inda suka yita gana mishi azaba. Kamar bazai tashi ba, dake sun san akwai karfe a jikin shi shine suka yita dukar gurin.

Allah yayi yana da nisan kwana, ana yaga Innarki da Baban ki a gurin su.

Sai da ya kwashi sati biyu a hannun su kafin Allah ya kawo musu dauki ta hanyar, Kawo Imam Nawaz, inda sanya wuta a gurin ya hallaka wasu sannan ya fidda su zuwa alkaryan su, kwanan su biyar, suka wuce Zimbabwe. Da Innarki tare dasu Maryam dukkan yan uwanki, suna can. Husnah duk halin da kike ciki mijinki yana sane bai manta dake ba, Husnah kina ja ne da Son da Abubakar yake miki?

Da har zaki yi tunanin kiyi amfani da damarki dan yace yana bukatar ki! Husnah bafa a musulunci ya taso ba, har zaki decided akan ya faɗa miki miye matsayinta! Waye aike ki yanke wannan hukuncin! Toh kin b'allowa kanki ruwa, dan ya biya ta gurinsu Innarku..daga can zai tsaya Devanah....

***nan zasu iya biyan ta wannan acc***

Acct: 0472282105

***Ramlat Abdul Rahman Manga***

***GTBNK*****.....**
200 ***ta bank***
300 ***ta katin mtn domin biyan ta tana ga wannan number zaku turawa***/.+2347035133148👈🏻
***Domin shiga VIP*** 500/ ***ta bank***/600 ***ta katin mtn***....
Yan Niger Republic...
Zaku tuntube wannan number ne +227 84 50 64 76👈🏻
***Idan zaka sayi Kuma Inuwar Gajimare ne*** 200 ***ta bank idan katin mtn*** 300.......
[7/2, 9:17 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BHSY48

Zai dauko matar shi, shawarata dake kiyi hakuri, da halin shi, dan yanzun ya koyi zafin zuciya, wanda ban san taya yake ba, sabida ba a hannuna ya tashi ba.

Na rike ki da koyi hakuri, shima kuma na gaya mishi laifin shi.

Kuka mara sauti nake, jikina sai rawa yaƙe, abu biyu de samtime, is not easy, misery nd rapture, nasai naji baki daya duniyar tayi min fad'i.

Wani irin abu ne ya taso tun daga cikin cikina har zuwa kirjina ya tukare min wuya, hawaye ne yake zuba da mugun gudu.

Tsurawa Yarinyar ido nayi kamarta da ubanta yayi yawa, dan zan iya cewa, har fatarta kalar nashine.

Dukar da kaina nayi, ruwan hawaye na zuba akan fuskarta.
Ina son na bude baki nayi kuka amma na kasa dan abin da yake tokare a kirjina ya hanani kuka, jin digar hawayena yasata bude idonta.

"Kuma Insha Allah! Bazan tab'a bari a cutar dake ba, HUSNAH ina sonki da Mijinki sosai, shi yasa nake gaya miki Kuskuren ki! Shima yaci da zuci. Amma ki dauka ajizanci ne"

Daga haka tafita daga dakin, zama nayi na sussuce, na rasa inda ke min dad'i. Haka kawai nake nazarin rayuwarmu da muyi, uwa uba zamanta babu miji! Shin zata iya rike kanta kamar ni.

Tsoron Allah ne ya kamani, da gudun kar yaje ya dawo da ita tazo min da Bala'i.

Duk sai na kuma rikicewa, na manta mijinta ne ya aure ni, bani bace za a kawo min ita.
....... A hankali na suma ramewa. Ga rikicin da Zar-minah take min wanda rashin ruwan nono ya haifar.

Kwana biyar da tafiyar shi. Ina daki zaune sai ga Dadah.
"Ke! Ni bana son bakin rai, akanki aka fara kishiya da zaki kwazazzabi kanki? Duk kin kare

kamar kudin guziri, dalla matsa can. Ban da zubda haji ake cewa ko aji! Salon dabana tazo tarena ki, Waye ya gaya miki anan wannan kishin bal-bal d'in, billahizi, renaki zata yi.

Dubi wuyarki sai ka sanya wawan loma kacinye. Tsabar damuwa, toh ahir dinki. Ban da jaraba irinta matan yanzun Meye abin kishi, da abinda yafi karfin ki. Dan haka kul na kuma ganin ki a cikin uwar d'aka, me aka yi dabana balle shi sahoramin, sakarya kin zauna kishin miji, zai rakaki lahira.

Toh koda wasa, ban yarda ba, kuma ban amince ba. Muna nan dake zai kwaso uwar kanshi nan kamar tukunyar giyar, yazo Zungure ki, saura ki nuna mishi kiyi misheee yake ko mieesi, kai can muku wannan abinku nan sai ki barni da dan wofi na gyara mishi zama."

Karfi da yaji Dadah ta sanyani ina fitowa, ana hira dani,  ranar da ya cika sati biyu ya kwaso jiki ya dawo da ita, dama ya gayawa su Ummi nice dama babu waya a hannuna bai gaya min ba.

Ina kwance a daki, dan tun safe da naga anata hidimar abinda za a girka, na fahimci gidan da baki, ashe ba shi daya bane, har dasu Muhammad daga Japan da kuma Fa'iz, Sai Siyamah da Sughra da Rafi'q tare da Na'ilah.

Ina kwance na rufe fuskana da hisnul Muslim, shine book dina na biyu, daga Alkur'an sai shi.

Na nutsu sosai ina nazarin shi, har barci ya dauke ni.

Cikin barci naji kamar akwai mutum a kaina, buɗe ido nayi nagan shi rungume da yarshi yana sumbatar goshinta, gyara kwanciyata nayi. Tare da juya musu baya. Ashe wai nan ta shi ya b'aci.
Fuuu ya sauka a gadon tare da barin dakin, ban damu ba na cigaba da Barcina.

Lokacin Sallah ne ya taddani,, ban daki na wuce. Naje nayi wanka tare da saka kayana, na rufe kaina.

Sannan na fito rike da Alqur'ani, zan tafi masalaci, dan na fahimci gidan namu akwai mahaukata da yawa.

Wani ikon Allah, Siyamah da Sughra, har da Rafi'q sunga Bature amma zuciyarsu ya kasa nutsuwa su kira mahaifiyar su, asalima, sai ya zame musu kamar dodo. Domin tsoron shi suke ji.

Ina fitowa naga, yarinyata a dangware a kujeran ga Devanah, tana kallon ta, tana kananun kuka. Hankalinta yana kan wayarta inda take hira da Joe.

Yana tambayar ta ina take, sai zata rubuta mishi tana Makka sai ya kasa.

Sanya hannuna nayi na dauki yarinyar ko kallon bata ishe ni ba, na leka kitchen naga Ummi fuskarta a daure.

"Ummi! Zan tafi masalaci, ina ga sai dare zan dawo."

Sake fuska tayi sannan ta kalle ni tace.
"Toh amma kinci abinci?!"
Sam ban tab'a tsammanin yana kitchen din ba amma naji kamshin turaren shi na zata ko ya shigo ya fita ne, sai muryan shi ce da ta dake ni.

"Ina zata ci! Ta mai dai kowa irinta. Wallahi Ummi ki mata magana, na shiga dakin na sameta tana barci, an ta bude ido ta kalle ni, ta juya min baya."

"Kayi hakuri! Daddyn Zar-minah!"

"Jeki abinki! Allah ya dawo dake lafiya!" Inji Ummi.

"Ummi! Gata nan kiyi mata maganar, ba sai a wuce gurin ba" ya fada tare da lankwasa murya da kai,

"Husnah! Jeki abinki!" Tace min, kasa tafiya nayi, jikina yayi nauyi, kaina a sunkuye.

"Ummi ki gaya mata kawai!"
Ya faɗa a shagwaɓe,
Iska taja sannan tace.
"Kai kake aurenta! Bani ba, sannan da burbushin kimata a idanunta bazan yi sakacin da zai zube ba, Husnah jeki abinki idan ya matso zai gaya miki."

Jikina a sanyayye na fito, ina jin b'acin rai. Wato Sadeeq nice zai wa Horon mgn, ba kome.

Ina fita ta juya a fusace, kamar zata kifa mishi mari, har ta d'aga hannu. Sai ya saka hannun shi biyu ya kare kanshi, sauke hannun tayi ranta na zafi.
"Kaje dakina ina zuwa!"

A tsorace ya fita, kwalla ta maida, sabida tasan tana da zafi. Amma kwana biyu nan zafinta yana kara yawa, kuma ba akan kowa bane, sai akan Husnah bata son taji ko taga abinda zai sakata damuwa, shi yasa ko yayya aka tab'ata akan ta take jin zafi sosai, abinda tasani tun ranar da aka cire takwaran Dadah, take karajin don Yarinyar, dan koda aka yi maganar an sanya mata sunar Dadah taga tsantsan farin ciki  a idanunta, taga kunya da kawaici. Taga tsantsar tarbiya da hakuri, tare da sadaukarwa, wanda tayi imani da wata ce, da sai anyi karamin yankin duniya.

Shi yasa daga ita har mutanen gidan suke matukar girmama Husnah, domin ta nuna musu ita yace, babu inda zaka ce ta cika dari, sabida babu wanda aka haifa da iyawa, abinda ya sani Husnah na cikin jerin mata masu zafin kishi, wanda take tsoron kar haka yasa Devanah ta sami logonta.

Tana gama kad'a miyar, ta rufe ganin Siyamah tana rab'e,² yaɗata ce mata.
"Bana son kinibibi, meye kike rab'e."

Kuka yarinyar tasaka, har tana jan majina tace.
"Ummi! Wallahi bani da lafiya! Kuma na kasa zuwa asibiti am scare, kar naje su ce min, ina da ciki ne!"

Kuka ne ya kwace mata.
"Kema jeki dakin ku! Idan Husnah ta dawo zata duba ki!"

Haka yarinyar tafita, har zata yi nisa ta kira sunanta da sauri ta dawo.
"Me yasa baki gayawa Mamie kuba?!"
Kurawa Ummi Ido tayi hawaye na zubo Mata tace.
"She don't care, for us! Ita kudi Kawai take nima."

"Jeki!" Ummi ta faɗa tare da jinjina kai.

Devanah tana zaune a gurin tare da Na'ilah da Sughra, suna kallon wani fim,. Ummi tazo ta wuce su. Shekeke suka bita da kallo.

Bata bi takansu ba, dan ita bata damu dasu ba. Tunaninta Sadeeq da yake daki.
Tana shiga ta same Shi Yana sallah, ban daki ta shiga tayi alola tana fitowa yana idarwa, kujera dress mirror ya dauka yana kallonta,. Har ta idar sannan ta cigaba da addu'a. Tana shafawa ya shafa.

Zuba mishi ido tayi kafin tace.
"Kana nufin Husnah ta zauna a nan kai ka zauna da matar ka a can? Sannan dan rashin kunya nice zan gaya mata ba kai ba, dan haka ishashe ko? Ni bazan gaya mata ba, sannan idan zaka tafi ka dauki matar ka da Yarka kuyi tafiyarki, sannan ka dauko Kirista ka kawota har maka, ita da ba tsarki ne da ita ba, Anya kana da lissafi, koda yake na maka uzuri. Tunda baka gama sanin akan addininmu ba.

Sannan kuma ka gaya mata a nan matuƙar kace zaka yi gangancin fita irinta rashin hankali zasu sanyata a jirgi ta kaita inda suka yi niyya, kuma wallahi na samu wata matsala daga gare ka ko ita wannan din wallahi sai ka rabu da ita."

Nan tayi ta Bala'i kamar zata cinye shi da fada.
....

A falon kuwa Dadah ce tafito tana niman me buɗe mata wani dan kwalbar man zafi, wani kallon banza tayi musu, dake Allah ya daura musu tsoron Dadah, take suka shiga zare ido.

"Uban me kuke anan?, dama kunzo Makka hutawa ne? Toh maza ku fice min zuwa masallacin. Gayyar na aye, gayyar arna a ido, maza kufita."

Cikin tsoro Devanah tace.
"Good day Gran mah"

Zuba mata ido tayi tana gyad'a kai sai kace kadangariya.

"Ai dole! Kice min gundai! Garan ma,,,,, wato wani salon cin mutuncin dan adam ne, ko? Yar banza da fuska kamar kosan manja, Moddibo ma sai naci mutuncin shi balle ke! Sha-sha-sha, arniyar wofi.

Da shegen jiki kamar an watsawa, burodi ruwan zafi.

Mijinki ma dan kaniyar shi ba zan kyale shi ba, dan banza. Balle ke Yar wofi Kanwar Paparoma, shima naci uwa tai, dani kuke zance ba dai kin dibo jiki kamar an zubawa alade ruwan zafi ba, toh naji ko na gani Huzna ta kawo karanku, sai na hada har da Moddibo da Zuhrah tare da, shima sakaran naci mutumcinku la'ada a waje,.

Yar wofi duk ta cika mana gida da warin nakasa, toh Kubura! Wallahi sai an wanke gidan nan domin Ni bazan zauna a kujeran da jikar masu fitsari a tsaye ta zauna ba, kuma ko cokalin gidan nan tab'a idan zaku wanke a wanke sau bakwai, tare da wankan tsarki. Shima kujeran ayi mishi wankewa bakwai tare da wankan tsarki."

Ganin mutanen gidan sunyi cirko cirko, suna kallon yadda Devanah take kuka, ya kara b'atawa B rai duk sabida ni ake cin mishi fuska da matar shi.

"Kai! Uwa ka, maza ce min Nagode" shiru tayi ta juya ga Moddibo, tace..
"Idan baka son b'acin rai na, maza kace ya faɗa min nagode"

Cike da takaicin abinda Sadeeq din yake yi, Ummi ta dube shi.
"Sabida bamu isa da kai ba? Sabida ka rena mu ko? Dadah zage ni, kuma zan ce na...."

"Nagode sosai! Allah ya huci zuciyarki!"
Murmushi tayi sannan tace.
"Ko kai fa! Ai nan duniya bani da sama da kai, ku kuma lafiya kuke zaro mana idanu, kamar kunga abin mamaki, jika na ne, kuma ya bani hakuri sai na cigaba da gaba dashi, ni fa Kubura

da Zuhrah bana son sa'ido da munafunci..."

Kafin a kamo sunan Abba ya juya Abinshi.......

***nan zasu iya biyan ta wannan acc***

Acct: 0472282105
***Ramlat Abdul Rahman Manga***
***GTBNK*****.....**
200 ***ta bank***
300 ***ta katin mtn domin biyan ta tana ga wannan number zaku turawa***/.+2347035133148👈🏻
***Domin shiga VIP*** 500/ ***ta bank***/600 ***ta katin mtn***....
Yan Niger Republic...
Zaku tuntube wannan number ne +227 84 50 64 76👈🏻
***Idan zaka sayi Kuma Inuwar Gajimare ne*** 200 ***ta bank idan katin mtn*** 300.......
[7/2, 9:19 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BHSY50

"Saketa dan uwaka! Saketa ko naci mutuncika! Dan wofi mutumin banza"

Janye hannun shi yayi daga jikina, ya zuba mana ido, haka Dadah tazo ta fincike ni, tana murguda mishi baki.

Hawayen da ya ciko mishi idanu ya shanye, tare da kwafa. Kamar zai iya ɗaukar mataki.
"Ko za a dauki mataki ne? Ubana? Da shegen idanu kamar na y'ay'an matsatsaku!"

Yana ji yana gani Dadah tayi wuf dani, tare da ja mishi dogon tsaki.

Kullewa yayi da bakin ciki, a ranshi yace.
"Zan je aiki! Fitinanniyar tsohuwa kawai."

Iya bakin ciki yaji shi, bai iya hakuri ba. Ya biyo mu, har waje, nan Dada ta tsare ni, da ido wai kar na mishi murmushi, duk salon jan hankali taki barina nayi ko idan ya zuba min ido na kula shi.

Addu'a Abba yayi mana, yana rungume da Zar-minah. Amsar yar yayi tare da barin gurin, ya kalle ni da ido, gurin motar Safa da ta kawo shi yaje ya hau.
Shiru kowa yayi tare da zuba min ido, ban damu ba na zauna a cikin motar da zai kai mu, airport.
"Husnah! Ki gaida Innarki! Insha Allah muna nan zuwa!" Mai da kwallar nayi, sannan na gyad'a kai na.

Domin kuka zanyi, zama nayi cikin motar Fatimah da Maryam suka shiga kusa dani, sannan Dadah ta shigo bayan ta gama zubawa Ummi da Abba kashedin.

"Wallahi ku ja mishi kunne, zan rakata aryapo, matukar bai kai yar can ba, zai ga tijara a garin Makka, nifa ina d'aga mishi kafa shine zai raina ni. Sabida ina garin fiyayyen halitta shi yasa nake share shi. Idan ya kuskura raina ya b'aci sai naci mutuncin kowa ba iya shiba, da kanshi kamar faranti. Kai kuma me sudadden kai muje, anyi magana ka sanyawa mutane dariya"
Ta juya kan Fa'iz da zai ja motar.

......
Haka muka bari gidan Dadah bata bar kowa ba, har muka isa, a gurin da zamu shiga cikin arrive muka hadu dashi.

Shigewa ciki muka yi, riko hannuna yayi.
"Me kike nufi da ni? Meye nayi miki da zafi haka? Toh wallahi kwana biyar zak.."

"Bata yi kwana biyar din ba , wallahi ka fita idanuna, ko kuma na zabga maka mari. Wuce ke kuma, bani yarinyar tun ban tara maka jama'a ba."

Mika min yarinyar, na ansheta da sauri, har ina sauke ajiyar zuciya.

"Sorry!" Ya furta min a hankali, sannan ya juya ya bar Airport ɗin.
Kasa tafiya nayi, ina kallon bayan shi.

"Ke dalla can! Muje ko jirgi ya tafi ya barki. Indai wancan me kwalelen kan nan, rankwal-rankwal."

Haka muka bar garin cike da kewar juna.

Mu hudu muka tafi, kwancan.
Cikin murna da farin ciki, Dadah ta isa gida, tana basu labarin irin wulakancin da tayiwa Sadeeq.

---
Alhamdulillah! Mun isa karfe takwas na dare. Mubarak da Abdul suka zo daukarmu!

Rasa bakin maganar yi nayi, ga kanena. Sai kuka har muka isa gida, ina ganin Innarmu kuwa.
Kuka na ya tsananta, karb'an Zar-minah suka yi, aka shiga kallonta.

Dakin Mubarak aka kai Fa'iz, Fatimah da Aminah d'akin Maryama, dare yayi dan mun gaji, abinci aka kai musu. Ni kam tunda na zauna. Saka Innarmu nayi a gaba ina kuka na kasa yin komai.

Mika min Yarinyar tayi na fara feeding ɗinta, har Tayi barci. Sannan na kwantar da ita.

Nuna min ban daki tayi naje nayi wanka da alola, na dawo nayi sallah.
Ina idarwa, ta ajiye min abincin. Kasa ci nayi sannan na zubawa Luluh ido wacce tazo ta sumbaci kumatun Zar-minah.

Sannan tace min..
"Addarmu, sai da safe."

"Allah ya tashe mu!"
Na fada mata,.
"Ina bazan iya cin abinci ba, nayi mamakin yadda kuka yi nisan kwana. Bayan gidan ya kone!"

Gyara zama tayi sannan ta fara bani labarin abinda ya faru.
.....
,"A ranar da kuka tafi gidan Yakumbo Salmah, sai Baban ku ya fita zuwa cikin gidan, duba jikin Yawale. Yana shiga sai muka ji karar motocci, tunda suka shigo garin kofar gidan mu suka tsaya, nan suka tara mutane wai su fito ke. Aka shigo kiranki baki nan sai nice da Ghaddafi.

Shi ya fita Ni kuma ina cikin gidan.

Aikuwa suka rufe shi da duka, abinda ya fidda babanku daga cikin gida shima aka hada da shi, sannan suka fito dani, aka jefani cikin motar, suka kuma kina gidan, tare da yiwa mutane gargad'in.

Sunyi tafiya me nisa damu, kafin aka sauke mu aka kuma saka mu a cikin wata mota, daga nan sai tsintar kanmu mukayi a wani gida.

Munsha wahala sosai. Watan mu biyu, Allah ya kawo Baban Aminatu ya fidda mu. Tunda na fito nayita jinya a nan kasar. Daga baya kawai Babanku yace yafi son zaman nan ma Kawai.

Daga baya aka kawo su Mubarak da Abdul tare dasu Maryam.

Alhamdulillah! Domin babu abinda muka rasa gashi Baban ku yana sana'ar shi dai-dai gwargwado.

Da fatan Kema kina lafiya.
Kaina a sunkuye na fara bata labarin irin wuyar da nasha tare da, halin da nake ciki. Wanda Ummi ta gaya mata, matsalata.

Shiru tayi sannan tace min.
"Kwanta! Idan Allah ya kai mu zamu tattauna akai, amma mijinki mutumin kirki ne. Kiyi hakuri dashi."

Munyi hirar kamar ba gobe, kafin barci ya dauke ni, sabida Babanmu bai dawo ba.

---

"Tarewa sahorami fa! Dube shi da wata uwar kafada kaman an sanyawa Katako riga, Yaro kayi sake domin wannan karon sai dai ka Zungure dabana ba dai, Yar halal ba, mara mutumci."..

Bai kulata ba ya gaida Ummi da Ammih, dabana tana gefen shi.
"Good....."
"Ke dalla can! Gundai kaniyarki sabo da zagin mutane wani sabon feleke kika samu, Mangofak din ma yaci kaniyar shi. Yar banza da fuska kamar an murje taliya, kuma wallahi ka kuma kawo mana ita gidan nan sai na zabga maka mari, Dan bazan lamunta ba. Kullum sai an yayyafa ruwa sabida rashin tsarki"

Ita kam Devanah komawa jikin mijinta tayi tare da makale shi, dan bata saba ganin fada ba, kuma Allah ya gani tsoron Dadah take ji.

Idan ran Sadeeq yayi dubu sai da Dadah ta b'ata mishi su, kuma ta shiga gaya mishi magana, tare da ce mishi ai shi yayi asarar mace, wannan fuskarta kamar an taka burodi.

Nan ta gama kwashewa Dabana albarka, inda tace mishi.
"Kayi a hankali! Tunda dai tace zata musulunta gwara ta musulunta in ba haka ba......hmm"

Abincin Ummi ta kira Siyamah ta jera musu, yaja hannunta suka tafi cin abincin, a hankali take ci, tana gyad'a kai. Suna gama ci mike tare da tattara kwaninka.

Dai-dai fitowar Dadah daga d'akinta tace.
"Kee Dabana!"
Yadda yadda daka mata tsawa, aikuwa ta sake kwanikan a kasa sai jin tarrssss.

Tsaki Dadah tayi sannan tace..
"Aikin banza! Toh ai bakin san zafin kudin ba ina zaki iya, Ke Zuhrah, gashi maza kira min Ikilimah."

Karb'an wayar Ummi tayi, sannan ta fara niman layin aikuwa aka ce mata User busy!

"Dadah suna tace min User busy!"

Baki tayi cikin mamaki, tace.
"Shi wisabisi din Waye shi haka da bazai barni nayi waya da autana ba!"

Dukda ran shi a b'ace yake sai da ya d'ago tare da zuba mata ido, kafin yace.
"Hmm! Ai shi din wisabisi."
Shiru yayi yana kallon fuskarta, ganin yadda tashin hankali ya bayyana a fuskar ta.
"Toh lalata kunne yake!"

"Mtseew! Nazata wani abun tashin hankali ne! You Allah na tuba ai mun sha ruwa, tunda gashi nan naga jikar Zuhrah da Moddibo, tunda naga na sauran abokan wasanka, ai kome ya kare."

Shiru yayi yana mamakin ta, ya zata, zai ga tsoron mutuwa ne a fuskar ta. Sai yaga sam babu hakan.

Kamar tasan abinda yake tunani kenan, tace mishi.
"Ka zata zan tsorata ne?  Toh wallahi bari kaji, Ni nan an tab'a barina da tsohon cikin Kanwar Ubanka, kuma nahaihu nabi bayan su, ka zata ni Fulanin bogi ce? Ni nan Fulanin tashi ce."

Shiru tayi tana kuma mikawa Ummi wayar.
Tun daga ranar, suka fara shiri sama sama, bashi zai hana ta sille shi idan yayi mata laifi ba, ta kuma bishi da gori ba.

Tsakaninta da Devanah babu shiri dan k'iyayyar gaskiya take nuna mata.

----

Washi gari kuwa Fa'iz da Aminah da kuma Fatimah suka dawo, na cigaba da samon kulawa daga iyayena, sai dai kishin mijina ya hanani gaba, domin gani a gaban Innarmu, amma abin takaici bana wani kara gaba, sai da ranar ta fito min a mutum, sannan na rage zafin kishi, zai kira wayar maryam suyi video call, dan yaga yar shi amma ni ko muryana yaki zai datse kiran, (🤷🏾‍♂️🤔 Chakwakiyya! Wannan book din na kudine)

Tunda na fahimci da nice baya son magana ta hadani dashi tuni na yafe shi na watsar, idan na gadama suna wayar yana kallon yar zan dauke ta, kuma na hana kowa gayawa Innarmu, bai tab'a zata zan mishi horon haka ba, yazata lokacin da nake kuka yayi min magana ne, yanzun Wallahi na fi karfin nan, tuni na watsa shi a kwandon share.

---

A bangar shi da Devanah kuwa, matsalar ta ya hana shi sauke nauyin ta, dukda yana yi amma ba sosai ba. Karshe idan ya gama shi ya tashi zuciyarshi kamar zata fito sabida amai ita kuma duk ya yagata, Dan jikinta tsagewa yake, illar Infection kenan, tayi mata mugun kamu.

Gashi jarababbe, tunda yayi wanka, ya bude laptop din shi ya fara bincike akan wani irin ciwo ne! Karku manta ilimin kimiyya ce dashi.

Lokacin da yaga dalilin da yake janyo cutar sanyi yayi mamaki, Nan tashi yaje dakin nan ya sameta tana susa har da hannu bibbiyu. Kamar mahaukaciya, a ranta kuwa zagin Joe tare da tsine masa yafi sau dubu.

Dakyar da ita yayi, ya tasata a gaba har ban daki, tayi sitbath. Sosai sannan ya sanyata tayi

wanka, a ranar suka bar Makka zuwa jidda.

Ya kashe kudi sosai lokacin da aka gaya mishi ciwon ta rabe shi, amma zai iya kasheta da wuri dan matsalarta toshe mishi gaba zata yi, ko kuma tashafi gurin kwayoyin halittar jikinsa.

Kuma abin damuwar, shine ciwon zata iya harban wani, tsoron shi kar Husnah ta dauka, gashi garin abinda bai kai ayi rigima ba, ya sayo ciwo da hannun shi ya dibo damuwar da tafi karfin shi, dan yayi Imani da Husnah ce, bazata tab'a barin ya kusanceta.

Haka suka amshi magani ba allurai, shiru yayi ya zuba mata ido.

Har suka dawo maka washi gari, ya suka fara zuwa ana musu alluran.
Sai dai dake akwai mugun manufa, a ranta. Alluran kawai nake amsa bata shan maganin da kuma wanda zata cusa a gabanta, kuma ba karamin kudi ya kashe ba.

Arne kenan! Ai idan bata yi hakan ba ai bata cika arniyar ba, domin bakin cikin yin sallar shi take, kuma a hakan da suke zaune tayi alkawarin sai ta dawo dashi kan hanyar da ya sauka....
***nan zasu iya biyan ta wannan acc***

Acct: 0472282105
***Ramlat Abdul Rahman Manga***
***GTBNK*****.....**
200 ***ta bank***
300 ***ta katin mtn domin biyan ta tana ga wannan number zaku turawa***/.+2347035133148👈🏻
***Domin shiga VIP*** 500/ ***ta bank***/600 ***ta katin mtn***....
Yan Niger Republic...
Zaku tuntube wannan number ne +227 84 50 64 76👈🏻
***Idan zaka sayi Kuma Inuwar Gajimare ne*** 200 ***ta bank idan katin mtn*** 300.......
[7/2, 9:19 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BHSY49

Sannan hannun tayi a habbarta cikin son kara mishi haushi tace.
"Yanzun don Allah meye laifin Huznah! Da kaje ka kwaso jajja amaren!"

Dake Hausar da yake ji bata wani nuna ba, sai ya kuma kulewa. Har yaja hannun Devanah zai fita.
"Meye matsayin Husnah? Tunda itama haka tayi maka tambayar Matsayin Devanah kake fushi?!"

Juyowa yayi tare da sunkuyar da kai yace..
"Mata tace!"

"Toh yayi kyau! Zata gurin Iyayenta! Itama kaima sai kaji dadin ka"

Da sauri ya d'ago kai, Ummi ta kuwa bone Fuska tace.
"Kasan ni ba sa'arka bace! Dan haka zata gurin iyayenta, tunda Fa'iz ya san inda suke zai kaita."

"Ummi!!"
Ya kira sunanta a kage! Harar shi tayi, sannan ta cigaba da abinda take a kallon,

Haka ya fita ranshi a jagule, shi bazai yarda da wannan abin ba, dan bai shirya musu tafiya zimbabwe ba, kuma Allah ya gani yar shi yake bege.

Suna isa gidan, wanda aka mishi gyara na musamman, nunawa Devanah d'akinta yayi, sannan ya shiga dakin shi. Ban daki ya shiga, ya bude ko ina.

Cire kayan jikin shi yayi sannan, ya sake ruwan, kewar Husnah ce take azazzalar shi, amma fushin da ya daurawa zuciyarshi, yaki fahimtar kome!

Gani yake ai yayi mata gargad'i, akan maganar Devanah. Toh ina ruwanta da zata tambaye shi.

_Husnah bata da laifi! Kowacce mace abinda zata aikata kenan! Tunda addinin ku ba daya ba da Devanah! Sannan koda kake fushi da ita! Ai ta gama da kai, ko kamanta Uwar Yar da kake so ne! Kasassanta da Husnah shine masalaha_
Kalaman Ummin shi ce! Yake dawo mishi.

Haka yayi wankan ya fito, saka kananun kaya yayi, sannan ya karaso ya zubawa Devanah ido, wacce take zaune.
"Baki yi wanka ba?!"
Tashi tayi zuwa ban dakinta, tayi wanka, tun da taga akwai ruwa zafi, ta dawo d'akinta. Ta dauki gishiri da maganin da take sawa a gabanta sabida kaikayi da yake mata, ta shiga wankewa.

Kamar zata yi hauka, sabida gaban ta, kuraje yayi sosai shi yasa idan tazo wankewa. Take yi kaman zata yi hauka.

Tana gamawa ta shafa maganin, sannan ta fito ta saka, wandonta. Bayan ta gyara jikinta, wajen sai zafi yake mata, amma tayi kamar bata jin kome.

......
Tunda na tafi masalaci, a hanya muka hadu da Muh'd, ya dauki Babyn Zar-minah, bayan munyi sallah, muka wucce dauwafi.

A ka'aba na jima ina kuka, tare da niman sulhu da mijina, kishinsa na kara samun mazauni a raina da zuciyata, bamu dawo gida ba, sai bayan sallah isha.

Tun da muka dawo naga baya gidan, dakin Ummi na wuce, ina shiga Aminah na kawo min Abincin kuma ta dauko yar, ta shiga ban dakinta sauya mata pampes, ta mata wanka.

Tana kawo min ita har tayi barci, sanya mata kayan barci tayi da sabon pampes, ta gyara mata kwanciya, tare da mata addu'o'in, sannan tace.

"Aunty nagama!" Murmushi nayi sannan nace.
"Kina nuna sonka! Kin mata wanka ni kin manta dani"

Rufe fuskarta tayi ta fece da sauri tana dariya, shigowar Ummi ya sani d'ago kaina,

" Idan kin gama! Ki hada kayanku! Gobe Insha Allah,  zaki zimbabwe."

Kallon ta nayi na wasu lokutan, fuskana dauke da mamaki tare da tsoro! "Kar dai Daddyn Zar-minah sake Ni yayi"

Tambayar da nake da yakinin a zuciyata nayi sai jin Ummi nayi tace.
"Bai sake ki ba, sai dai bai san darajar ki bane,  idan kika yi nisa. Zai nime ki da kafarshi"

Gyada kai nayi, tare da tsame hannuna, sannan na nufi ban daki. Wanke hannu nayi sannan nafi.

Zama nayi ina me dafe kaina, sabida nasan yanzun yana can yana fama da matar shi.

Haurawa gadon nayi ko canza kayana ban yi na, wutar dakin na kashe sannan na zauna ina kallon hasken farin wata.

Kishin mijina ne da tsananin bukatarsa tare da kaunar shi yake damuna, ban san iya adadin lokutan da na bata ba. Amma na tsinci kaina da son gayawa Allah kuka na.

Dan haka na shiga ban daki nayi alola, nazo na fara gabatar da sallar nafilla.

Tun da na fara har kusan karfe biyu sannan nan idar. Addu'o'in nayi Sosai, kafin na tashi zuwa ban daki.

Nayi wanka tare da sauya kayana, na kwanta da asuba. Na hada kayan mu tas, sannan na koma na Kwanta.

Shigowarta ya sani, tashi zaune.
"Ummi Ina kwana? Ya kwanan baki"

"Alhamdulillah! Kun shirya?" Ta tambaye ni a kage,

"Eh mun shirya! Sai dai Zar-minah ce take barci,!" Na bata amsa.

"Toh ba damuwa a barta zuwa lokacin da zata tashi "
Ta faɗa tare da barin dakin.

A gurguje na shiga nayi wanka nazo na shirya cikin, atamfar English. Orange color.

....... Karfe bakwai na daga ta daga barci naje nayi mata wanka.

Muna fitowa na zauna na bata nono sannan na shiryata tsaf, har ta koma barcin.

Abinci Fatimah ta kawo min, fuskarta kamar gonar audigan, tace.
"Aunty Hussy! Muna zamu raka ki, inji Ummi."

Murmushi nayi, sannan na cigaba da kitsawa, ina saka rai kafin nabar saudiya bawan Allah nan yazo.

Amma har na kusan gama cin abinci bai zo ba. Bana sonu rabu hakan, atleast ya kamata mu fahimci juna. Amma bai zo ba.

---

A can kuwa, jiya sun turmushe juna, sai dai matsalar da aka samu. Ciwonta yana fidda ruwa me wari, wanda ya kusan san ya shi amai. Dame ya rabu da ita.

Tare da nufar ban daki, yayi aman sosai, sannan ya duba, jakadiyar shi, a nan yaga yadda ya b'aci da jini tare da wasu irin ruwa kamar tumbudi.

Wanka yayi tare da saka jikin shi a cikin ruwan zafi, sannan ya fito, tsareta yayi da ido.
Kafin ya jefa mata tambaya.
"Dama baki da lafiya ne? Meke damunki?"

Cikin damuwa ta zauna sannan ta shiga matsar kwalla, tana fadin.
"Tun ranar da muka dawo daga Yola,  nake tunanin na gaya maka, domin anyi min evil charms, sabida kai shi yasa kayi nisa gashi ni da zan maka addu'a, nima bani da lafiya."

Shiru yayi ta cigaba da gaya mishi irin faraku da aka masu tare da shiga tsakanin su da aka yi, tayi mishi bayani tare da kuka sosai.

Ya tambaye ta waye ne yayi musu wankar kauna haka, amma fir taki faɗa, wai tana gudun tadda husuma.

Har gari ya waye, yana makale da ita.
...... Idanuna akan agogon dakin, jikina yana kara sanyi da gaske, Nooruz zaman bazai zo ba, kwallar bakin ciki ne suka taru a idanuna.

Har muka fito, aka kaiwa Abba Zar-minah, sannan nima na shiga. Ina shiga na samu yabawa jikar shi addu'o'in, kunnen dama da hagu, yana gama mata ya sumbaci goshinta, sannan ya rungume ta, yana kallon Ummi da Ammih. Dan dama kullum idan gari yawaye za a kai mishi ita.

Yana matuƙa son Jikar shin, kallona yayi sannan ya mai da idanun shi kan Ummi, yace.
"Ki kira min mijinta! Dan nasan ko sallama basu yi ba"

Tsaki Ummi tayi dan ita bata son mu hadu, tsaf mara kirki zai iya rusa mata kome.

Can ya kira shi har wayar ta tsinke, sai a karo na biyu.
Devanah ta dauka, sabida ya saka First love.
"Toh mayya! Sai a barni nima na same Kan mijina, kuma na gaya miki mark my words, kin rabu dashi kenan, domin bazai kuma rayuwa dake ba, shegiyar Yarki da kika kawo mishi sai God yayi punish you!"

"Young lady! Ummin shi ce ba. Husnah bace."

A tsorace ta kashe wayar tare da zuwa kitchen ta kalle shi yadda yake musu abin karyawa, wanda tasan al'adar su ce, har namiji ana koya mishi girki.

Bayan shi taje ta runguma, tana murmushi tace.
"Good morning! Honey"
"Good morning! Mahn...! Ohh Devanah ya kike!"

Sama sama, suke hira wanda duk labarin Yar shi ce, bata gaya mishi an kira shi ba, har ya gama tare da komawa daki nan yaga wayar shi tayi haske, yana dubawa yaga.

Hero.
Kiran na kuma shigowa, ya dauka, cikin biyayya yace.
"Good Morning! Sir? Yasu First love? Da Zar-minah"

"Morning! Sadauki, Amma ka manta yau iyalinka zasu zimbabwe?!"

Ai bai san lokacin da yace .
"What!!? Yau?!"
Kashe kiran yayi, tare da barin gurin da sauri.
......
Tunda muka fito daga dakin Abba nake danne kuka na, sabida daga wayar da Ummi tayi d'azun AM sure yana tare da Devanah, rike kafaduna Ammih tayi, na sake kukan da ya tsaya min a rai.

"Ammih! Laifine dan na tambayi matsayin matar da bata musulunci, meye laifina dan naso sanin darajar ta, shine Nooruz zaman yake hukuntani da haka. Inshallah idan na tafi bani kuma dawowa. Yasha zaman shi da matar shine."

"Auu! Dama har yau kina rike da abinda dan kwafa da tokare yayi miki, yar banza me zubin buzayen. Sai me? Lallai aiki ya tadda meye namiji baka nuna min shi ka mutu akan shi ba, ya banka maka barkonon wulakanci, tare da yajin tijara.

Maza kashe kanki yar banza mara zuciya, ina dalili. Zaki addabi rayuwarki da wancan galafirin, Wallahi Huzna kin rako mata ne, meye na kuka."

Mtseew taja dogon tsaki kafin ta kuma cigaba da cewa.
"Aikin banza zani ya mutu! Ya bar duwawu! Maza zauna. Autan maza yazo ya rarrashi ki, sai ki tafi ganin gida, Sakarya me aka yi akayi Jauro da Dabana take."

Fada Dadah take kamar zata aro wani baƙin tayi fada sosai kafin kuma ta daura min nasiha, muna cikin haka ya shigo, sai muzurai yake.
"Ke dube ni! Da izinin waye zaki zimbabwe!"
Sabida nasan tsaf idan na kalle shi bazan iya bin maganar Ummi ba, ya sani sunkuyar da kai na kasa.

"Ba tambayarki nake ba"
Ya kuma daka min tsawa.
"Eh wallahi, gwara ka mata haka, dan talaka bai iya samun gur."
Juyawa yayi, kan Na'ilah wacce ba ita ta kar zomon ba, amma ta sami kyautar marin da ya fasa mata baki.

Nayi imani da Allah nice, yaso yiwa haka Allah ya maida kanta, dan naga gani-ganin da take min ya fara yawa, kanta yayi tare da turata kofar gida.

Ya dawo kaina.
Zai hauni da masifa, Dadah tace.
"Kai Ubanka! Dan banza damamme, Uban waye ya saka dawowa da Dabana, dan Ubanka yau zata ganin Iyayenta sai dai ka mutum, kafiri me kishin Bala'i daga kai har ita halinku daya, kishi mara dalili, kuma sai taje.
Zungwagwuwen dan Ubanka ka jima karfen dake zuciyarka bata buga ba, kai Jauro na rantse da Allah zan sanya kafar wando daya da kai.

Tafiya kuma kamar tayi, ka zata kowacce mace tauraruwa ce, sha-sha-sha. Iya juya dube fuskar ka, wanda ya samu farin ciki, babu bakin cikin da yake sauka akan fuskar shi.

Kuma Huzna tayi maka nisa, kema tashi maza, domin har dami ayin rakiyar, domin yanzun muna zamanin kifinatin, sai a iya turawa hanya a sunkuce ki, Tunda anyi haukar kishi bal-bal

baki kula ba."

Daga Ummi har Abba da Ammih babu wanda yayi magana, domin kurar Hajiya Dadah ya isa, haka suka fitar min da kaya, kowa yafita ina zaune a gurin, tashi nayi nazo gaban shi, na riko hannun shi.

Sannan na sumbaci, hannun a hankali na zare daga cikin nashi zan tafi, riko hannuna yayi ban juya ba, amma hawaye na. Suna kara tsannanta zuba.

Kirjinshi ya dawo dani.
"My heart is beating for you! Asmeeh! Me yasa zaki tafi! Munyi dake haka ne! Ko nace miki bazan iya zama dake ne, wallahi bazan iya..."

"Toh! A sarin fage fallin daki, ka gama mata masifa ka kwakukumeta, zaka saketa ko sai na sami fuskarka na dalla maka mari........

Dadah😂🤣😆

***nan zasu iya biyan ta wannan acc***

Acct: 0472282105
***Ramlat Abdul Rahman Manga***
***GTBNK*****.....**
200 ***ta bank***
300 ***ta katin mtn domin biyan ta tana ga wannan number zaku turawa***/.+2347035133148👈🏻
***Domin shiga VIP*** 500/ ***ta bank***/600 ***ta katin mtn***....
Yan Niger Republic...
Zaku tuntube wannan number ne +227 84 50 64 76👈🏻
***Idan zaka sayi Kuma Inuwar Gajimare ne*** 200 ***ta bank idan katin mtn*** 300.......
[7/2, 9:19 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BHSY51

Bayan ta mai dashi addinin da ta baro, ta kuma sanya shi ya wulakantani, fiye da yadda ya wulakanta ta, da danginta.

Babban burinta bai tsaya a nan ba, abinda take bukata nan gaba. Zar-minah burinta akan Zar-minah kawai zata yi aikinta, sannan kafin nan sai ta haddasa musu Muguwar rashin fahimta, sannan ta hanashi zaman lafiya.

Yadda Husnah sai tayi danasanin rayuwarta da Bature.

Ko nawa zai kashe bazata sha maganin ba, domin bata da niyyar samun lafiya, sai ta haddasa musu wutar gaba. Hmm BAHAUSHIYAH! Ta aure mata mijin da take so, zaki ga baki da wayo.

---

Muna cikin farin ciki sosai, musamman idan naga yadda ake daukar Zar-minah, kowa son yarinyar yake, idan muka fita cikin birnin Harare domin ganin yadda garin yaƙe, toh sai mun sami mutanen da zasu dauki yarinyar ko ayita daukarta hoto,

Haka zamu dawo gida da kyauttatar mutane, a cikin wannan yanayin Muka fita. Mun dawo kenan muka hadu da wasu, zasu wuce, shine suka dauki hoton mu, dayan ya dauki yar Maryam ta dauke su, har nima na dan fito cikin su.

Ban san ya akayi Maryam ta daura a Status ba, ko waye a cikin kanena ya daura. Kawai sai ga Wayar shi, ya kirani ta wayar maryam, kawai mutumin nan ya shiga gaya min magana.

Kasa nayi da muryana, sannan nace mishi.

"Luk! Nifa ba wayata kayi ba! Dan kaga hoto shine zaka fara cewa da wani dan iskan nayi hoto dashi, na barshi ya dauki yarka. Hhh B kenan, Nagode. Sai dai wannan ya zama kashedin da kai na karshe idan ka kuma gaya min maganar banza, zan maka abinda. Sai ya dame ka, kuma da kake magana akan aurenka ake yawo dashi, har ana daukar hoto da Yarka baka yafe ba, toh nagode sai dai ka sani, abinda ya faru dani ma, Qaddara ce.

Allah sai ya saka min, kuma kaje ka cigaba da min kallon mara kamun kai. Wanda bai san inda ke mishi ciwo ba."

Daga haka na kuma kashe wayar na cigaba da abinda nake. Wai Nice B yake zargi har da cewa idan zanyi Iskancina bada igiyar aurenshi ba.

Sabida ya same ni, a fanko. Wani ya dauke mishi abinda yake tsammanin. Dan haka nayi fushi sosai, wanda ya shafi yar dan kuka tayi kamar zata tsaga gidan, har Innarmu tayi magana, sannan na bata nono.

Ya zata wasa ne, sai da muka dauki sati biyu dama ba waya muke bazan idan ya kira a dame shi hoton yar shi, na hanata. Kira yayi zai gaya min magana, Ni dakatar dashi.

"Wallahi baka isa ka gaya min abinda yayi maka ba, akan me yarinya ce bazan bada a dauka ba, idan ka isa kazo da kanka. Kuma har kana da bakin ce min ba zuwa nayi da ita ba, kai din zuwa kayi da ita, ka kuma gaya min maganar banza zan rama."

"Shi yasa Devanah ta fiki, bata tab'a min rashin kunyar da kike min ba, Nagode da kika nuna min halinki, mara kunya."

"Au! Arniyar matar ka kake magana akai toh ni ina Ruwana, ba Devanah ba, ko Devil ce babu abinda ya dame ni sabida kai ne ka damu da ita ni bata gabana."

"Arniyar! Arniyar!! Arniyar!!!  Kika kira ta?!"
Ya jefo min tambaya, cikin gatse nace.
"Eh! Arniyar dai me? Akwai abinda zaka yi? Ok zaka iya sake ni sabida na kirata arniyar."

Da nasan abinda zai gaya min da ban kula shi ba, na kashe wayar, baki daya.

"Yes ita arniya ce! Sai dai nayi imani ko a cikin Yan matan Hausawa baza a samu macen da takai shekara talatin da Virgin dinta ba, wasu a kananun shekarun su, suke kaiwa samarika kansu, sannan su dake, su kuma lalata musu......"

"Thank you! Form Pastor Bature Yohana Chibok! Now Abubakar UA Moddibo! Young billionia! Ko! Toh Alhamdulillah!

Nagode da ka tunatar dani, bayana, a matsayina na tsohuwar karuwar Aahil.

Mr Arrogant! Kayi da yar halak, Insha Allah. Na gama zama da kai, ni ka gayawa Magana Sadeeq idan kaine autan maza bazan zauna da kai ba.

Insha Allah, sai kaga abinda zai hana ka barci, sai kaji kuncin da zai hanaka farin ciki, kuma ina kara tuna maka nice na kaiwa Dr Aahil kaina yayi yadda yaso dani, kuma da zan ganshi sai na kuma kwanciya dashi, sai Meye, karka manta idan ka Kuskura kazo inda muke wallahi. Zan tafi na bar da Yarka har duniya ta tashi, kuma na ciyar da ita da sana'a mafi kaskanci.!

Sadeeq yadda kasani kuka sai kayi fiye da wanda nayi, Bazan zageka ba, amma Allah yana tare da wanda aka zalunta. Nagode! B"

Daga hakan ban kuma bin takan shi ba,  na zauna nayi kuka. Tare da tir da abinda na aikata abaya, Aahil ya cuce ni, matuka.

Tun daga lokacin ban kuma jin shi ba, asalima zan jishi suna waya su Innarmu, ana kawo min wayar zan kashe baki daya.

Ban tsaya haka ba, na rufe shi a duk wata layi kanena, domin sai da na amshi wayar su nasaka shi a blacklist,  hankalina ya kwanta.

A yanzun bana jin Dr a raina, koda yake fushi nake.

--
Bayan tafiyata Zimbabwe, su Fa'iz suka gama kwanakin su, suka koma, sannan su Siyamah suma suna nan, Dadah na cin Ubansu la'ada waje.

..... Shi kuma ciwon jikin shi Allah ya taimaka ya kone, sai dai na jikin Devanah, wanda suke kara samun mafaka, tunda bata kashe na wajen, sai ya zamana cikin ya mutu amma waje

yana nan danye.

Bai sani ba, dan haka ya cigaba da dangwalar arzikinta..

Sai dai ko wata bai yi ba, ya fara fama da kaikayi me mugun Bala'i tashin hankali, wanda shi ya kuma kara mishi jin haushina, dan yana ganin kamar nice na sanya shi dawowa Devanah.

Sosai sandar girman shi, take haihuwar kuraje, ba shiri ya hada musu kaya, sai Germany!

A can kuwa sai da suka yi fada da ita, wanda yaja ya maketa, domin ranshi yakai kololowar ɓaci, ga rashin samuna, ga kuma tashin hankali Bala'in da take fama dashi. Shi yana nan ya bude baki tana kunyar kanta ashe ita nan kanta take kashewa. Bai iya hakuri ba sai da ya gaya mata magana har da gori yace.
"Wallahi da Husnah ce! Bazata tab'a cutar dani ba, Yarinyar da tasan darajar rayuwarta.

Haba gaskiya mana take tambayana, matsayinki, ashe tana gurin kar na dawo dake ki kasheta da ranta, bakar muguwa.

Wato dan baki addinin mu shine ni bari ki kashe ni, hankalinki ya kwanta, kin sanya min ciwon da ya tab'a min kwayoyin halitta na, ni da Haihuwa sai dai naga wasu nayi, Allah ya isa Devanah, kin cuce ni. Sai kinga abinda zai dame ki, Badan Allah yaga zuciyata ba, ya bamu Zar-minah da bansan ya zanyi da hakkin Husnah ba"

Haka yayi mata zagin cin mutuncin, tare da ja mata jarfa, shi damuwar shi, Haihuwar da bazai kuma ba. Gashi Allah ya daura mishi don yara kamar me. Dan ji yaƙe kamar ya saka akawo ni daga Zimbabwe. Ga mission d'inshi da ya fara, kai Devanah ta cuce shi.

Dole ya kira Ummi ya gaya mata, halin da yake ciki. Hankalinta ya tashi sosai. Dan dama tana kokarin su koma London, aikuwa tace mishi.
"Hakkin Husnah! Tun ba ayi nisa ba, toh ka sani bazan barta ta zauna da kai ba, domin da lafiyarka ka jajjibo abinda ya dame ka.

Wallahi ba dani ba, kayi ta zama da autar Mata, ita kuma Husnah sai ka sake musu yar mutane."

Inda Ummi ke shiga ba nan take fita ba, domin taji zafin abinda yayi har take cewa.
"Daga tambayar Matsayin Devanah kace tana bakin kishi da matar da basu tare, dan taga kana damuwa da ita, dan taga kana bukatar alamarinta, kasan me yasa tayi maka wannan tambayar? Gudun faruwar wannan al'amarin ne, yasa take don yiwa tufkar hancin ne!

Sadeeq kai ba yaro bane!  Talatin da wani abu kake wannan shirmen, ka bani kunya, sosai, ka bani mamaki. Ai nayi shiru ne na zuba maka ido, kasa yar mutane a gaba da damuwa,

ashe rabon ba za a nakasata bane, daga tambaya.

Idan na fahimci fadar nan take musu kai suka tare da juna, Hadiza Fatima, kuyi min Shari'a tsakanin abinda ya faru, sai dai ku sani, zanyi hukuncine da abinda kuka bani shawara akai, duk yarinyar bada zata soka, kana arnen ka, kuma ta zauna da kai har ka dawo ka musulunta, ka aureta a wacce bata damu da kazaman cigaba ba, ita burinta, taga ta sameka.

Bata da burin da ya wuce, ka zama nata ita daya ba, toh ba damuwa haka ma ya ishe ta."

Haka Dadah tayi ta gaya musu magana cikin b'acin rai amma a cikin sanyi, wanda ta dauki laifin ka kacokan ta daurawa Sadeeq da Moddibo, ni kuma ta riko hannuna tace.
"Ku rike dan ku da Jikarku ni na rike mara iyayen zan riketa,"

Inda Dadah ke shiga banan take fita ba, Dadah sai ta tayi kowa wankin.

A lokacin Ummi take tambayar ina yarinyar, sam na manta, tana dakin shi.

Koda aka je, an sameta ita daya sai dariya take, tana wasannin ta.

Devanah kuwa tunda taga bai dawo ba, tayi tafiyarta asibiti, sannan ta wuce gurin matar da take mata ke, ita kuma ta kai ta gurin wasu mutane a can wajen London.

Rike hannunta mutumin yayi, yajima yana rike da hannun ta, kafin can ya buɗe idanun shi.
Da suka yi mugun ja, yace.
"Idan kika yi asiri ko tsafi, bazai ti tasiri ba, amma idan kika tafi a yadda kike al'amarin ki, babu

wanda zai yar da da ita, akwai sauran lokacin kiyi yadda zaki juyo da hankalin shi, suna fushi da juna, kawo kunnenki."

Nan ya gaya mata abinda zata shi, sannan ya dauki wani ƙarfe na azurfa ya wurga a wuta, ya tambaye ta sunan shi da sunana, rubutawa yayi a wani karfe sannan ya dauko wannan ruwan azurfan ya zuba a karfen.

Yana gamawa ya mika mata, da zafi yace.
"Saka! Wannan zuciyarshi ce! Kuma tana zafi, da zaran kina bukatar yayi mata abu, bani kunnenki!"

Nan ya gama gaya mata yadda zatayi sannan ya cigaba da cewa.
"Tana da zafin kishi, akan shi da yarta bata da hakuri, amma kisani duk lokacin da kika bari zoben ya b'ata bazai saurareki, ba, kije yanzun ku cigaba da sanyata bakin ciki, duk da kakarsu ta shiga tsakaninsu, Auren su ba mai mutuwa bane, akwai Alamarin Allah a cikin auren, amma karki matsa sai sun rabu, domin kina haka zaki iya mutuwa. Domin akwai masu tsaya mata, matsalar da tasamu dashi yasanya sun juya mata baya, kiyi ƙoƙarin kafin su dawo, kin mamaye tunanin shi, ta yadda zaki cigaba da juya tunanin kowa, sannan yarinyar su ki fita harkokin ta, domin itace yanzun take cikin tsaron Allah da wasu abubuwan, kina cewa zaki bata madararta, zaki iya tonawa kanki asiri.

Kitafi yanzun zaki sami yadda kike bukata, kuma ki shigar da abinda na gaya miki, in ba haka ba zata iya miki illar da ke baki mata ba, mijinki yana sonta, kema kiyi amfani da sonda yake mata ki nemi abinda na gaya miki, zaki yita nasara, amma daga ranar da suka kusan fita a zanen kaddararsu toh ina gaya miki, koni bazan iya dakatar da Hukuncin Allah ba, domin Alkawarin Allah tabbatacciya ce,(Safiya Musa Hukuma nemi naku a kasuwa)"

"Amma Bana! Ya batun QAUNARMU dashi?!"

"A'a yarinyar! Ba kaunarki bace! Itace mafarkin shi, itace yake iya ambata da QAUNARMU (Mamuhgee karku bari a baku labari yana nan labari me tab'a zuciya) tun bai santa ba yake begen haduwa da Ita, lokacin da suka haɗu, zuciyoyinsu taki haɗuwa, sai da Igiyar zato ta shiga cikin lamarin su, sannan suka fahimci juna......"

---------------------------
*_Assalamun Alaikum jama'a barkanku da jimirin bin labarin! Kamar yadda nayi muku bayanai jiya, yau ma ina son na kuma muku bayani! Labarin Bahaushiyah! Labarine da yake beating ta kowani b'angare, musamman kan Tauraruwan labarin HUSNAH HABIB Manga! Da Dr Bature! Tare da DEVANAH Ezrah Chibok! A yanzun na san wasu sun fahimci me zai iya faruwa a Next Pages! Tunda nayi muku bayani 🤔😆 toh Nagode! A farko labarin 80pages ne, ina tafiya labarin na kara kusanta kanshi ya sake warware wasu abubuwan! Tabbas kishi halal ce! Sai dai kishi irin na HUSNAH ya kan zamewa mutane kamar tsohon yayi, Koni idan aka hadani da Husnah zan iya rabata da mijinta, sabida ina da mugun zolaya,  iya wannan ma zan koreta!

Wayayyarta bai kai inda zata fahimci kanta bane, idan ba ragewa Husnah kishi, games din labarin ya kare! Amma jigon labarin makasudin labarin zafin kishi! Idan na saka zafin kishi kowa yasan abinda zai faru! Idan nasaka HUSNAH a labarin kowa zai kawo rayuwarta ce! Idan na saka Dr Bature kowa zai iya cewa nayi Dr wane? Tsaf sai sunan labarin ya dace da Dabi'u kanwata da kuma sunanta a gurin Babanmu! Asalin Bahaushiyah, zuciyarta babu mugunta ko mugun nufi! Ta kan tsaya namiji yayi kome a duniya! Ta sayar da kayana d'akinta domin mijinta, shin da nasaka labarin da Sunan Yar Arewa kowa mita zai yi akan ai ba dukka matan Arewa suke da zafin kishi ba! Jama'a Kishi kawai da tugga Nana A'ishah da Hafsah suka haɗawa Manzon Allah akan Zainab bintu Jash! Ya ki shan zuma da namar karamar dabba da take girka mishi, high quality na rayuwar Manzon Allah, ya rayu ne da wadannan matan, kuma suka yi mubaya'a lokacin da aka sauko da sura sukutun da guda akan su! Misalin farko, musuluntar Bature! Bai rayu a cikin hausawa ba, balle ya fahimci irin rayuwar su, daga roma aka kawo shi, bai san zamantakewar Hausa ba, Husnah ta taso cikin kuncin rayuwa, iya iyayen su suke musu gata, bata san yadda zata sarafa abinda ya shigo hannunta ba, shi yasa take mishi riƙon da bata kaunar wani yace yana so! Devanah! Ta taso da son shi, lokacin ƙalilan ya koma musulmi, kuma yana nuna mata don Husnah, ya danne sonta, kaunar Husnah baya hadata da kome. Gashi tana zaune ana wulakanta ta, wani lokacin mune muke sayan Bala'i da hannun mu, da zasu jata a jiki, ana nuna mata addinin ya bada dama ayi da ita wallahi baza sauya, dabi'unta, amma ido da ido ake kyamar ta. Nayi Imanin idan Fa'iz ne da mata biyu, zai iya zama dasu lafiya, amma B fa, Uban rikon shi Bishop ne! Matar shi daya, kuma bai tab'a ganin tana abinda bai dace ba, akwai banbancin Muhallin a labarin, banbancin addini! Banbancin Ra'ayin! Sannan matsalar duka SON abu daya Dukkan su, babu wacce zata iya sadaukar da B sabida a zauna lafiya, da Husnah zata rage zafin kishinta, tabbas sai Devanah ta fidda nata, ga abin haushi kowa bakinta suka yi fada a cikin gidan, Lokacin da Devanah ta kirashi babu wanda ta sani! Amma ita hatta iyayenshi suna jin ta, halittar tace! Muje gaba ko zata iya ragewa dan samun mijinta, amma ana mata laifi sosai kawai abinda nake so na nuna muku, ita ake cuta amma mutane ba zasu ga hakan ba, sabida itace take nuna rashin hakurinta, da koda wasa zata dauki shawarar Mama da Ummi ta danne da an wuce gurin, amma sai take ganin ai zata iya kwatar kanta, data ga  zai  sauka, idan wata ce me wayo, ita ya dace ta amshi mgnr Devanah, ko kuma ta sanya shi yaje ita ba damuwa, ko a haka ya wadatar da ita, ku nazarci labarin don Allah kuyi hakuri! Karku damu da sab'anin fahimtar juna, dan ko me zaku yi, idan Allah ya yanko maka kazar wahalar, a figeta da jin jiki Nagode_*

***Ga masu bukatar sayan book din  nan zasu iya biyan ta wannan acc***

Acct: 0472282105
***Ramlat Abdul Rahman Manga***
***GTBNK*****.....**
200 ***ta bank***
300 ***ta katin mtn domin biyan ta tana ga wannan number zaku turawa***/.+2347035133148👈🏻
***Domin shiga VIP*** 500/ ***ta bank***/600 ***ta katin mtn***....
Yan Niger Republic...
Zaku tuntube wannan number ne +227 84 50 64 76👈🏻

***Idan zaka sayi Kuma Inuwar Gajimare ne*** 200 ***ta bank idan katin mtn*** 300.......

[7/2, 9:19 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BHSY58
Zaro idanu Dadah tayi cikin fusata tana tambayar su Abinda suka min.

Amma dake munafukai ne, sai suka b'ata rai, alamar babu abinda suka min, duk yadda naso sarrafa jikina na mike na kasa, ina kwance a gurin.

A hankali ta d'ago hannunta a babban d'an yatsana kafana, tana kallona.
"Wato dai ba zaki rage jin haushin matar mijinki ba! Ita da take da yadda zata juya mijinki, shine kike kinta, ga damar ramuwa nan.

Ba an kafa musu doka ba, kawai ki sa musu ido, kira abinda zai faru. Dukda ban so gaya miki mu suwaye, amma nasan kin fahimci mu ba mutane bane irinki.

Kakan mijinki shine yayi mana Alkhairi, bani Mantawa mun fito daga birnin Kisra! Kasancewar mahaifina shine Sarkin kisra a Narudeen bin Aslma.

Ina da yayi biyu, Yazid da Aminatu, kanwata Na'imatullah,"

Sunkuyar da kanta tayi tana share kwalla, sannan ta kalli kowa yadda suka damu na tashi, sannan tace.
"Mu zuri'anmu tafarkin Muslunci muke, bamu tab'a cutar da dan adam ba, koda kuwa ya kasance Azzalumi.

Mun tashi da gata, tarbiyya uwa uba, ilimi Addinin Musulunci, kuskuren da na aikata ba kome bane, sai bijirewa Mahaifina, Magajin garin kisra Imaran bin Faris,(🤔😒 sai kuce kun manta da Zuljah! Imran mijin Zuljah)

Imaran malamine babba a kisra kasancewar mahaifin shi malamine shima, amma Imran ya haɗa abu biyu, malanta da jarumata.

Gashi mutum ne da yake da hakuri da biyayya, dan haka Mahaifina yaga dacewar ya haɗa mu a matsayin miji da mata.

Sam ni bana son Imran, kasancewar shi bai cika sakin fuska ba, shi yasa lokacin da aka bani shi naji bana son shi kuma bazan iya auren shi ba.

Wata jumma'a mun fita kasuwa anan na haɗu da Ayatullah bin Assadullah, tunda ya ganni yake bina, ganin haka na shiga gudun kar ya ganni, karshe dai yazo har cikin gidan mu, a matsayin mai kula da wasu abubuwan, dake an sanya auren mu nan da shekara guda, dan haka na amincewa Ayatullah muna shiga soyayya har muka.

Lokacin da bikin ya karato, a nan muka ji bazamu iya hakura da juna ba, dan haka muka tattara muka gudu ana gobe daurin aurena.

Bayan mun gudu, zuwa garin su Ayatullah, ashe shima dan babban malamin ne, kuma babban gidan, Sheikh Najmuddawlah, ya amshe ni hannu bibbiyu, tare da yan uwansa Ayatullah.

Sai dai matsalar Mahaifiyarshi bata karb'e ni ba, dukda nazo da hatimin masarautar mu, amma haka Ummi Hurmat takini.

Shekarar mu talatin, a binin askandariya, na kasar Misira. Ina kusan bakin ciki.

Amma ban tab'a nuna mijina ina cikin damuwa, matsalar da aka samu, duk lokacin da na samu ciki lalacewa yake, bamu tab'a damuwan ko akwai wani matsala ba, sai lokacin da tasaka shi ya auri Fanilah.

Abubuwan babu dad'i, dan ki zan kwana na wuni bazaki ji dadin labarin ba, a hankali ya fahimci halin Mahaifiyarshi, sai ya tattara mu muka dawo yanki nan da kuka ganmu, shi ya kafa garin.

Wata rana kakan Mijinki ya fito da shanu, nan ya ganmu ni da Fanilah mun dauki Yarona mai suna Aabis, zamu niman magani dan matsalar da nake samu, idan na haifi yara sai sun data sai su fara ciwo jikin su na kore.

Anan muka hadu dashi ya kalle mu, sannan yace.
"Bayin Allah! Ku kawo yaron nan na duba shi"

Nan muka mika mishi, murmushi yayi sannan yace.
"Ai Koriya ce! Bata da wata doguwar jinyatuwa, kasancewar idan zamu nime maganinta TOH nan da wani lokaci zai warke."

Mika min yaron yayi sannan ya shiga cikin daji, yajima sosai dan har mun cire rai zai dawo kawai sai gashi da ganye aduruku. Da ganye biyinda zugun, sai hararabi da sabara.
Dan haka ya nuna min sabara da hararabi zan sha biyinda zungu da aduruku na yaro.

Munyi godiya sosai, ganin kayan zai mana yawa, shine ya dauka mana har alkaryan mu.
Tunda muka iso, Malam ya ganmu yasa almajirai suka amshi. Kayan sannan ya tsaya tare da kallon garin yace.
"Gaskiya garin nan yayi kyau, ga nima iri biyu, TOH bayin Allah na barku da Alkhairi"

Cikin sauri malam yace.
"Malam Abubakar! Ka manta dani ne!"

D'ago kanshi yayi sannan yace.
"Anyi haka, yanzun na tunaka"
Ashe sun tab'a haduwa da jimawa, lokacin da Malam ya hadu da wata iftila'in, dake yana fita da'awa, a hanyar dawowar shi wasu shaidanun aljanun suka biyo shi, zasu far mishi, shine. Kakan mijikin ya far musu, har ya ilata dayan su, TOH dake bai san cewa mu ba mutane bane, sai suka kula abota da Mijinmu.

Bayan sun gaisa ne, yake tambayan shi sha'anin rayuwa, ban san iya adadin tattaunawar ba, sai dai yayi mana sallama, inda muke tambayar shi me zamu bashi. Dariya yayi sannan yace.
"Abubuwa guda biyu, sukan dawowa me shi, Alkhairi da Sharri, idan bai fada kanka ba zai fada bayanka! Dan haka Nagode sosai"

Tun daga lokacin bamu kuma waiwayo shi, ba amma munyi alqawarin duba bayan shi, sai dai kuma aka samu akasi domin kuwa, mun koma askandariya

Bamu samu halin dawowa ba sai lokacin da akuka fito da Abubakar aka sanya muku abu a hanya, shine muka karkato da motarku zuwa alkaryan mu.

Yanzun dai zan barki domin ki kashe rigimar kakanku da mijinki, sannan zan dawo na baki labarin Yadda suka tafi dashi hannun arna.

---

Tana tafiya na bude idanuna, dai dai Dadah ta rufe B da duka, tana yi tana kuka, tana fadin.
"Dan ubaka! Gaya min me kuka mata, kai jama'a Haihuwa da makiyi ba abin ka bawa masoyi ba, wallahi sai nasaka yan sanda sun kamaka, kuma katafi da yar banzan nan bani son ganinta.

Haba Abubakar! Meye laifin Huznah, dan tana sonka. Tun kana arnen ka. Take binka me yasa bazaka gane cewa tana yin komai ne dan kai take yi shi me yasa baza ku fahimta ba, Me yasa ka aureta idan kasan cutar da ita zaka yi.

TOH wallahi zaka rabu da ita dole kasake musu yar mutane mugu Azzalumi.

Kafirci ya gauraya jinin jikinka, shine bari ka kashe mus..."

"Dadah!"
Na kira sunan ta a hankali, da sauri ta juya tana kallona, mik'ewa zanyi Devanah tayi saurin dakatar da ni ta hanyar cewa.
"Karki kuskura, ki takura min Yarona, dan haka ki kwanta. Sai a kira likitan ta duba ko ya zau..."

Dafe goshinsa yayi a tsorace, yace.
"Devah!"

Take kirjinta ya shiga bugawa, tare da tsoron abinda ta aikata, nan ta shiga muzurai.

Kafeta da Ido Ummi tayi sannan tace.
"Me kike nufi! Ciki kuma?  Taya?"

Cikin makirci tayi maza tace.
"A'ah ina nufi tayi a hankali domin faduwa tayi a ban daki, cikin ta ya bugu da abin bayan gida shine aka ce karta na motsa jikinta."

Shiru suka yi basu ce mata kome ba, suka ci-gaba da tambayana me nake so.

"Yunwa nake ji!"
Na gaya musu, a hankali.

Komawa gida yayi shi da Devanah, a hanya ya mata rashin mutunci, tare da gaya mata magana.
Wanda yasata kuka. Dan har da gori yayi mata, sannan yace mata.
"Zaki koma naija! Soon, idan zan tafi tare zamu tafi. Ki bar min mata da dangina su zauna cikin salama, ke Shaidaniya ce, babu Alkhairi a tare dake, haba wannan wacce irin masifa ce.

Wallahi idan dangina suka gane abinda kika sani na aikata, sallame ni zasu yi ke muguwa ce, kin sani ina ta ganin laifin Husnah, bayan kece da son zuciya.

Ita dan nayi farin ciki take kome, kefa dan nayi bakin ciki iyayena suji badadi kike kome, zaki koma."
Yadda yake mata, zaka sha mamaki. Da ta gaji da masifar shi ta amsa ya kuwa dalla mata mari, dama yana niman inda zai sauke haushin Dadah ya sauke akanta.

Ya mata rashin mutunci, karshe suka sauka akan hanya suka yi kaca-kaca, har tace mishi.
"Na rantse! Sai na sanya ka kuka da idon ka, sai na rabaka da ita Husnah! Ciwon sanyi da nasaka maka, wallahi ban so ya kasance sanyi bane, so nayi yafi cutar muni, wanda zaka gane kayiwa Addininmu butulci, bayan mun gama maka kome, shine bari ka koma wani addinin.

Zaka yi dana sani, zan dawo kuma zaka sha mamakina, domin dana na jikin Husnah tawa ce. Domin kai babu kwan halittarka da zai iya sarrafa d'a, shi yasa na dulmiyar da kai bayan na sanya an maka Karyan zaka iya Haihuwa bayan kuma bazaka iya ba, kaga kenan kana kishin matar ka karta bi maza, toh ai idan na gaya maka dan waye a cikin ta mutuwa zaka yi da bakin ciki, Hahhhh ka zata zan yarda na shanye bakin cikin da danginka suka min ne?!

Toh albishirinka, mahaifinka. Yanzun za a kiraka domin ya fadi!

Mahaifiyarka ce na kasa nakasata, idan kayi wani yunkuri, Next abinda zai faru. Shine

za a iya tuhumar ka da taaddanci, kakarka na kyaleta ne sabida shekarunta da kuma ita daya ce bazan iya da ita ba.

Amma Imam Moddibo aikin da aka sani akan shi ya ƙare, muje gida na dauki kayana, sauran kuma Yan kungiyar CAN zasu ji da kai.

Ina sonka amma Uncle Amos yana bukatar jin labarin mutuwar Babanka.

Shi yasa na zabi ajiye ganyen tea din da za a na dafa mishi yana sha, kullum.

Yana lalata kome"
Shafa fuskar shi tayi tana ce mishi.
"Dauki wayarka, tana kara"

Hero!
Ya fito baro baro, a sannu tayi swip din wayar cikin tashin hankali Ummi take ce mishi.
"Kayi maza kazo Abban ku ya fad'i"

Katse kiran yayi yana kallon Devanah. Murmushi tayi sannan tace.
"Kana mamaki, Cheated, naive,betrayal,hypocrisy, duk a jinin mu yake kai ne bako a cikin addinmu, shi yasa baka sani ba, mu kuma zamu iya aikata hakan.

A lokacin da kaso yaudaran kanka kace baka son Husnah, tun a lokacin na daura d'amara wargaza ka bai kai iya ba hatta kazar gidanku sai na lalata mata suna, naso na fara daga yarka.

Sai uwar Yarinyar ta shiga tsakaninmu, shi yasa na koma kan Mahaifinka, kaji yadda mahaifina yaji lokacin da kace baka sona.

Shi yaso na hakura da kai sabida yasan ko bijima ko badade zaka koma gurin danginka, amma ina baki karshe nice na zuba mishi guba, yaci ya wula, sabida kar ya min sanadin da zan rasa miji irinka.

Hhhhh! Ai nasan addininku ya hana wannan abin, amma na cusa maka tausayina da rashin son kuka na, kai kuma kayi abinda na saka, bayan kasan Husnah zata iya kin amincewa, amma sabida tana sonka ta amince, dan ta sami kusanci da kai, toh ka gaya mata na bar mata kai, dan nasan baka da amfanin da zaka yi Mata, sai na S**x shikenan, ba kai ba Haihuwa, amma dan makiyinka yana cikin ta.

Ranar da ta haifa ranar zan gabatar maka da Ubanshi, sai kasan Yaren da zaka mata bayani.

Shi yasa na hanaka........

***nan zasu iya biyan ta wannan acc***

Acct: 0472282105
***Ramlat Abdul Rahman Manga***
***GTBNK*****.....**
200 ***ta bank***
300 ***ta katin mtn domin biyan ta tana ga wannan number zaku turawa***/.+2347035133148👈🏻
***Domin shiga VIP*** 500/ ***ta bank***/600 ***ta katin mtn***....
Yan Niger Republic...
Zaku tuntube wannan number ne +227 84 50 64 76👈🏻
***Idan zaka sayi Kuma Inuwar Gajimare ne*** 200 ***ta bank idan katin mtn*** 300.......
[7/2, 9:19 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BHSY57

_Ki amince Ubangiji yana madakata! Shi kuma ki mishi uzuri kaidin mace yafi na shaidan kaifi_

Naji muryan Mama, sunkuyar dai kaina nayi jikina na rawa ji nayi kamar bana fahimtar kaina, nace.

"Na amince! But i have little requirement!"

Zama nayi a daya daga cikin kujerun falon, idanuna a rufe nace.

"Zan muku aikin kuma Insha Allah za a samu nasara ina jin haka a jikina, amma sharadin farko! Babu ruwan ku da cikin jikina! Na biyu dole ki bar min mijina, na uku dole ki biyani kudin daukar cikin, sannan babu ke babu mijina, kina bukatar haihuwa ni Bahaushiyah mara galihu zan miki ina nufin babu ruwan ki dashi, idan kina bukatar shi sai kin tuntubeni, idan yayi miki toh idan bai miki ba zan iya tafiya."

Shiru suka yi tare da kallon Juna suka yi tare nitsa tunanin su.

"Mahnoor! Ki bamu lokaci muyi nazari, kar ya wuce awa daya dan zan iya gayawa kowa yaji abinda kuke bukata dani."

Mik'ewa nayi na bar musu part din, ina shiga falon Ummi na zube a gurin, na fara wani irin Barci.

......

"Devah ki hakura da idan kin yarda, dan bana son na gaba mu sami damuwa a cikin alamarin,"

"Hmm! Nasan yau da Husnah ce ta kawo wannan shawaran hatta familyn ka zasu amince, amma dake nice na kawo shine bari ka juya min baya, karka manta kai ka min alkawarin zaka min duk abinda nace idan na dawo shine zaka juyawa min baya!"

Aikuwa ta sanya shi a gaba da kuka tare da kananun magana. Tana kuka hada kayan ta ta fara, ya riko hannunta ta kwace, ya kuma rikota tare da rungume ta, yace.

" Shi kenan! Amma kinji requirement ɗinta kin amince!"

Wani katon faint smile ta sake a fuskar ta, tare da sauke kanta a kirjin shi, tana kara jin

dole ta dawo dashi hanyar da ya sauka dole ta dawo dashi dai dai.

Daga haka suka tayar da shawarar, indai zata yi nasarar cutar dani bata da matsala.

---

Kura mata ido nayi cikin damuwa idanuna suna dab da zubda hawaye.
"Ko ya-ya a rayuwar duniya kowa dama yake jira da kai, ita tafiki sanin kan shi, dan tasha wutar wulakancin shi, kuma gashi yau tana tare dashi, kece baki san halin kishiyarki ba. Domin kuwa bata da mutunci da sanin ya kamata.

A baki na sakarya zaki ce bazaki yarda ba, matsalar mijin ki bai gama sanin ilimi Addinin Musulunci bane, su kuma iyayen shi ganin yana fama da cutar zuciya shi yasa basa iya tsawatar Mishi.

Kina da option biyu da zaki iya ramawa, na farko dole ki ajiye kishin tunda mijinki zai dawo hannunki, ko kuma ki cigaba da kishi ki rasa shi tayi ta gana miki matsalolin rayuwa."

"Mama baki ganin akwai matsala daukar cikin!"
Murmushi tayi sannan tace.
"Ta yaro kyau take bata karko, toh ya kenan ita ta iya makirci sai kece bazaki yi makirci ba, kinsan me ta gaya mishi, dan haka sharuddan da na gaya musu ta amince, sai ki taimake ni ki rage damuwar su, wannan cikin da take buƙatar ki ɗauka shine makamin ki, karki yarda ki bada wannan damar ki rike shi sosai, zan taya ki."

Buɗe baki nayi zan mata magana, naji hannun shi cikin rigana, yana wasa da abinda yafi damun shi kenan.

Make hannun shi nayi, sannan na tashi tare da tsuke fuskana, "Husnah mun amince."

"Hmm! Kace mata nice zan sanya lokacin ba kune zaku sanya min lokacin ba!"

Daga haka na wuce dakin Ammih, ban kuma jin duriyar su ba, sai da dare da yazo muje mu kwanta.
Tunda muka shiga dakin naga take taken shi, tuni nayi Fuska, tare da kwanciya a falo, yana zuwa zai dame ni na sanya shi a gaba da kuka, ina gaya mishi irin abinda yake min, tare da cutarwa da suka min. Yanzun kuma suce na haihu musu, ga wulakancin.

Duk masifa da mita da kukan da nayi bai hana shi, sai da yaci abinda ya samu kafin ya iya barci.

....

Idan zauna ina tunanin abinda suke buƙatar nayi musu, sai naga kamar mun rena Ubangiji ne, ko nuna mishi bai iya ba.

Sam bana son Abin dan ina shirin musu, bayani bazan yi ba, Mama ta bani addu'o'in na istahara, nayi tare da azumi.
Ni Ko alamar wani abu banji ba, kawai dai nasan zamu je gurin.

Ummi tayi tayi ta san meke damuna naki gaya mata, har ranar da aka shirya mana tafiyan bayan sun roke ni.

Tunda muka isa Asibitin, aka fita aka barni da likitan, dan mace ce.

Yan tambayoyin tayi min, na bata amsa, tare da dogon hira, har muka shiga wani daki anan na kwanta.
Tayi min alluran, da zai sani barci daga nan kuma ban kuma farkawa ba, sai bayan awa guda.

Cikin damuwa ta kalle ni, sannan tace.
"Bamu karasa aikin ba, aka sami matsala, Wata sati ku dawo."

Haka na fito jikina a sanyayye, inda ta musu bayanin da tayi min. Muka dawo gidan.

Sharadina bai fara aiki ba, dan haka yau na sake mata mijinta na cigaba da zama a cikin dakin Ummi.

*
Yau ake bikin bude kamfanin kayan sawa na Zar-minah kids Fashion.
Tun daga gown din da nasaka, zuwa sarka da yan kunne, da warwaron da nasaka Ummi ce ta saya min

Sai Zar-minah, da aka mata wasu irin kwalliya me shegen kyau, tare da wani gown me matuƙar kyau.

Lokacin da muka je, aka fara bikin, Devanah da ta ganmu sai da ranta ya b'aci, domin Ni nasaka gown din amma na rufe jikina sosai, bata ga yan kunne da sarkan wuyana ba, awarwaron hannuna ta gani.

Tana zaune ta dauki hoton kayan jikina da abin hannun ta shiga niman prize din kayan, haka ta cigaba da nima, dakyar ta samu. Kamfanin da Ummi ta saya min kayan dan daga U.S ne, shiru tayi, tana jin daci a ranta.

Amma da ta tuna abinda zata min bayan na haifa mata cikin sai ta sake dariya.

Haka suka yita daukar hoto da Zar-minah, wacce bakinta babu kome sai wawulo, idan tayi

dariya sai kace tsohuwa.

Anyi taron buɗewa lafiya, domin kuwa lokacin da Devanah taga sunan Zar-minah, bakin ciki ya sata tayi ta shan ruwa, har aka tashi itama tana hango itama ta kusan samun yaron ta, dan ta ruwa likitan da zata yi abin ta tabbatar mata da namijine, zata biyata.

Abin bai kuma damunta ba, sai da aka ce an baiwa yarinyar kudi na hauka nan ne. Hankalin ta ya kuma tashi tana mamakin wani irin arziki Ummi take dashi ne haka, kafin mu bar gurin sai da tasha kwalba uku ta wine.

Ina halkance da ita a raina nace.
*Zaki mutu da bakin ciki na kuwa muna nan dake mu zuba.*

Har aka tashi taron bamu sami kan mu ba sai da Bakin Ummi suka tafi.

---

Bayan kwana bakwai muka koma, nan matar ta kuma shiga dani dakin da aka kwantar dani, ta min Allura, sannan ta kama aikinta. Tana gamawa, aka fito dani. Ina barci toh ban san inda kaina yake ba.

Tun sha biyu ya dace na farka har dare wajen karfe biyu, tsoro ne ya kama su, dukda asibitin babba ne, kuma sananne.

Sai aka shiga damuwa, har Yakira Ummi ya gaya mata bani da lafiya ne tun safe, toh gamu a asibiti, an kwantar dani.

Hankalin ta yayi mugun tashi, tunda tazo take musu kallon tuhuma, amma basu nuna alamar rashin gaskiya ba, har aka gari ya waye.

Ban farka ba sai da na cika lokacin da aka min Allura, ina farkawa na zuba musu ido. Ina kallon kowa, kafin na mike Devanah ta kai hannu zata tab'a ni na buge hannunta, dan wannan bugewar sai da zoben hannunta ya cire tare da faduwa, da sauri tabi zoben ta dauka tana sauke wani B'oyayyen ajiyar zuciya.

Shigowa Abbansu yayi ya mikawa B hannu suka yi modification, sannan suka shiga tattaunawa akan abinda ya dame ni...

Lokacin da Dadah tazo ritsashi tayi, tana tare gida, kamar zata rufe shi da duka, dole ya sunkuyar da kanshi.
"Wannan kafiran tasanya ka a gaba dole mu tayata da addu'a, dan ta gama sid'e maka zuciyarka, baka iya fahimtar kowa sai ita nakira me kama da fadar kirimesi, wannan munafuka banda farin fatar ta ba da baka aka yota, tabbas da sai bala'in ta yafi haka, toh annami tsutsar shadda, zaku gaya min me kuka yiwa yar mutane ko sai na hadaku maci banten iyayenku.......

***nan zasu iya biyan ta wannan acc***

Acct: 0472282105
***Ramlat Abdul Rahman Manga***
***GTBNK*****.....**
200 ***ta bank***
300 ***ta katin mtn domin biyan ta tana ga wannan number zaku turawa***/.+2347035133148👈🏻
***Domin shiga VIP*** 500/ ***ta bank***/600 ***ta katin mtn***....
Yan Niger Republic...
Zaku tuntube wannan number ne +227 84 50 64 76👈🏻
***Idan zaka sayi Kuma Inuwar Gajimare ne*** 200 ***ta bank idan katin mtn*** 300.......
[7/2, 9:19 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BHSY59

"Shi yasa na habaka kusantar Inuwar Husnah, kasan dan me. Dan na b'atar da kai, shi yasa naki barin Husnah ta rab'eka jin ka zan so kane domin Allah, ko ɗaya burina na Kenan na tarwatsa duk wanda zai juyawa Addininmu baya, iya haka ma kawai ya isheka, domin nasan zaka rasa yadda zaka yi dani.

Kuma dama babu yadda zaka yi dani, haka akewa mutanen da basu godewa Allah ba, a yanzun kaga dalilin da yasa Husnah ta tsane ni.

Yarinyar tana da kaifin basira, sai dai tana da zafin kishi. Idan nace zamu yi da ita ne, har abada nice da nasara, amma idan na cigaba da tunzurata tabbas, zata iya kunco min kura.

Zaka iya yadda mota, Mr Arrogant!"

Kamar wanda aka zarewa laka, haka ya cigaba da tafiya, har gida.

Tana sauka ya juya, zai tafi kamar zai tsaya ya sake ta, sai ya fasa ya juya da mugun gudu, cikin ikon Allah ya isa asibitin.

Koda ya isa basu tare dani sai Dadah, wacce take kuka ina tayata, jingina yayi da kofar.

Yana min kallon taya haka ta faru. Saukowa nayi naje inda yake na kwantar da kaina a kafad'arshi.

"Ka dauki hakan a matsayin kaddarar ka! Babu wanda ya isa kauce mata, Allah yana tare da musu hakuri" janyo ni yayi gabanshi ya rungume ni, yana sauke ajiyer zuciya. Yayinda karfe kirjin shi take wani irin bugawa.

"Me yasa? Me nayi Mata? Me na tsare mata da zata min haka, son shin me yasa mutane

suke son ganin na kasa?"

Sanya hannuna nayi na kara rungume shi, ina ce mishi.
"Kayi hakuri! Kayi hakuri! Kayi hakuri"

Janye jikina nayi na riko hannun shi, kamar zan yi magana sai na fasa haka naja shi har inda Su Ummi suke, tana ganin shi. Jikinta yayi sanyi,

Zuciyarta tayi rauni, kauda kanta tayi, tana kallon ICU.

"Meye likitocin Suka ce?!" Ya tambaye ta, muryan shi a sanyayye.
Kafin yayi magana Dadah ta amshi maganar,
"Meye kuwa zasu ce! Bayan guba aka bashi yayi taci, ta lalata mishi kayan cikin shi. Komawa gida zamu yi, domin kuwa babu amfanin b'adda kudi domin bazai tashi ba."

"Dadah!"
Ammih ta kira sunanta, daga mata hannu tayi, tana murmushi. Sannan tace musu da gaske mutuwa zai yi, dan babu wasa batuna. Kin tab'a ganin wanda yayi aman hantar shi ya tashi."

Da sauri ya shige dakin, duk da ana rike shi, haka ya shige ciki yana kallon yadda suketa fama dashi, sai yau ya lura da yadda Abban nashi yayi wani fari, kamar babu jini a jikinshi.

Fitar dashi aka yi, jingina jikin shi yayi da bango yana lissafin goma da ishirin, danna wayarshi tayi,
"Ok! Thanks"
D'aga haka bai kuma cewa kome ba.

---
Tun daga ranar bamu kuma gane kan Sadeeq ba, bai da lokacin kowa sai na Abba, sosai yake gayyato manyan likitoci daga duk wata shahararrun Asibitin yazo yaga Abba sakon daya ce Ayi hakuri,

Hankalin shi yayi mugun tashi, baya ko ina rintsa idanun shi, kullum yana hanyar niman masalaha.

Satin mu biyu aka sallame Abba zuwa gida, kai tsaye ya tattaro mu dukkan mu zuwa kasar nigeria.

A garin Lagos muka sauka, a lekki, anan gidan shi yake, wanda babu wanda yasan da gidan sai Daniel.

Tunda muka iso gidan ya shiga damu, wani part. Su Ummi ya bar musu main house din, Wanda yake zaman gidan sama da wasu dakunan.

Tunda muka shiga gurin mu, naga ya b'ata rai sosai sai na fita sha'anin shi, naki zama inda yake.

Sosai yake jin haushi na, da naga haka sai na tattare kome na, na koma gurin su Dadah. Dan ya shiga wanka ne.

Yana fitowa yaga bani nan shine ya shirya cikin kananun kaya, ya tawo. Tun a kofar Dadah yake harara na.

"Zoki wuce!"
Ba musu na wuce, muna shiga ya fincikoni. Idanun shi jajjir yana huci,
"Wallahi ki nimawa cikin ki, Uban shi dan ba kwayoyi halitta na bane."

Kura mishi ido nayi cikin tsoro da farga ba,

Cire hannun shi nayi daga rike ni da yayi.
" Bazan nima mishi uba ba, sabida bai da uban da yafika, dama wacce tasaka ba kana ganin kaunarka take ba. Toh ni bazan zubda cikin ba, kuma ina haifa sununka zan saka, tunda baka da tsoron Allah, kai abinda ranka yake so shi kake aikatawa.

Ko tausayi na baka ji, abinda yazo maka shine me kyau wanda bai zo ba, ko oho.

Kun mai da Bahaushen mutum mara kima, da sanin ya kamata, ku babban damuwarku shine ku ci gajiyar shi, sannan ku yarda shi sabida bai da amfani,, Sadeeq kana moruwa dani, amma kana iya cutar dani ta kowani fuska, kai baka damu yadda nake ji ba, kai idan buƙatar ka zata biya, shikenan!

Sadeeq baka da tausayi, kana da mugun nufi sosai, sannan bana raba daya biyu kaine kake son kashe mahaifin....."

Tasss ya kifa min mari, rike gurin nayi. Tare da kafe shi da ido, sannan na cigaba da cewa.

"Eh mana, kai nake zargin za ka kashe mahaifinka, kuma wallahi ciki ko kana so ko baka so sai na haife shi.

Kuma ya kiraka da Uban shi, mara alkibla kawai. Allah zai bi min hakkina, Insha Allah."

Tun daga ranar, na fara ganin wulakanci mara iyaka, wanda ta kai baya iya b'oyewa a gaban kowa, zai min sabida rashin adalci.

Mahaifin shi da yake cikin wani yanayi kullum sai ya kirani, ya ce.

"Asma'uh! Kiyi hakuri, kiyi hakuri da Sadeeq, kowani mutum da kika gani yana tare da jarabtar shi. Ke taki jarabtar sai ya zamo a cikin ahalina ne, gashi shigowar ki abubuwa da yawa sun fito fili. Don Allah kiyi hakuri da mutumin da kike tare dashi, wallahi zai sauya"

Wannan shine kullum abinda Abba yake ce min, haka ma ummi da Dadah.

Har zuwa yanzu jikin Abba sai godiyar Ubangiji, amma babu wani canji.

Haka kullum suna hanyar asibiti, abinda ake gaya musu kullum suyi hakuri.

.....

Watan mu biyu da dawowa, Sadeeq yayi wata tafiya, wanda sai da ya shafe kwanaki goma sha biyar, ya dawo. Sannan ya kuma sake tattarawa ya dauki Abba da sauran mutane ya tafi dasu India, ku kuma ya turani gurin Iyayena, sabida yace na zubda cikin da yanzun tabbata, wahalar da nayi a cikin Zar-minah ashe wasa ne, domin wannan sai da akaita sanin ruwa, tare da karin jini.

Bana cikakken sati Daya zan kwanta a asibitin.

Tsabar wahala har ta kai na fara tunanin nima na zubda cikin tunda bai so.

......

Wato tun ranar da yazo Asibitin, na bashi hakuri, shine kawai idan ya zauna sai yaji ranshi ya b'aci, sabida cikin jikina.

Da zaran ya tuna cikin bana shi bane, sai yaji kamar ya saka hannu ya fincike cikin, tsabar kishin da yake damun shi.

Lokaci guda ya daina jin ko sha'awan kallonta, damuwa ta yawaita mishi, ya shiga tashin hankali.

Dan lokacin da yace mu koma zimbabwe, Ummi sai da ta d'ago mishi abinda Devanah ta fada. Nan ya fara kame kame.

Karshe dai sai da ta bugi cikin shi taji gaskiya ko nace Allah ya matsi bakin shi, ya fadi abinda suka min.

Bata iya cewa kome ba, ta kirani tayi ta faɗa, sannan tace min.
"Insha Allah! Idan muka gama abinda muke zamu dawo."

---

Har ila yau, Su Hindu basu fadi kome ba, asalima sunce basu san kome ba akan b'atar shi da yayi dan basu da masaniyar haka.

Dan haka yan sanda suka tura su kotu, inda aka ka kuma gabatar da abubuwan da suka aikata, har da yunkurin kisan kai.

Da haka Alkalin ya dakatar da yanke musu hukunci har zuwa lokacin da Abubakar zai zo.

---

Cape town...
Na kasar Afirka ta Kudu...

A hankali take jan motar ta, har zuwa Nelson Mandella stree, cikin kwarewa tayi parking a kofar gidan, tare da zama cikin motar ta, kafin ta fito.

Tana waya cikin murya me matuƙar kasala, tace.
"Na gama maka aikinka! Saura mu ruguza duk wani aikin da yayi, kaima kana yunkurin cin amanata zan yi wasan mage da b'era da kai."

Katse kiran Devanah tayi tare da murmushi, sannan ta shiga cikin gidan.

Da Joel suka fara karo, rungume ta yayi sannan yace.
"Good Girl! Kin gama aikin ki, saura Sakamakon ki, me kyau!"

Kafin tayi wani yunkuri, Joel ya burma mata, wuka sai da ya fito ta bayanta, murmushi yayi sannan yace.
"Dama na gaya miki! Idan kika zab'i Sadeeq zan kashe ki! Kin dauka wasa ne! Sannan kika yaudari mutumin da ya yarda dake sama dani."

Hawaye ne ya zuba, sannan tace.
" Bani bace Devanah Ezra Chibok ba."
Ta faɗa dakyar, tare da cire mask din fuskar ta, tare da.

Saketa yayi cikin tsoro, kafin yayi wani yunkuri yan sanda sun shigo gidan, tare da Devanah.

Tana murmushi, ta kalli yarinyar da har ta shuri bokiti, tace.
"I pity for you Ada, ka zata zanzo maka ne kai tsaye, ga yan sanda nan zasu maka jagora har gidan yari nan hukuncin su na irinta naija bace. Sauka lafiya."

Tayi ficewarta, bayan ta gama da Joel, dan.

---

Tashi nayi na zauna, tare da matse cinyoyina, sabida cikin ya sani mugun buƙatar mijina, haka zan zauna nayita kuka.

Gashi ko fahimtar watanni cikin ban sani ba, haka.

Ban daki na shiga na sakewa kaina na ruwa, ina jin shi har cikin zuciyata saboda bakin ciki abinda Sadeeq yayi min.

Ina gamawa na fito, na saka kayana, na kwanta ina nazari.

Hamma na fara yi daga nan kuma ban zance ga lokacin da tashigo ba.

"Surikinki! Gubar da yasha bata da makari, sai dai kuyi hakuri su dawo dashi gida, dan itace wasu bishiyoyi ne, tare da saiwowin su, itacen da bishiyoyi asalin su guba ce bata cika fitowa a ko ina ba, sai a can kudancin CHINA, Al'amarin Ubangiji sai kiga ya sami lafiya.

Batun cikin ki kuwa, kiyi hakuri. Shima mijinki kishi ke damun shi Insha Allah zai dawo gareki.

Bana son kina yawaita tunani akan cikin ki, dan baki san me Allah ya baki ba, sannan haka kawai bazan ce ki amshi tayin su ba.

Zaki samu farin ciki amma sai kinyi gwagwarmayyan, domin wasu dalilai, kafin kuci moriyata Soyayyarku.

Karki bari Iyayen ki su fahimci matsalar ki, domin zasu iya rike mijinki har abada, amma idan kika shanye sai ma ki Basu labarin daga baya, yanzun babu wata damuwa sai ta ciwon Uban mijinki.

Daga nan zaki iya fahimtar irin tasirin hakurin da nace kiyi, da kin Kuskura kince bazaki amshi cikin ba, da kece zata yiwa mugun kulli, Dan tayiwa Dan uwansa ma, balle ke.

Zan tafi amma koda yazo karki nuna mishi kina jin ciwon abinda yayi miki, cikine dai dai kin haifa koda kuwa ana mutuwa a dawo sai kinyi shi, Idan yazo nima zan zo Insha Allah, dan na fahimci sai mun fada da shi kafin ......

🤔☹️
B! Toh kayi a hankali dan akwai masu shigarwa Husnah rigima, gaskiya bana son kalen dangi 😒😏☹️🤔 Mama Aljana mun yafe 😏
***nan zasu iya biyan ta wannan acc***

Acct: 0472282105
***Ramlat Abdul Rahman Manga***
***GTBNK*****.....**
200 ***ta bank***
300 ***ta katin mtn domin biyan ta tana ga wannan number zaku turawa***/.+2347035133148👈🏻
***Domin shiga VIP*** 500/ ***ta bank***/600 ***ta katin mtn***....

Yan Niger Republic...
Zaku tuntube wannan number ne +227 84 50 64 76👈🏻
***Idan zaka sayi Kuma Inuwar Gajimare ne*** 200 ***ta bank idan katin mtn*** 300.......
[7/2, 9:19 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BHSY60

_Wooow nice har Page na 60 ni da iyakata 😆🤣🙄 59 Nayi breaking record dina_

"Ba zan kuma barin shi ya cutar dake, dan muma da sauran danginki muna matuƙar kaunar ki.

Zaki sha mamakin yadda Allah zai baki nasara, akan duk wanda ya tunkareki da wata matsala. Allah zai baki nasara.

Amma sai kinyi hakuri fa."

Ta jima sosai a gurina, sannan ta bani shawara tunda ba cin abinci nake ba, na fara azumi kawai shima zai taimaka min.

Bayan tafiyarta ne na ji jikina na ciwo.
Abubuwan da suke wakana ban sani ba.

---

Abba ya kare sosai, domin ciwon ya ci jikin shi ainun, dan haka suka sallame su, kawai dan babu amfanin zama a can, dole tasanya su dawowa har da su Muhammad da Fa'iz.

Suka sauka a Yola, washi gari suka tafi kotu, abin tausayi.

Hajiya Hindu ta fita hayacinta, kana ganinta kaga wahala, kuka suke sosai.

Lokacin da Alkalin ya fara yanke hukunci.
Hindu ta fashe da kuka tace.
"Alkali! Kayi mana, afuwa. Nice na kai Sadeeq gidan Amos! Sabida ya biyani kudi, domin daukar fansan abinda Moddibo yayi mishi."

Bayan dawowar Moddibo daga Saudiya ne, ya fara aiki a jami'ar Yola, wanda aka dauke shi tare dasu Amos tare da Alhaji Aliyu Maitama, duk lokaci guda aka dauke su.

Ta gefe guda kuwa yana aiki da ma'aikata noma, ga kasuwanci, da yake yi ba kama hannun yaro.

Lokacin ƙalilan Allah ya albarkaci rayuwarshi tare da arzikin ban mamaki duk da sun san yana ƙoƙarin Niman na kanshi sai suke tambayar shi ko yana da wata B'oyayyen sana'a ce.

Yace a'a bai dashi kawai dai yana rike da dukiyar matashin ce, amma bayan nan wallahi baya wani abu.

Basu yarda ba, sai suka shiga zagin shi tare da, yayyatawa a makarantar wai yana cikin kungiyar Asiri, haka yaja mishi damuwa sosai, wanda Allah ne kaɗai ya fidda shi, daga baya aka fahimci sharrin Amos da Aliyu Maitama ne.

Sai aka dakatar dasu, wanna dakatarwan itace ta kuma haihuwar sabon gaba, me cike da bakin ciki da hassada, Aliyu ya ajiye aikin shi Bayan an dawo dashi, sabida lokacin an nime shi a kasar waje aiki.

Sai ya rage Amos, wanda yake kallon Moddibo a matsayin wanda ya hana shi cigaba, domin kuwa kullum arzikin Moddibo kara yawaita yake, amma Amos baya tunanin cewa Allah ne ya sanya Albarka a cikin dukiyar.

Bayan wani lokaci, Amos ya shiga harkan cin hanci a makarantar, duk abinda za'a yi sai yayi ha'incin, amma babu wanda ya fahimci haka Sai Moddibo, yayi mishi magana yace ai shima abinda yake kenan ya tara dukiyar shi.

Dan haka ya zuba mishi ido, kwatsam aka turo jami'a, daga can Abuja, suna zuwa kuwa suka yi gaba da Amos.

A can yaje yayi ta karya da Karerayi.

Karshe dai da aka fahimci babu gaskiya a maganarshi, aka kore shi, tun daga lokacin ya fara fadi tashin sai ya ruguza Moddibo, ana cikin haka ya hadu da Mohmood wanda shima kuma yana da bakin cikin. Na rabu dashi na auri Moddibo.

Haka ya kuma karawa musu tsanar Moddibo, bayan wani lokaci ne, kuma suka hade kai har da Mahaifina, tare da wani na kusada Moddibo, suka shiga da fita hanyar da zasu kuntatta Moddibo.

Shine tunanin su ya fada kan Yaron shi Sadeeq, inda Ni na taimaka musu yaron ya isa hannun su.

Da farko sun so kashe shi, amma suka kasa, sabida bokan su ya gaya Musu, ba zasu yi nasara akan yaron ba, kai tsaye ko a yanzun fi. Shi sabida Allah baya kare shi, kuma bazasu iya nasara akan kowa a gidan ba, matuƙar yaron yana gidan.

Sai dai su mai dashi Kirista, ta yadda bazai ji tausayin iyayen ba, a duk lokacin da aka ce ya tozarta su zai aikata, amma sai me lokacin da muka dauki shi sai ya zamana yaron yayi kuka, har yayi zuciya, ki magana wanda Ni nasan yana magana.

Wannan rashin maganar da bai yi ba, shi ya hana k'iyayyar da zamu cusa mishi na iyayen shi, kuma dama bokan ya faɗa.

Dan haka yana gani na zai tab'a guri can, daga gidan shine Amos ya wuce da shi Chibok, daga nan kuma ban kuma sanin abinda ya faru ba, dan bana da lokacin bibiyar al'amarin yaron sai wani lokaci da naje biki garin naje har gidan Amos na nime ganin Yaron anan yako ya mutu.

Ai kuwa ina zuwa gidan ya tarbe ni, dan nayi sa'a matarshi bata nan.

Nan muka sheke ayar mu, sannan na tambaye shi, amsar bakin shi ce ta bani tsoro wai yaron ya mutu saboda ciwon zuciya naji tsoron kar bincike ya sanya so kamo Ni...

Tun daga ranar ban kuma tambayar shi ba, sabida nasan ya mutu, kwatsam wata rana naje italy kawai naga yaron, dan yafi kama da Moddibo, kasancewar nice na fita dashi daga gida, sai nayita bibiyar alamarin shi har nasan inda suke suna rome

Naso na kuma tunkarar Amos sai naga babu ruwa.

..... Nice na shigo da Namiji dakin Zuhrah dan su rabu da Moddibo, sai naga ashe koda nai haka bai san Yasu rabuwa ba, sai ma makale mishi da Zuhrah tayi.

Haka na bani haushi, sosai.

Kuma karku manta nice nake sanya shi yayi wani abu, sabida tsanar Zuhrah.

Koda nake da miji bai hanani bawai Alhaji Muhmood kaina ba, inda muke masha'ar mu, Sadeeq ne kawai dan shi, amma Siyamah da Sughra, da Rafi'q yaran Alhaji Muhmood ne, na gaya muku ne, dan ku kama dangin ku.

Ya mai Shari'a ayin min Afuwa, da abinda na aikta, Amma nasan hakkin Moddibo na bina.

A sanina bokan yace babu abinda zai tab'a dawo da Sadeeq gida, sai gashi daga Shigowar ta gari ta fara rufe mana aikin mu, dan haka ranar da aka tare Fa'iz, a daren da Sadeeq a gurin har kashe me Napep din da Sadeeq, sabida shine mutum na farko da ya bada shaida akan mu,

Husnah itace ta lalata min shirin mu, domin itace takawa yaron da muke da yakinin ya mutim.

Lokacin da ta kawo shine, na sami Amos da maganar nan ya gaya min, zamu iya kashe shi sabida akwai karfen. Da aka saka mishi a kirjin shi, lokacin da yayi ciwon zuciya.

Ranar nayi farin ciki, domin nasan bayan mun gama dashi, zamu kashe kowa mu mallaki kome nashi. Domin duk sun tattara kome sun zubawa yaron suna."

Haka tayi ta bada labarin abinda suka aikata,har da mahaifinta, Sadeeq kuka yake sosai sabida tausayin iyayen shi, dan bai tab'a kawowa sun wahala garin niman shi, sai yau.

Da yaji fitar dashi aka yi bashi ya fita da kanshi ba, ko sakacin Mahaifiyarshi.

Bayan alkali ya gama jin kome, ya gama rubuce-rubuce, kafin ya d'ago kanshi, yace.
"A yau sha uku ga watan Mayu na dubu biyu da sha bakwai, kotu tana son a nimo mata, inda Dangin Bishop Yohana Chibok, tare Amos, a gurfanar dasu a wannan kotun ranar sha biyar ga watan Yuli, dubu biyu da goma sha bakwai, tare da Aliyu Maitama ana bukatar ganin su, sannan kotu zata bukaci Imam Moddibo a wannan kotun domin jin.yadda zata kasance. A cigaba da tsare masu laifi, har zuwa sabon zaman da za a kuma yi.

Kotu ta sallama kowa..."
Nan ya buga gundumar nan, sannan kowa ya mike tare da cewa kooooootuh.

Jikin Sadeeq a mace ya fito daga kotun yana sanya abu yana boye fuskar shi dan har yan jarida sun mishi caaaaaa.

Dakyar aka matsa musu suka shiga motarsu,

Kwantar da kujeran yayi baya hawaye na zuba mishi.

Yana mamakin yadda mutane suka kware da cin amanar juna, haka kawai an dauke shi an kai shi wata duniya na daban sabida rashin adalci da imani, abin mamaki har da Mahaifin Aahil, ashe yasan shi, shi yasa da zaran ya ganshi da Aahil yake daure fuskar shi, ko kuma yayi rawa Aahil fada, shi ya zata dan yana Kirista ne, ashe sabida yasan ko shi waye!

***nan zasu iya biyan ta wannan acc***

Acct: 0472282105
***Ramlat Abdul Rahman Manga***
***GTBNK***.....
200 ***ta bank***
300 ***ta katin mtn domin biyan ta tana ga wannan number zaku turawa***/.+2347035133148👈🏻
***Domin shiga VIP*** 500/ ***ta bank***/600 ***ta katin mtn***....
Yan Niger Republic...
Zaku tuntube wannan number ne +227 84 50 64 76👈🏻
***Idan zaka sayi Kuma Inuwar Gajimare ne*** 200 ***ta bank idan katin mtn*** 300.......[7/2, 9:19 PM] BAHAUSHIYAH🥰: BHSY61

Koda suka isa gida jiki. Kowa yayi sanyi musamman yadda su Siyamah suka takurawa kansu zaman wani gefe, tausayi suka bashi yana shiga gidan ya mika musu hannu da gudu

suka rufa mishi suna wani irin kuka.

"Kuyi shiru Ni One above mistake!"

"A'ah Yaya is not mistake son zuciya ne, ashe shi yasa muke abinda babu kyau sabida mu din
illegitimacy ne, Nenneh ta cuce mu, Allah kayi mana sakayya!"

Wani irin tausayin yaran yaji ya sake kama shi tare da tsoron Allah.

"Dan Uban ku! Alqur'an fita zaku mana a gidan, kuke can ku cigaba da zama da shaidanun iyayenku, haba ashe shi yasa baku gajiya da bin maza,.kamar bunsuraye, ashe barbaran gado ce, maza ku b'ace min a gidan mu."

Cikin damuwa Fa'iz yace mata.
"Tunda bai san da yaran ba, kuma cikin su ya kai tsawon wata shida. Aure ya bashi babu yadda zayi dasu. Suma zasu zauna damu tunda kanen mune"

"TOH basu zauna ba, dan banza mara kishin iyayen shi, baka ji abinda ta aikata ba?

Ko tsabar son kai da kalan dangi zaka, shishigi fitar takaba da molo, Toh tafiya gurin dangin Ubansu zasu yi."

Muhawaran su yaki karewa tasa B barin gurin su, ya nufi shashin Abba.

Anan ya zauna, yana kallon yadda Ummi taci kuka har ta godewa Allah.

Daura kanshi nayi akan cinyarta, yana sauke wasu irin kwalla. Amadadin farin ciki, sai gashi sun buge da kuka.

"Ka tashi kaje ka dawo da Husnah!"
"Ummi! Cik....."

"Bana son Musu! Babu yadda za ayi Husnah ta cire yarinyar wata tara to ten a nono, babu reasons, kaje ka dawo da ita, idan ta haihu sai mu duba muga dan waye!"

Mik'ewa yayi cikin damuwa, dan wallahi baza a haifa mishi shegen ba, haka kawai. Kuma yasan halin Devanah ntunda ta fadi haka babu karya tasan kome akan babyn cikin Husnah.

Kawai Ummi tana nuna mishi bangaren ci ne zan bai da Wadatacce ilimin addini.

Shafa kan shi yayi, tare da barin gurin su, zuwa can inda ya zauna.

Dukda irin kewarta da take addabar ruhin shi, amma ya gwammace ya zauna babu ita, da ya ganta da cikin wani, a jikinta kai Devanah ta cuce shi.

Tunda yake bai tab'a jin tsanar wani a duniya sama da Devanah ba, haka ya shiga had'a kayan shi.
A ranshi yana alkawarin sai ya zubda cikin kota halin k'ak'a ne.

Kwana uku yayi a Yola sannan yayi musu sallama, sai Zimbabwe.
---
Ban san watannin cikin ba, ni burina kawai na samu maganin da zai b'arar min da cikin.

Dan haka bayan na samu Innarmu tayi barcin rana, Dama ba kowa a gidan sun tafi makarantar, daga ni sai Innarmu Babanmu ya tafi kasuwa.

Ban dauki Zar-minah ba, na lallaba a hankali har nafita dan bani da karfi ko kadan. A hankali nake tafiya.

"Lallai baki da hankali! Cikin zaki je a zubda shi! Husnah zaki biyewa zuciyarki da ta mijinki! Wallahi kin bani mamaki, maza juya ki koma gida dan ba magani ba ko asibitin zaki dura a cikin ki bazai fita ba, ke ko jini bazaki gani ba. Duk wanda ya matsa cikin ya fita, Allah sai na shafe mishi kafaffunshi da ganin shi, sai an haifi abin cikin zai budewa ganin shi ba shi daya ba, hatta ke.

Da kike uwar cikin bazan kyaleki, ba dan wallahi sai na nadeki guri guda har sai kin kusan haihuwa zan warware ki, fita. Maza ki koma dan mijinki ya kusan isowa. Kuma zaki sha mamaki dan wallahi sai kin nime ni da kanki"

Daga haka tayi b'acewarta cike da damuwa na juyo gida, ina shiga ko minti sha biyar ban yi ba, sai gashi ya iso.

Dole nice nayi ta hidima dashi kafin Ummi ta tashi.

Kallon yadda na rame, sosai sai cikin da ya danno. Rintsa idanun shi yayi, bakin ciki yana kara samun matsuguni a ranshi.

"Me yasa baki fidda wannan kadararren cikin ba?!"

Juyawa nayi na sake mishi murmushi, sannan nace.
"Ba zan iya ba!"
Daga haka na juya zan fita ya taso ya tsaya a bayana yace..
"Ki zubda cikin! Ko muje mu zubda"
Juyawa nayi tare da dafe cikin nace.
"Ina son cikina! Kuma ko me zaka yi bazan fidda shi ba, zaka iya sani nayi maka abu kuma yi

sabida biyayya, amma akan cikin jikina!

Gwara ka sake ni, sakin ma ba daya ba, ba biyu ba, kuma ba uku ba.
Zan dauka a matsayin line of my destiny."

Daga haka na ficce a dakin, ran shi kuwa kamar tayi bindiga.

Dole ya sab'awa Husnah, ta cika taurin kai, dole ya hukunta ta, ayi mace bata jin maganar ka.

Shi yasa yake jin tsanar cikin, dole ma a barar da cikin.
Zama yayi bakin kishi na turmushe shi, a gurin.

Barci ne me mugun dadi, ya kwashe shi a gurin.

Cincirindon mutane ya gani a kofar dakin Innar Husnah, ka wasu na kuka. Wasu na alhini.

Zar-minah kuwa ihu take tsallawa, cikin sassarfa ya isa bakin kofar Innar Husnah, yana d'aga labule yaga mutum cikin farin kaya a kwance, ga jini na malala.
A dimauce ya isa kan gawar ya shiga buɗe suturar da aka mata, yana jin wata na cewa.
"Wannan shine sakamakon zubda cikin da kuke buƙatar yi.

Matuƙar kuka nace zaku zubda cikin haka zai koma muku, wannan baka ga kome ba."

Buɗe gasar yayi yaga fuskana, da sauri ya rufe tare da. Kwala min kira.
"HUSNAH!!!"

Da karfi hakan ya farka dashi daga barcin da yake.

Shigowa nayi da sauri har muna buge juna.
"Baki mutu ba! Sannu babu abinda ya same ki, muje asibiti.

Muje su duba min ke, babu abinda zai faru, bazan kuma cewa a zubda cikin ba, ina sonki fiye da cikin."

Ga baki daya ya rude, ga tsoron Allah da nagani a idanun shi, haka na saka abaya muka tafi wani asibitin a cikin garin.

A cikin gwaje-gwajen da suka min, aka gano cikin kamar biyu ne, watanni cikin biyar.

Shiru nayi ina nazarin fuskar shi.
Sai naga bai damu ba, sai ma damuwar shi lafiyata.
Magani suka rubuta min dan har yanzun bana iya cin abinci.

Muna dawowa, Muka samu Innarmu ta tashi, gaisawa suka yi. Sannan ya gaya mata jibi zamu koma, amma akwai abinda zai yi a garin nan kafin ranar kuma yana son ya tafi dani.

Bata ce kome ba sai fatan a dawo lafiya.

